UMMI JB:
♡SIRRIN ƊAUKAKA...

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION..📚📚*

_♡F.J.W.A

'"Wa sallallahu ala Akaramil Mursalina Aj'main Muhammadin wa'ala alihi wa Sahabihi wa,sallam"'

PAGE ONE..

"Baba burina kasha kafini bukata dan Allah." kawar da kanshi ya yi gefe duk da jikinshi baya motsi sakamakon ciwon dake tattare da shi bakin shi ma a karkace yake ƙwalla ne ya gangaro masa da sauri ta ajiye kofin tana share mishi hawaye "Baba na ɓata maka rai ko? Toh kayi hakuri In Sha Allahu bazan ƙara ba." A hankali ya soma magana "Jiddah ni baki min komai ba, hasalima bana buƙatar komai ya shiga bakina.. da sauri ta dakatar dashi "kar kace haka Baba in baka shaba maganin fa? nafi son lafiyanka fiye da komai domin kai da mama kaɗai kuka ragemin kune gata na! kunne bangon da in na jingina ajikinku nake jin daɗi ku kaɗai ne farin cikina kayi hakuri kasha kaga jiya bakaci komai ba."

"Jiddah ina ganin gazawata! ni ya dace in fita in nimo muku abinci ni yadace na muku komai keda mahaifiyarki Amma dubi halin da nake ciki kalla fa? jiddah na gaza muku wannan abubuwan gashi dangina wanda ya kamata su tsaya su temakeni duk sun gujeni kowa guduna yake sabida banida kuɗi ni talaka ne!.." kukane ya kwace mishi Mama da fitowarta kenan daga banɗaki ta karaso tare da durkuwa a hankali ta ajiye butan hannunta dakyar ta miƙe sakamakon cikin jikinta dayafara tsufa "Kayi hakuri Allah yana sane damu kuma wannan jarrabawace bawai don baya sonmu bane a'a ya yi haƙan ne don ya gwada imaninmu kuma a kullin muna gode masa Allah ya ubangiji Allah kai kayi Adamu kayi hawa'u Allah bamu da kowa bayan kai Ubangiji ka sassauta mana Allah ka kawo mana agaji Alfarman wannan rana ta juma'a kabawa Mijina Usama lafiya" jiddah dake jikin mahaifinta ta amsa da "Ameen mamana. "
Dafa cikinta tayi tare da girgiza kai rabonta da abinci tun jiya shima kanzone wanda jiddah taje makota tayi wanke wanke ta samo musu Allah kenan! me yanda yaso da bawanshi "Asama'u ɗauki kokon nan ki sha." mama tace. "a ah Usama kai yafi dacewa daka sha domin kasha magani." Usama yace "Asma'u bana son jayayya kin fini bukata bani da burin da yawuce ganin farin cikin iyalina daga shi se bashin Mu'azzan dake kaina inna roƙon ka Allah ka billomin da hanyar da zan cika wannan burin nawa kafin mutuwata.. "kabarmu dawa usama?. "Akwai Allah.."
Juyo da kanshi yayi ga Jiddah "ɗauki ki baiwa mahaifiyar ki Allah ya miki Albarka ubangiji ya

tsaremin ke da mutuncinki Allah ya rabaki da sharrin samarin zamani!." ɗaukan kunnun tayi ta nufo mahaifiyarta dashi "buɗe bakinki nabaki mamana." ba musu ta buɗe bakinta domi Ɗan cikinta harya fara motsi tsaban yunwan dake cinta cokali kurɓa uku taman kokon ya kare cire kofin jiddah tayi a bakinta Ahankali Asma'u ta lumshe idonta hawaye na gangaro mata wani irin yunwane ya taso mata.

Wurgar da kofin Jiddah tayi tana kiran sunanta "Mama mamana meya sameki?." cizewa tayi tare da faɗin "bakomai Jiddah..."

Shuru suka zauna chan Jidda ta miƙe butan da mahaifiyarta ,ta ajiye ta ɗauka roban fentin da take zuba ruwa ta nufa shuru tayi sakamakon ganin bokitin ba ruwa "Sauran ruwan na zaga dashi." cewan Mama bokitin ta ɗauka "bari inje in samo ruwan" fatan Alkhairi suka mata bayan ta fita Asma'u ta matso jikin mijinta kwantar da kanta tayi a jikin taburman  da yake kwance "Ina son shafa fisƙanki babu halin haka ko zaki temaka ki ɗauki hannuna zuwa ƙan fusƙan taki?" wani irin marayan kuka tasa a hankali sautin kuƙan nata yake fita hannunshi ta kama takai saman fisƙanta amma Ina ko motsi bayayi dalilin haka yasa ta kara sautin kuƙan nata "meyasa haka! meyasa wasu mutanen basa duba gobensu! meyasa wasu mutanen suke manta alkhairi ? yanzun sakamakon temakon kenan? usama duk kai kajawo mana wannan masifar meyasa ka Auro mana masifa jubeni da yarintata na koma tsohuwa kalleni... kalli cikina wai yau mune abinda zamuci yake gagarar mu? me muka mata?, takwashe komai Allah kana gani ƴata ba makaranta ko ɗaya Ƴar da zamu ciyar amma i'ta take fita tasmo mana abinda zamuci Yarinyar da bata huci wanka ba amma wai yau i'ta ke ɗawainiya damu Allah ka kawo mana agaji.. "Asma'u kiyi hakuri tausayinta naji gani nayi kowa ya gujeta gani nayi ta fara fusƙantar tsana da tsangwaman mutane kowa ya gujeta bansan haka ze kasance ba na nufeta da Alkhairi amma ta saka min da sharri ta rabani da Ɗana ta ruguzamin komai nawa kalli yanda ta mayar dani, *LAIFINA NE"* (Shima sabon buk ɗina ne yana nan tafe da yardan Allah),

"Asma'u." ɗagowa tayi taga shima yana hawaye share mishi tayi sannan i'tama ta share na fisƙanta "Jin yanayin da ka kira sunana kaɗai ya shedamun magana kakeso kayi dani me muhimmanci koma menene in na Addu'ar Allah yasa kunnuwana suji Alkhairi.." "Tabbas maganace zamuyi wanda nake so kiyi mata kyakkyawan fahimta ki hangi nesa karki juyawa akalan maganata zuwa baya , ina nufin karki tuna baya domin inhar kikayi haka sheɗan ne ze rinjayeki ki bijiremin wanda inhar haƙan ta kasance bazanci daɗi ba nayi iya tunani da hange hange Asma'u bani da hanyar da zan biya Mu'azzan dubu talatin dalilin haka na yanke shawarar.. "shuru yayi yana nazarin yanayin da zata ɗauki maganan bezata ba, yaji tana faɗin "Ka yanke shawarar bashi Auren Hauwa'u koba abinda kakeson cewa ba kenan kayi shuru kanajin tsoron faɗa domin bazan amince bako? shifa mutumin nan baka sanshi ba, babu abinda kuka haɗa matarsa uku kasuwancine ya haɗaku gani nake kuma be damu da kuɗinsa ba domin yanada wanda sukaci uban dubu talatin Hauwa bazata iya ratsa mata uku ta zauna ba wallahi na tabbata zata ci baƙar wahala yarinyar da bata san menene rayuwa ba watan gobe fa Hauwa zata shiga sha-huɗu.." katseta yayi "wake sama da wani cikin neda ke?." sunkuyar da ƙanta tayi kasa "wakeda ikon zab'arwa Jiddah mijin Aure? cikin nida ke wake da iko da Me-Jiddah? akwai wani bayan ni akwai abinda uba shine adon ƴar sa, mutumcin ƴa mace Gidan mijinta.."

......."Tabbas Da Uba ake Ado, amma ka gane man, Hauwa bazata iya ɗauƙan nauyin da kake shirin ɗaura mata ba, kayi hakuri mijina bawai inna jayayya dakai bane a'ah halin da zata tsinci kanta nake tunani Ya zanyi? Na amince..." bata rufe bakinta ba taga mutane suna shigowa "Lafiya? ya zaku shigo mana har ɗaki ba niman izini?.." maƙalewa sauran maganan yai sakamakon ganin Maigidan dasuke zaune a ciki hannu ya miko mata cikin rawan murya tace "Kayi hakuri Ado.. "Ke Dakata bashi ya kawoni ba kud'i zaku bani banja da tsayi ba, shekara ta zagayo kunce na muku uziri nabarku kun sake wata biyar Kai! Gaskiya ina bukatar kud'i ko abarmin Gidana, domin zan zuba sabbi 'Yan haya"

"Ado kasake Kara Mana lokaci wallahi a halin yanzun ko ficika bazaka samu ba abincin da zamuci ma ya gagaremu.." Ado yace abincin da zakaci ma ya gagareka bare dubu takwas ku kwashe komatsansu ku watsar su fita min daga Gida wannan ai zance banzane! 'yan kayayyakinsu suka shiga kwashewa suna watsar dasu a kofan Gida "Dan Allah kiyi hakuri karku tozartamu ka dubi Allah ka dubi Halin rashin lafiyan da Mijina yake ciki... "Ku jasu ku fitar mun dasu daga Gida bana son Kara ganinsu Kona sak'an d'ayane" (Nayi Alkawari insha Allahu babu turanci a littafina sede in ya zama dole ne, dolenma me  k'arfi).

Tafiya take riƙe da bokiti Gurin d'iban ruwansu na tuka tuka, ta nufa nan ta tarar da Gurin cike da mutane Fam shuru ta tsaya tana tunanin yanda zata tsaya har layi yazo k'anta ga Halin da iyayenta suke ciki matsowa tayi Kusa da Yarinyar da layi yazo k'anta "Ayya 'yar uwa dan Allah ki temaka ki zuba min nabar Gida IYAYENA duka babu me gamsheshshen lafiyan jiki." Cikin tausayawa Yarinyar ta karb'i bakitinta ta Tara mata cik'e da murna Jiddah ta Mata godiya sannan ta shiga kok'arin d'agawa har ta d'aura a k'anta "Chabd'i jan ai wallahi Baki isa ba Taya zakiso a Bayan mu sannan kije kid'iba ruwa ai wallahi kinyi kad'an.." yarinyar data zubawa Jiddah ruwa tace "haba Baraka ki dubi Halin da take ciki dan Allah ki rage niman fitina Hauwace fa wanda Da, muke makarantar Allo tare kafin daga baya Allah ya jarrabe mahaifinta da rashi karatunta ya tsaya a halin yanzun ma Yana kwance baya motsi ai ko don Haka kya barta taje Gida." tsalle baraka tayi "Ke Zubaida ban tambayeki ba, surutu chaaa kaman wani kanari Ina ruwana da jarabta waya jawomusu ba ubanta ba ruwan Nan Kuma wallahi bazaki tafi dashi ba." Ture bokitin K'an Jiddah tayi take ya fashe ruwan ya zube a kasa Durkusawa Jiddah tayi tare da fashewa da wani i'rin marayan kuka taga samu taga rashi, wannan tozarcin dame yayi Kama? D'agowa tayi ta kalli Baraka ga mutanen gurin Kowa na tur DA abinda tayiwa Jiddah "Ku barta daman haka rayuwa take wannan d'inma yana dagacikin jarrabawan DA Allah ya rubuto mana kije bazan ce Miki komai ba Allahn dayayimu shi kad'ai yasan huk'uncin daze miki ni ban i'sa namiki Abinda Allah be miki ba." Tana kuka ta karasa maganan tattara bokitin tayi tasoma tafiya Zubaida tace "Hauwa kiyi hakuri dan Allah ga ruwana ki d'auki D'aya." Carab Baraka tace "Wallahi bazata d'auka ba aje a Haka gayyar tsiya Wanda talauci ya Kare musu..." Juyowa Jiddah tayi tare da fad'in "Me kud'i da talaka duk Allah ne yayisu! Kuma babu Wanda yafi wani a Gurin Ubangiji Bayan Wanda yafi jin tsoronsa da kiyaye dokokinsa Alhamdulillah mu talakawane Kuma bamu dogara da kowa ba se Allahn dayayimu bawai bayason mu bane yayimu a talakawa sedon ya gwada yanda karfin imaninmu yake kefa? Uban naki karkashin mace yake mijin tace! Se abinda uwarki take so yake Mata jikinsa na b'ari ban fad'i hak'an dan ranki ya b'aci ba, in kinji zafin maganata kiyi hakuri Zubaida nagode sosai da tausayawanki gareni." Tafiyarta tayi Baraka ta kudunduma wata uwar ashar Wanda ni Aysha bazaku jishi

abakina ba, domin yafi k'arfi na.
"Meye abin damuwa da zagi data Miki ,Bayan ke Kika fara? Ai wallahi Nan gaba duka zakisha Allah ya temakeki Hauwa yarinyace me hakuri wallahi na tabbata da watace Sekin kwashi kashinki a hannu kai Ina amfanin fitina?." Jiddah tana tafiya rumgume da fasassun bikitinta, tana kuka a Haka har ta karaso anguwarsu tun daga nesa ta fara ganin mutane a kofar gidan da sauri ta karaso Mama ta gani Kusa da Mahaifinta tana kuka Bata San lokacin da tayi watsi da bokitin ta karaso gurinsu ba "Baba Mama lafiya meya samu samu baba naganshi a kasa ya kuka fito waje.." kafin mamarta tayi magana Ado yace "Nina sa aka watsar min dasu a waje domin na gaji da ganinku cikin Gidana Dan Haka wallahi ku tattara ku barmin kofar gida Kona Kira muku jami'an tsaro" Wani i'rin kuka Jiddah tasa "Dan girman Allah Baba Ado kayi hakuri wallahi bamuda Gurin Zuwa kan dubi Halin DA muke ciki ka barmu mu zauna Wallahi nayi Alkawari zan biyaka kud'inka." Tsaf yake kallonta tare da shafa Tunbinsa "I'dan zaki ringa Zuwa D'akina muna kwana tare Har Gidan zan bar muku." Sunkuyar da kai Jiddah tayi kasa Asma'u tace "Wa'iyazu billahi 'yar tawa kakeson lalatawa Insha Allahu Allah baze ta'ba baka nasara ba D'an i'ska la'ananne..." Haureta yayi da kafarsa take ta kifu da cikin jikin wani i'rin kara tasa tare da Kiran sunan mijinTa "USAMA.. wayyo cikina mutuwa zanyi" daga Haka Bata karacewa komai ba Da sauri Jiddah ta matso gurinta d'agota tayi tare da d'orata jikinta Kumatunta ta shiga tabawa "Mamana dan Allah ki tashi mama karki tafi ki barmu a wannan duniyan da take cik'e da azzalumai mama Kinga babana banida wasu Bayan ku ki tashi mama karki min haka... "JIDDAH." DA k'arfi ya Kira sunanta kallon mamarta tayi tare da kallon mahaifinta Ajiye mahaifiyarta tayi tare da rarrafawa gurinshi "Baba kana ganin Abinda sukayiwa mama baba baka iya d'aukan mataki ba? Matarkace fa Wanda nauyinta yake rataye a wiyanka Baba kana kallo sunci mutumcinta sun tafi..."Jiddah Jiddah Jiddah ki kula da k'anki ki tsare mutumcinki duk runtsi karki d'auki d'abi'ar bezo cikin addini ba karkiyi abinda Al'uman musulmi zasuyi tur dake daga karshe Jiddah nayi biyan bashi dake , ki bishi duk inda ya Sanya kafafunsa.." Wani i'rin kunfane ke bin bakinsa Amma duk da Haka be Dena k'okarin mata magana ba, "Allah ya Miki Albarka Allah ya tsare ki.." Baba me kake cewa haka Ya mahaifina! Ka tashi ka motsa gab'ob'inka Muje mu kwaci hakkin mu... A hankali ya sauk'e wani i'rin ajiyan zuciya...

Maman Faruq
12/26/23, 8:58 AM - UMMI JB: ♡SIRRIN ƊAUKAKA..!♡

_Wattpad@ayshajb_

®🌁

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION..📚📚*
[Kungiya Domin wayar da kan mata, Farin jini writer's domin ci gaban Mata.]

_♡F.J.W.A♡_

Page2 .

Tab'ashi take tana kiran Sunanshi Amma shuru baya motsi kwantar da Kanta tayi a jikinshi tana kuka "Yanzun Baba kaima i'rin barcin mama kayi yanzun saura ni d'aya , ku tashi mana kun barni ni kad'ai , nifa bana jin wannan barcin" Limamin anguwarsu ne yazo gurin sakamakon ganin mutane da yayi sun kewayesu "a a lafiya naga kun taru anan meke faruwa?" Ganin Hauwa kwance jikin mahaifinta yasashi faɗin "Hauwa ya kuke zaune a waje?" ɗagowa tayi da sauri tana kuka ta fara labarta mishi abinda yafaru. durkusawa yayi tare da faɗin "Hasbunallahu wani'imal wakeel khai khai! wannan zaluncin har i'na yanzun duk acikin ku babu wanda ze temaka musu kun tsaya ne kawai kuna kallonsu haba! wannan wacce i'rin rayuwace Sekace ba musulmai ba, nasan da 'Yan uwanku ne Dole nasan se inda karfin ku yakare amma duba Usama ne da matarsa mutum me kirki dason jama'a mutumin da babu ruwanshi da kowa meye amfanin tsayuwarku , Dan Allah ku watse anan!".
d'aya bayan d'aya suka shiga tafiya ya saura mutum uku d'ago Usama yayi yanayinsa kaɗai ya sheda masa rai yayi halinsa Rai bakon DUNIYA girgiza kai yayi yana tunanin rayuwarsu na baya lokacin yana cikin wadata kafin zuwan  wannan bak'ar Kaddaran kai wasu mutanen basuyi ba , rufe mishi idanuwa yayi tare da fad'in "Allah yaji k'anka Usama ubangiji yasa halayyarka nagari subika Allah seya saka muku ka mutu da baƙincikin Ado kuma insha Allahu seyaga karshen sa" Da sauri na ɗago duk da kasancewata yarinya amma ai nasan kalman mutuwa kallon liman nayi ina zare mishi ido "Baban nawa ne ya mutu! Mahifina me sona Babana me K'aunata Babana meson Farin cikina Babana meson ganin dariyata ka duba liman da kyau mahaifina yana raye taya ma ze mutu ya barni ? kullun Babana seyace min Jiddah Allah ya miki Albarka Allah yakare min ke daga sharrin duniya da abinda ke cikinta kullun seya shafa kaina yana faɗin Jiddah burina ki samu ilimi burina kiyi karatun Addini Jidda Ki kasance 'Ya me biyaya gana sama dake Allah ya bani lafiya nabiya bashin mu'azzan Baralabe anya kuwa babana ze mutu dan Allah liman ka duba wallahi yana barci ne mama kinaji. ki tashi dan Allah baba katashi..!" wani i'rin kuka mecin rai take tana juya kai seda liman ya zubda kwalla tsaban tausayinta da yamamaye zuciyarsa "Kiyi hakuri Hauwa usama k'an ya rigamu gidan Gaskiya" Kan mahaifiyata na ɗago ina kuka duk na haɗa majina da hawaye na ɗaurata asaman cinyata, hannunta na kama ina matsewa "Shi kenan Liman Babana yace indena Jayayya da nagaba dani, Allah yaji ƙanshi Allah ya kafarta mishi mama ki tashi dan Allah kema karki mutu ki dubeni nayi k'ank'anta da zaman maraici"

Da temakon sauran mutanen dake gurin Liman suka D'auki gawan mahaifina bayan an mishi wanka an suturtashi suka mishi sallah lokacin muna ɗakin matar liman Mama har yanzun bata farka ba sun dubata wai dogon suma tayi har zuwa lokacin da liman yazo yace inje inma mahaifina bankwana amma nadena kuka inhar inna son mahaifina sede na kasa domin ina tuno halin da zamu shiga nan gaba nida mamana haka na daure na mayar da sautin kukan sede hawaye yaki barin fiskata hannu nasa a zanin da aka rufeshi hawaye masu zafine sukaci gaba da biyo k'uncina dakayar na i'ya masa addu'a shima cikin zuciyata domin muddin nace zan fito dashi fili ba shakka kuka zanyi haka innaji inna gani aka ɗauki mahaifina Babana me sona da son farin cikina aka tafi dashi gidanshi na gaskiya shi kenan babu shi an rufe babinsa ya tafi ya barmu bazan sake ganinshi ba ya zanyi da raina ranan haka na wuni kuka sallah ma yinsa kawai nakeyi abinda ya kara ɗagamin hankali har yamma mama bata farka ba, ga zuciyarta na bugawa fisƙanta yayi fayau, gashi mu ba wanda yazo daga dangin mahaifina duk da anje an

faɗamusu amma sunki zuwa kirin kirin suka ware mahaifina sabida shi mahaifina shi ɗaya mahaifiyarshi ta haifa ko gurinsu naje se su ringa kyarata basa so na raɓu da ƴaƴansu dalilin haka nadena zuwa suna sane da halin rashi da muke ciki amma cikinsu babu me temakon mu.. mahaifiyata kuma marainiyace matar liman ta kawo min abinci amma na kasaci domin nariga na saba da zaman yunwa a halin da nake ciki ma wallahi ko nace zanci bazan iya ba,

Seda mama tayi kwana biyu kafin Allah ya farkar da i'ta lokacin ina saman sallaya ina sallan la'asar juyawan da zanyi naga tana motsi kafin nace wani abu ta rigani magana abinda ya fito bakinta shine "USAMA cikina ciwo yake min" mezanyi in banda kuka Domin akwai so kauna da Fahimtar juna a tsakaninsu gurinta nazo "Mama kin tashi?" kallona tayi tare da faɗin "Hauwa i'nane nan ina Usama?" kafin na mata bayani matar liman ta shigo "Masha Allah sannu Asma'u kin farka?" kallonta mama tayi kafin tace "Larai.. Ke Hauwa magana nake dake kina min kuka ina usama yake!" Wani i'rin kuka nasake fashewa dashi duk na kasa mata bayani muryanta ne ya fara rawa alaman i'tama kuƙan take son yi Larai ne ta shiga mana nasiha kafin tace "Asma'u sede kiyi hakuri Usama ya rigamu gidan gaskiya" tun lokacin da Larai ke magana mama tayi shuru tana kallonta cak kuƙanta ya ɗauke wani i'rin abune ya tokare mata makoshi da kyar ta i'ya faɗin "Allahu akbar.. Allah kaji ƙan usama. mijina me kaunata! mijina meson dariya da farin cikina.
"Allah ka saukarwa Ado masifa da bala'in dayafi karfinsa Allah ka haɗashi da ajalinsa kaman yadda ya zamo ajalin mijina Allah ka tozartashi kaman yadda ya tozartamu Ya Allah na roƙeka kabani hakuri da jurinyan rashin mijina uban 'Ya'yana Allah kakai haske da rahama kabarin Usama Allah..." kasa, karasa maganan tayi sakamakon kuka da yakwace mata wanda bata san da zuwansa ba. tana kuka nima inna kuka Larai nata bamu hakuri dakyar na tsayar da nawa kuƙan na kara matsawa jikinta na ɗaura kaina a cinyarta fuskana na kallon nata hawayen idanunta na ɗiga a fiskana.
Hannu nakai fuskanta tare da share mata hawayenta "Ya zamuyi da Ƙaddararmu Haka Allah ya tsara mana Hakuri shine kalman da kullun Baba yake faɗa komai ya fito bakinsa seya haɗa da hakuri se yace muyi hakuri watarana zamuga riban haƙan, sannan duk wanda ya nufemu da sharri mu, mubisa da alkhairi, Mama kiyi hakuri kidena kuka bana son ganin zuban hawayenki hankalina tashi yake.." shuru Asma'u tayi "shi kenan Jiddan Baba nayi shuru Allah ya kara mana juriya da, dangana"
"Ameen mamana"
Kallon larai Asma'u tayi kafin tace "Dan Allah kimin magana da liman" miƙewa Larai tayi kafin tace "Toh" ciƙe da tausayawa Abinci larai ta aiko musu dashi Kallon mama nayi tare da buɗe kwanon samiran tuwon masarane da miyan kuka "Mama kici abinci" girgiza mata kai tayi " a a Hauwa bana bukatar abinci a yanzun... "Dan Allah mama karkice haka yaushe rabonki da abinci ai ko dan ƙani ko ƙanwata ya kamata kici" lumshe ido mama tayi "Bazaki gane ba, Hauwa ki bar maganan abincin nan kawai.." kuka nasa mata da sauri tace "Ya isa haka zanci" ɗan murmushi nayi kafin nace "yauwa mamana buɗe baki na baki" buɗe bakinta tayi nan na shiga bata tana haɗiya kawai take tana kallona hawaye nabin fisƙanta loma biyar na bata ana shiga ta dakatar dani.
"Ya isa haka kema kici" Girgiza mata kai nayi "Base naci ba burina na cigaba da baki har ki koshi.."a a Hauwa kici abinci" rufewa nayi kafin nace "Anjima zanci" Liman da larai suna tsaye suna kallonsu abin sha'awa ya basu ganin yanda yarinya karama take nunawa mahaifiyarta

kulawa abinda ya kara birgesu yanda Jiddah ki magana cikin kwantar da murya tare da rarrashi yarinyar da i'ta ya kamata abaiwa wannan kulawar kai! gaskiya Rayuwa ba abakin komai take ba, ta ko'ina Allah yaga dama seya jarrabi bawansa kuma baka isa ka tsallakewa wannan kaddarar ba, Bar ganin Kanada dukiya ka samu duniya kana cinsa yanda kake so kaci me kyau kasha me kyau, ka sanya me kyau kana tafiya cikin isa da izza masu baka kariya nabiye dakai a baya in mota zaka shiga za'a buɗe maka kana zama za'a rufe maka matuƙinka na gefenka duk inda kake so nan za'a kaika mutane na bauta maka sabida dukiya kai kuma a lokacin jin kanƙa kake kafi kowa babu wanda ya kaika zaka taka kowa son ranka! Sufa wanda kake nuna musu isa da izza kake takasu yanda kaso ba finsu kayi ba! domin suma Bani Adam ne kaman yanda kake banbanci shine kai Kanada dukiya, suma in Allah yaso lokaci ɗaya seya kwace naka ya basu nikin ba ninkin naka, Allah yasa mudace Allah ya rabamu da kwaɗayi da ruɗin DUNIYA sallama Liman yayi a hankali Asma'u ta amsa mishi miƙewa nayi naje na kwanko hannuna na dawo "Hauwa in sauran kayan mu na kusa ki duba zaki sami takarda ki ɗauko" hakan kuwa tayi karɓan takardan Mama tayi sannan ta miƙawa malam "Wannan takardan yana ɗauke da sunan Mu'azzan da numbobin wayarsa da adireshinsa mu'azzan nabin usama dubu talatin shekara guda ke nan da watanni babushi babu labarin sa ganin halin matsin da muke cikine yasa usama yanke huƙuncin biyan bashi da Hauwa kafin ya rasu sede ya faɗamin kuma jadda damin nan ta kwashe komai ta faɗa musu sunkuyar dakai kawai nayi inna hawaye "Dan Allah liman ka dubi halin da muke ciki da wanda muke shirin shiga ka samo mutumin nan Hauwa ke kuma kiyi hakuri bamu da yanda zamuyi bamuda shi bamu bawa wani ajiyan sa ba dolence tasa mahaifinki yanke huƙuncin haka" liman yace "insha Allahu zanyi i'ya kokari na gurin ganin na samoshi Allah yaji ƙan usama" da dare ina zaune saman sallaya mama na kwance saman katifan larai duk munyi shuru ga abincin da larai ta kawo mana na dare miƙewa nayi na ninke sallayan tare da cire himar ɗin dana saka "mama abinci" Buɗe idonta da sukayi ja tayi "kici Hauwa inna sane ɗazun bakici ba.. "a a mama ki faraci kafin naci" miƙewa tayi "To shi ƙenan" yanzun ma kaman ɗazun a baki na bata shinkafa da mai da yaji bataci sosai ba ta juyar da kai ruwa na bata ina shirin rufe kwanon ta buɗe nan ta shiga bani dolece tasa nakeci haka ta bani seda ta turamin abincin sosai kafin ta barni. ruwa nasha nazo na kwanta kusa da i'ta Larai na ɗakin liman a haka har barci ya ɗauki mama niƙan idona biyu domin tunda Baba ya rasu na kasa barci tunanin halin da zamu shiga nan gaba nida mahaifiyata da abinde ke cikinta nakeyi domin nasan zaman mu a gidan liman bame ɗorewa bane tun ina kuƙan zuci har ya fito fili ban saniba Hannun mama kawai naji tana share min hawaye na "Ki dena kuka Jiddan baba, Allah yana sane damu be manta damu ba , Hakuri kawai zamuyi mu rumgumi kaddararmu" a daren nan mama tamin nasiha sosai kuka nake wiwi na kasa tsayar da hawayena ashe na bankwana takemin ashe i'tama tafiya zatayi ta barni ta samin albarka tamin addu'a sosai tana shafa kaina tana magana har barci ya ɗaukeni ban sani ba kallona kawai take i'tama barci ya ɗauketa da sanyin asuba ne ya farkar dani har yanzun hannun mama na ɗaure a kaina juyowa nayi na kalli fiskanta tayi fayau se wani haske da tayi zare hannunta nayi nafita naje nayi ɗahara kafin nayi alwala na dawo ɗakin ana kiran sallan asuba naje inna tashin ta "mama lokacin Sallah yayi" a hankali nake magana amma shuru bata amsa min ba ganin haka yasa na taɓata "mama ki tashi haka lokacin sallah yayi" shima shuru kafin na sake magana sega larai "Har kun tashi" a hankali nace "na tashi mama ne take barci ina tashinta taki tashi ma" hannunta larai ta kama nan taji ya sake da sauri ta ɗaura kanta a setin zuciyarta amma ina rai ya riga da yayi halinsa domin kominta baya motsi "innalillahi wainna ilaihi rajiun Allah ya miki rahama Asma'u" bansan lokacin

da nayi zaman ƴan bori a kasa ba ɗif nadena jin komai....

Maman Faruq
12/26/23, 8:58 AM - UMMI JB: *SIRRIN ƊAUKAKA..*

_Wattpad@ayshajb_

Free Book

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION*

Page3 .
..........Salati kawai Larai takeyi kafin tayi kaina "Hauwa! Hauwa!!" Amma shuru da sauri tayi waje Liman da shigowarsa Kenan ya dawo daga masallaci yace "Lafiya naganki haka?" Larai tace "malam Ina fa Lafiya! Asma'u ta rasu.... " Be gama jin maganarta ba ya nufi d'akin Nan ya tadda Jiddah kwance Larai na shigowa yace ta kawo masa ruwa da sauri ta d'ibo ruwan ta kawo masa shafamin yayi a fiska ajiyan zuciya na sauke ban bud'e idanuwa ba , kuka na fashe dashi shi Kenan banida uwa bani da Uba , babu dangi Na rage ni kad'ai dagani se Allah se Kuma halina wayyo haka tawa K'addarar take yanzun babu Wanda zan kalla inji Dad'i ..

"Kiyi Hakuri Hauwa.." Da sauri na katse shi "To ya zanyi inba hakurin ba! Banida kowa fa! Babu ! ni ce fa ni D'aya! Kai!!." Wani irin kuka na sake fashewa dashi Bani da Gata fa yanzun , Larai da wasu mata makotanta ne sukayiwa Mama wanka malam yaje ya siyo likkafani ina kwance inna kuka har aka gama had'a mama Akayi mata sallah koda akace inje in mata addu'a kasawa nayi rik'e mankaran nayi inna kuka harda majina na kasa furta komai ganin na jima ne yasa Larai zuwa inda nake wai zata d'agani Amma tayi tayi naki tashi karshe de maza ne suka d'agani a gaban mankaran inna ihu da shurewa haka suka d'agani fad'i kawai nake "ku barmin mamana ku wasu i'rin azzalumai ne me yasa bazaku tausayamin ba , mamanace fa zaku tafi min da i'ta so kuke rayuwata ta tagayyara? banida uwa bani da uba ya zanyi kuji tausayi na mana haba! Bayin Allah..Wayyo Allah jama'a kuna gani zasu tafi min da UWA" mutanen dake gurin seda suka kokamin na zama wata iri bani da aiki se kuka abinci bana ci magana ma banayi Sallah kad'ai shike d'agani satin mama D'aya Liman ya shiga niman mu'azzan Balarabe Numbobin wayarsa baya shiga kullun aka Kira a kashe zuwa lokaci na fara saka juriya wa zuciyata sabida kullun Liman da matarsa hard'a 'ya'yansa haka zasu tasani gaba suna tausar zuciyata da kalamai masu kwantar da hankali hakade nake daurewa ina cin abinci badon inna jin dad'insa ba, bana son gwalesu ne kawai suna kokari dani banida abinda zance musu sede Allah ya saka musu da alkhairi Wata D'aya da kwana biyar aka samu wayar Balarabe bansan abinda Liman suka tattaunaba nede yace min sunyi waya da mu'azzan hakan ya faru da kwana biyar se gashi sunzo su biyu .

Dangin mahaifina babu Wanda yazo Kuma an aika musu haka lokacin da Liman ya aika a kirasu ko da Wanda ze wakilci auren Amma babu Wanda yazo karshe shiya tsayamin wanda

sukazo da mu'azzan ya zama waliyinsa A masallaci bayan sallan azahar aka d'auramin Aure da mutumin da bansan waye shi ba.
Kai! ranan nayi kuk'an da yafi na ko yaushe Larai tasani a gaba nayi wanka i'ta ta bani sabon kayan yarinyarta D'aya na saka Wai Ashe a ranan zamu tafi ban sani ba se da Akayi la'asar tace in had'a abinda ya dace na d'auka "Inna nifa ban gane in had'a abinda ya dace ba" Larai tace "Hauwa tafiya zakuyi.." da sauri na Mike har inna dafe Qirji "Ni dawa zamu tafi Kuma inna ne?" Murmushi Larai tayi kafin tace "Keda mijinki Kinga shi ba d'an garin nan bane..."

"Nashiga uku da Allah kimin rai mutumin da bansan wanene shiba zan bishi wayyo Allah kumin rai" kamoni tayi tare da zaunar dani "Hakuri zakiyi Aure babu inda baya Kai mutum.." nasiha ta shiga min Liman ma ya shigo ya d'ora da nashi nasihar Inna kuka suka karkatoni gurin jibgegiyar motarsa Mu'azzan dake zaune a mota shida abokinsa suna Hira cikin hiran abokinsa yace "Kai kaga yarinyar Kuwa Arab daga ganinta akwai nutsuwa kalli yanda take zuwa k'anta a kasa" mu'azzan yace "Wallahi inna tausaya mata yanda Zata shiga cikin iyayenta" Dariya Abokinsa yayi sannan yace "Gidanka Gobara ne zasu iya sata zuba mata fetur su k'yatta mata ashana" runtsa ido yayi yana tuna Gobaran dake gidanshi.

"Dan Allah kalleta fa , karaman yarinya 'yar sha uku" fitowa sukayi Abokinsa ne ya karb'i bakon kayana yasa a bayan motar Baya ya bud'e Inna kuka na shiga k'ankame jikina nayi tare da cusa kaina a gwiwa na kuka nake wiwi haka naji tashin motar Kara sautin kuka na nayi suna tafiya ba Wanda yace min ci k'anki tafiya yayi nisa min munfita Obudu har mukazo Gboko har muka bar jihar benue inna kuka daga Nan muka d'auki hanyar abuja barci barawo ne ya d'aukeni Inna sauke a jiyan zuciya Jin shuru na Dena kuka ne ya sashi lik'awa Nan yaga wiyanta ya karkace "Adam tsayar da motar na gyara yarinyar Nan" ba musu ya tsayar fita yayi tare da bud'e baya kwantar dani yayi sannan ya dawo gaba yana zama yayi shuru Adam yace "wayaga mijin mata hud'u ta hud'un ma yarinya yar Sha uku.. Allah sarki yarinya har na hango yanda za'ayi wasan qwallo dake" dukan wasa Arab ya Kai mishi "banson Shakiyanci mubar wannan maganar Wallahi fargaba na bansan yanda zamu kwashe dasu ba" tsaki Adam yaja "inna jin takaici haba se kace ba namiji ba! Ka tsawatar musu ma ya gagareka Wai ace kana da mata har uku ba kwanciyar hankali fitinar yau daban na gobe daban wallahi idan ka Kai musu wannan mareniyar suka cutar da i'ta kai da Allah domin bawai biyan bashi kad'ai aka baka ba, wallahi amanace iyayenta suka baka inka barta matanka suka nakasata Kai da Allah" Arab yace "naji Kai gwara na kaita Zaria ko na mikata Gurin Hajiya kawai , mahaifiyarshi Kenan" Adam yace " wallahi kanada aiki gwara de ka Kai musu Susan matsayinta a gurinka" Arab yace "shike Nan" a haka suna hirarsu har suka karaso abuja.

Nik'an innata ramuwar barcin da banyishi kwanakin baya ba Gidan shi nacan gaba da babangida market , Gidane babba Wanda fad'ar had'uwa da tsaruwanshi bata lokacine hon adam yayi megadi ya bud'e mishi kofa yana gama fakin suka fito hannu Adam ya Mika mishi sukayi musaba daga Nan ya Mika mishi makullin motarsa "To abokina fatan alkahairi zan d'auki motana nima naje naga tawa Matar a kula da 'yar mutane Dan Allah" Arab yace "nagode a gaida Maryama" Adam yace "insha Allahu" bud'e bayan motar yayi tare da Kiran sunana jiddah bud'e ido nayi "fito Arab na jiranki"
"Waye Arab?" Adam yace "To mijinki" take idona ya kawo ruwan hawaye haka na fito kai seda na tsorata wallahi na d'auka ba mutum bane farinshi yayi yawa kaman ka tab'a jikinshi jini a fito kasancewar d'azun ko kallonsu ma banyi ba bare nasan yanda yake babban mutumne Amma kud'inshi ya b'oye girman nashi.

Gaba yayi nabi bayanshi muna doso kofan gabana ya buga ras tsayawa shima yayi kafin ya juyo ya kalleni girzgiza k'anshi yayi tare da tura kofan kwan..! Se sauk'an kofin glass a goshin sa har hulanshi ya fad'i dafe goshin yayi tare da fad'in "waiku wasu i'rin dabbobi ne! Kullun se kuci ku hau ihu kaman karnuka ! jubi Gidan Nan kullun a hargitse ni Kenan inna da mata uku bani da kwanciyar hankali haba! Haba!! Wannan wacce i'rin masiface" nide kasa nayi na d'auko hullanshi ji kawai nayi an fisge Juyowa nayi Dan inga wacece wata farar mata ce fiska a d'aure ta kalleshi sannan tace "Ibrahim Nafisa ce masifar ko Zainab dan ni Fure wallahi baka isa ka kirani da masifa ba Ga karnuka nan..." tana nuna Nafisat da Zainab "Kutuman uban Amma ke Fure'atu anyi yar..." Faf Fure ta make mata baki Nafisat ta kamo wiyan rigan Fure "ke yanzun Dan Kinga kinyi Kiban rashin zuciya shine zakice min kariya kazama dake shegiya me warin hammata..." Wallahi bansan lokacin da na k'yalky'ale da dariya ba kalli tib'a tib'a dasu Wai suna fad'a da junansu.. juyowa sukayi shi kuwa ya jani bayansa Dan yasan halinsu zasu i'ya makeni a gabanshi ba damuwarsu bane "Ke Kuma daga I'na aka rarumoki kasan de bama bukatar 'Yar aiki ko?" Arab yace "Kai! Kai!! Ya isheni haka haba!! Duk kunbi kun cikawa mutum kunni..." ZAINAB tace "Heee Tsaya nima kana cikamin kunni Bayani zaka Mana wacece wannan?" Ta karasa maganar tana jawoni "ku zauna na muku bayani to" Zama sukayi a kasa dukkansu domin kujerun ma an turasu gefe tsaban fitina da bak'in kishi i'rin nasu.

Seda ya jawo D'aya ya zauna domin be i'sa yace a kawo mishi abin Zama ba yana Zama ko sauke numfashi beyi ba Nafisat tace "munajin ka" Arab yace "yanzun ko arzikin ruwa da abinci bazan samu ba..." Fure tace "Kai kai dakata Ibrahim babu baiwarka anan ka Mana bayani wannan" nunani tayi Arab yace "Matatace.." wayarshi ne yayi kara mikewa yayi tare da fad'in "Ku bata abinci da masauki inna zuwa" fita yayi da sauri yana Kara wayan a kunninsa.. a sukwane Fure ta tashi hannuna ta kama "ke fad'amin Gaskiya Wai da gaske Auro ki yaje yayi ko sadakarki aka bashi domin nasan halin mijina seya wanke hannu kafin yake zab'o mace kalle ni da kyau ki kalli sauran kin gammu da muni?" Girgiza mata Kai nayi Nafisat tace "fad'amin da gaske ke matar shi ce?" Shuru nayi Zainab ta zaburo tare da daka min tsawa "Ke ba magana ake Miki ba!" Da sauri nace "Eh Eh matar sa ce ni..." Ai ban rufe baki ba naji ta d'aukeni da mari fau.. har seda gefen bakina ya fashe da sauri Nafisat tayi kichin galan d'in karanzir ta d'auko tashiga zazzzaga min a jiki Zainab ta cire min himar ihu nasa Fure taje ta d'auko a shana Tsayawa tayi tana karemin kallo "in banda maza ma da shegen jaraba uban me zeci a jikin wannan yarinyar Qirji a shafe ba cinya ba sharab'a Yau zakije lahira in aka tambayeki ya'akayi kikazo a haka kice *Matan Mu'azzan Balarabe* ne suka jefoki baki shirya ba tana shirin k'yatta ashana ya shigo a guje dan tun a waje ya fara jin hayaniyan su yana doson kofan yaji ihu na abinda yasa ya shigo a guje ke Nan ture fure yayi ta fad'i ragwajan kafin suyi wani Yunkuri ya d'aukeni kaman yar Baby da sauri ya fita Zainab da Nafisat ne sukabi bayanmu "Bud'e min Get da sauri" makuli yasa ya bud'e motan domin gudun ma be karb'esu ba Sabida Kiba Ta gurin Direva ya turani a kujeran gefe motan ya shiga yaja kofan a guje yaja de de lokacin da suke karasowa da gudu suka rufa mishi suna nishi "Zainab tace zaka dawo ka same mu wallahi" juyowa sukayi kowa na zuba masifa a bak'in kofa suka samu Fure'atu "Ina suke?" Cewar Fure Nafisat tace "Ya tafi" Fure tace "aikuwa ze dawo ya sameni" Zainab tace "i'rin ke kad'ai ce matarshi dole ya dawo ya sameki ai"

Maman Faruq

12/26/23, 8:58 AM - UMMI JB: *SIRRIN ƊAUKAKA*

_Wattpad@ayshajb_

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION*

Page4 .

............Yana tuƙi yana shafa goshin shi, domin kofin Da aka jefo masa harya fasa mishi gurin Tausayi ya bani har bansan lokacin da na cire D'ankwalin kaina na mika mishi ba cikin masifa yayi magana "Ke dallah barni wannan kayan karanzir d'inne zansa a jikina Allah ya kiyaye duk ba ke kika jawomin wannan fitinan ba" Shuru nayi tare da mayar da d'ankwali na, kuka nasa inna mishi ihu harda dukan kujeran da nake kwance "Wallahi baka i'sa ka d'aukoni daga garinmu ka kawoni cikin wannan kattin banzan ba ance maka bani da gata ne! su sumin kaima ka fasamin kai da ihun ka wallahi kamayar dani inda kad'auko ni" gaangarar da motarshi yayi tare da tsayarwa "Ke! Da kike maganar kina da Gata uban waye gatan naki inba ni ba haba! wannan wacce i'rin masiface haka ! karna kuma ji kin kiramin matana da Katti inba haka ba wallahi zakiji a jikinki" wallahi bansan ina da masifa ba se yau "Allah ne gata na domin kai ba gatana bane , matanka kuma nace katti kayi duk abinda zaka min kai! nifa ba jakarsu bane da zasu fasamin baki wallahi sena rama kuma karka karacemin masifa domin ka barosu a baya kuma zaka koma ka taddasu domin na rantse da wanda raina ke hannunsa baka i'sa kamar dani wancan hargitsattsen gidan ba, Gidan jahilai wanda basu san kishi ba..." fauf ya bigemin baki "Allah ya isa kai kaci zalina matanka suci Zalina akwai Allah wallahi kuma seya saka min tunda ban muku komai ba" inna fad'ar haka naci gaba da kuka Na shikuwa shuru yayi ganin haka yasa nace “Nifa bansan amfanin tsayuwarnan da kayi ba in baka da inda zaka kaini ka bud'emin mota na fita.." Hannu ya d'agamin tare da d'aukan wayarshi dake kara tun d'azu “Adam wallahi akwai katon matsala kaina duk ya kulle bansan Ya zanyi dasu..." Nan ya kwashe komai ya fad'a mishi me Adam zeyi kuwa in banda dariya matarshi dake gefe ta rik'e baki tana kallon i'kon Allah Arab yace “Kaga malam banson hulak'anci ya zan fad'a maka abinda sukamin maimakon ka bani shawara se ka b'ige damin dariya mahaukaci ka mayar Dani?”
Adam yace “a a yi Hakuri yanzun kuzo Gidana Amma kafin nan ka siyo mata wasu kayan da Zata canza” Arab yace “Toh” duk inna jinsu kala bance mishi ba ya tada motar munyi nisa da tafiya kafin ya tsaya kusa da wani kantin kaya inna zaune a cikin mota ya fita ya siyo ya dawo tafiya kad'an mukayi se gamu a kofar wani madedecin Gida Adam d'inne ya Bud'e Mana Get yana gama faka mota ya fito Arab yace “Wai kai har yanzun bazaka sa megadi ba? Kafi so in kayi bak'i kazo ka bud'e musu get in Kuma ka fita Ruma ce zata bud'e Get yanzun Kuna jin dad'i rayuwa haka?” Adam yace “Taya zansa megadi ya ringa kalle min mata a a wallahi inna kishin matata rayuwarmu a haka yayi in nafita na dawo tazo ta bud’e min kofa ina dalili" nik'an da zaman motan ya isheni na shiga bubbuga glass da sauri Adam ya bud'e min na fito wani uwar harara na maka musu kafin naja gefe na tsaya gaba Adam yai yana dariya “Arab ka Tara mata kutt kowa da guntun nata rigiman muje ciki" Matarshi Ruma na zaune ta amsa sallamarmu da fara'arta Zama nayi a kasa tare da fasa ihu Arab yace “Kefa na lura mahaukaciya ce karki tasar

musu yara suna barci...” birgima nashiga yi ina duk'an kasa “wallahi ni ba mahaukaciya bace sede matanka sune mahaukata nide dan Allah kuce ya mayar dani garina na fasa Auren zan biyashi kud'insa” Hannu ya d'aga ze mareni Adam ya rik'e shi “Haba Ya zaka huce akan karaman yarinya marainiyan Allah wannan ba yi bane Gaskiya koda wasa karka sake marmarin D'aga hannunka zuwa jikinta Su sauran matan naka kana duk'ansu ne?” zaune na tashi “Wallahi daka barshi ya dakeni tunda na Zama jakarsu kalleni fa jikanin sukayi da karanzir zasu k'onani bayan sun fasa min bak'i shima dan rashin imani ya sake bug'emin bakina Allah daka barshi inya dakeni zan rama ai ba jaka bace ni, in Kuma Kuna ganin banida Gata babu me tsayamin dan,ni talakace akwai Allah zan Kai mishi karar ku tunda ba zaku iya duba maraicina ba” tausayinta ne ya kamasu maganarta Kuma gaskiya ne Ruma ta Mike tare da kamo hannuna “Kiyi Hakuri Jiddah Allah ze saka miki zo muje kiyi wanka se kici abinci” Mikewa nayi nabita “Gaskiya abokina abinda kayi kaida matanka be kamata ba yarinya karama zakusa a gaba haba Mu'azzan bansan ka da duk'an mace ba” Zama Arab yayi tare da dafe kai “Ni wallahi Adam bansan mesu Nafisat sukeso dani ba, kullun burinsu suga hankalina a tashe sun mayarmin da Gida kaman filin dambe ban isa Kuma na hanasu su hanu ba ya zanyi ne wallahi nagaji kasar zan barmusu na huta da wannan fitinar, Mata Uku ko Gobara?” ..
“Wallahi ka i'sa ka Hana Kuma su hanu inhar kaci gaba da nuna musu kana tsoronsu abinda zasuyi maka Nan gaba seya fi haka, Ga abinci kaci kaima se kayi wanka” Band’aki ta kaini Tsayawa nayi inna bin gurin da kallo kwab'a baki nayi zanyi kuka tace “Ya salaam! Meye Kuma?” Seda na gama cire kayana kafin nace “toya zanyi nayi wankan?” bata ja da tsayi ba tamin wanka tsefe kitson da yafi wata uku tayi tare da wanke min kai mun dad'e a bayin domin Gaskiya ta wankeni sosai Kuma na wanku sede hasken fatata ta fito tana wankeni tace “Masha Allahu Tubar khallah Ibrahim ta zab'o mana kala me kyau wankan tarwad'a” babban tawul ta bani da sufe jikina yayinda take goge kaina da karami seda ta busar min da gashin da wani abu ko menen oho gurin Jane na ringa mafa ihu domin da zafi Nan da Nan gashina na sake ya kwanto har wiyana, ga shi baki sid’ik Mayuka masu khamshi ta shafani dasu “Jirani inna zuwa” Falo taje Amma babu kowa ledan dake gurin ta bud'e Nan taga kayane doguwan riga me ruwan zuma ta d'auko da d'ankwalinsa Duk ta duba kayan babu kanfe dole cikin kayan yaranta ta samo karamin wando nasa Himar ta bani nasa Nan nashiga yin sallolin da banyi ba inna idarwa ana Kiran isha, sallan isha'in nayi naso inyi shafa'i da hutiri sena tuna inna tashin dare Dalilin da yasa banyi ba Kenan Zama nayi inna lazumi se takwas da rabi, nabar saman Sallayan duk abinda nake Ruma tana kallona ji kawai tayi na birgeta barinma yanda nake abubuwana cikin nutsuwa “Zo muje kichi abinci” Bin ta nayi har falon d'azun zama nayi a kasa ta zubomin tuwon shinkafa da miyan taushe se farfesun kayan ciki.
inna cikin cin abinci Ruma ta fara min fad'a “Jiddah karki Kara d'agawa Arab murya in yana fad’arshi in bazaki iya ce masa yi Hakuri ba karki kuskura ki tanka masa Sannan ki Dena ce mishi kin barshi da Allah Kinga babu kyau yima babba rashin kunya matsayin miji yake a gareki tunda wa'yancan banzaye sun kasa rik'eshi inna so ke ki rik'eshi ki jawoshi a jikinki sosai ki zama me share mishi hawaye a duk lokacin da yake kuka da halayyarsu ki zama maganin damuwarshi karki Kara d'aga mishi murya domin babu kyau mace ta ringa d'agawa mijinta Murya sannan innaso in yazo kice ki tsuguna har kasa ki bashi Hakuri matan shi Kuma babu runki dasu ki Dena ce musu katti Kinga sun girme Miki tsakaninki dasu mutumtawa da girmamawa Kinji” tunda ta fara min nasihar Nan nayi shuru ji nake kaman mamana ne take min magana cikin sanyi murya nace Mata “To nagode Mama Amma dan Allah kice ya Dena dukana

iyayena har suka rasu babu Wanda ya tab'a dukana Kuma kice mishi ya Dena cemin mahaukaciya bana so kalman yamin zafi” sharemin Hawaye Ruma tayi kafin tace “insha Allahu bazai Kara ce Miki mahaukaciya ba matukar kikayi abinda nace miki Kinga anan zaku kwana Kuma d'aki d'aya inna so idan kunje kwanciya kice mishi ya yafe miki bazaki sake ba, Kuma Gobe ze kaiki Zaria ki gaida mahaifiyarshi daga Nan ze kaiki Kaduna Gidan Yayarshi i'ta zata rik'eki zata zame Miki uwa da uba domin malamace zata koyar dake abubuwa kala kala Dan Allah banda rashin kunya ki Mata biyayya kinji” Gyad’a Mata Kai nayi kafi nace “Amma kince d’aki D'aya zamu kwana Kuma babu kyau fa...” katseni tayi “Ai mijinki ne da kaman ba mijinki bane shine za'ace babu kyau” ..
Kafin na Kuma cewa wani abu se gasu sun shigo kasa kasa na kalleshi Nan naga ya canza kaya da alama shima yayi wanka tab'ashi Adam yayi tare da yin magana kasa kasa “Kai Arab kaga Amariyarka kuwa Gaskiya ka samu mata Ashe haka take da kyau” Had'e Gira Arab yayi ba tare da yace komai ba sema satar kallonta da yakeyi batare da anlura dashi ba ,  Zama sukayi Arab yace “Sannu da kokari Ummuh Rumana” murmushi kawai tayi ba tare da tace komai ba “Karfe Tara fa ya gota madam na fara jin idanuna na rufewa Arab asuba ta gari ga makullin d'akin” Karb'a Arab yayi Adam na shiga d'akin Ruma shima Arab ya Mike ya bud'e kofa “Tashi kije ku kwanta karki manta Kuma da abinda nace” wanke  hannu nayi nace Mata “Seda safe Ummuh”  Murmushi nima tamin kafin tace “Allah ya tashe mu lafiya” kwashe kanunk'an abincin tayi seda ta gyara Gurin kafin ta kashe kwan wutan ta nufi D'aki , da Sallama na tura kofan yana zaune bak'in katifan dake shimfid’e a kasa ya amsa min Durkusawa nayi tare da fad'in “Allah kayi Hakuri da abinda na maka in Allah ya yarda bazan Karayin rashin kunyar ba” da sauri ya kalleni Mamaki ne ya cikashi shine yau mace take durkushe a gabanshi tana bashi Hakuri abinda be tab'a faruwa dashi ba lallai a gaida Ruma dan yasan i'tace tasa Jiddah “Kaji kayi Hakuri” maganarta ne ya Kara katse shi “Naji kema kiyi Hakuri da abinda matana suka miki” A hankali nace “Na Hakura Amma dan Allah karka sake kaini Gurinsu domin zasu kasheni ne tun kafin burina ya cika” ..
“Meye burin naki” Zama nayi sosai kafin na fara mishi lissafi “burina idan na girma nayi karatu na samu aiki zan Gina katon Rijiya Kuma inyi bohol zan Gina islamiya na marayu zan ringa tallafawa gajiyayyu...” cikin gajiyawa da maganarta yace “Naji Allah ya kaimu zoki kwanta kiyi barci nik'an barci nake ji” yana fad'in Haka ya shiga cikin Gadon tare da rufe kanshi da sauri Kuma ya bud'e bargon “na manta ga maganin a saman firizan can ki balle kisha seki kwanta” Da nasha maganin memakon inhau Gadon sena koma na zauna tare da d'ora kaina saman Gadon shuru shuru beji tazo ta kwanta ba yasa shi mikewa “Ke a Haka zaki kwanta?” d'agowa nayi cikin turo baki nace “To ai ba kyau a kwanta gado D'aya da namiji” Dariyan Shakiyanci yasa sannan yace “Amma baki da hankali an fad'a Miki wani abu zan Miki? Me zanci a jikinki? Me zan shafa naji dad'i abu sur Kashi gani da cikak'ku had'add'un mata me zanyi da jikin yarinya! inma zaki zo ki kwanta gwara ki taso” murkud'a mishi baki nayi “oh koma menene nide nace bazan hau Gadon ba” saukowa yayi “To Ni na sauka jeki kwanta” Ai da sauri nace “Wa? Bade Ni Jiddan ba gwara ma kayi kwanciyar ka, ni hakan yamin” be ja da tsayi ba ya koma yayi kwanciyarshi nima a Haka na kwanta kayana.

Maman Faruq
12/26/23, 8:59 AM - UMMI JB: *♡SIRRIN ƊAUKAKA♡*

_Wattpad@ayshajb_

®🌁

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION..*

FREE BOOK

Page5

Barcin ma rabi da rabi nake yinsa domin tsoron ya taɓani nake ji can da barci ya fisgeni naji ya cicciɓeni ya dora saman gadon zabura nayi tare da kurma ihu jikina na ɓari dan ko gizau be yi ba, haka ya ajiye ni tsawa ya daka mata. "Ke mahaukaciyar Inace! in banda wawanci irin na ɗan kauye me zesa ki kwanta a kasa sanyi na shigarki, Ina miki Gata kina kaucewa" na tsani tsawa ban sabaji ba, domin har iyayena sukabar Gidan duniya basu taɓa tsawata min ba, shiyasa na toshe bakina da hannuna kalmominsa sun ƙona min rai sosai ajiyan zuciya nake saukewa hawaye na wanke min fiska haka ya gama cimin mutumci ya kwanta abinsa takurewa nayi sosai Ina ajiyan rai barci ɓarawone ya ɗauki "Bansan ki da wannan halin ba jiddah lokaci ɗaya kina kokarin fanɗarewa! raina na ɓaci in naji kina mayarwa mutumin daya amsheki batare da ya musa ba!, me akayi ko? hakuri zakiyi domin Guguwa na nan tana tunkaroki sekin tsunu ki sanyawa ranki hakuri... "amma Mama kina gani daga zuwana matanshi zasu kassarani shima zagina fa yake yi har cemin yai mahaukaciya yamin zafi! naji ciwo bazan iya ba!.." shafa kanta tayi kibar kuka kiyi hakuri da komai shi zaman duniya ɗan hakuri ne karna kuma ji kin ɗaga mishi murya.." Gyaɗa mata kai nayi cikin wani irin juriya nace "insha Allahu mama bazan sake ba" murmushi tayi tare da share min hawayen dake sauka kuka nasa sosai Ina jin raina na zafi zan sake magana ta hanani Ina kuka naji ya daka min tsawa ashe sosai nakeyi domin sautin muruyana na fita, "ke tunɗazu nake tashin ki kinyi banza dani kina kukan banza" miƙewa nayi jikina na rawa hawaye na zubamin ban taba tsintar kaina cikin quncin rayuwa irin na yau ba, hanyar banɗaki ya nunamin na shiga tsarki nayi da alwala Ina fitowa naga ya shimfiɗamin sallaya ga himar ma , fita yayi nima na tada ikama sallanake inna kuka cikin sujadata Ina kai karansu gurin Allah kaina nakasa har ya dawo ya zauna a gefen gado, ɗagowa nayi na sallame sallan ɗaga hannuna Ina addu'a a bayyane "Allah kaji ƙan iyayena sanyi idaniyata abaɓen alfaharina allah yakai haske da rahama kabarinsu allah ya yafe musu zunubansu allah ya haɗasu da annabinka annabin rahama sallallahu alaihi wasallan, Allah na kawo karan wasu bayin ka, wanda sukayiwa rayuwata dirar bazata ba tare da na shiryawa haƙan ba, Allah ka shiga tsakanin nagari da mugu Allah kamin katangar karfe dasu Allah duk wanda ya zalunceni kabimin haƙƙina Allah ka yafe kuskurena..."kukane yaci karfinta haka ta shafa addu'ar ta mike tare da ninke sallayar Tsungunawa nayi gabanshi "ina kwana?.." cikin masifa yace "daban kwana ba, zaki ganni? watou har karata kike kaiwa gurin Allah gani azzalumi ko?" ban kulashi ba na tashi haka ya ringa cin mutumcina ko cin kanka bance mishi ba, karshe ma fita nayi a ɗakin,

suna zaune a falo durkusawa nayi na gaida adam cikin sakin fuska ya amsa min "Ummuh Ina

kwana?" nace mata Ina kara sunkuyar da kaina kasa "matso nan ƴata" domin a haife ta haifeta matsowa nayi na kwanta a jikinta kukan da naketa matsewa ne ya kwace min, kuka nake sosai shafa kaina tayi tare da faɗin "A duk lokacin daka tsinci kanka cikin Qunci rayuwa kace alhamdulillah base Allah ya jarrabeka da abin farin ciki zaka gode masa ba, ki zama me amsar kaddarar aduk yanda tazo miki.." gyaɗa mata kai nayi "inshaallahu nagode da tunatarwa" murmushi tayi sannan ta nuna min abinci kaɗan naci sabida raina a ɓace yake, miƙewa yayi bayan ya gama cin abinci "tafiyan kenan?" adam ya tambaye shi kallon agogon dake ɗaure Tsitsiyar hannunsa yayi tare da taɓe baki "lokaci na tafiya ki tashi" ya fad'i haka tare da tsare ni da ido rai a had'e danne kukan dake shirin kwacemin nayi tare da mikewa nayiwa ummuh sallama suna gaba Ina biye dasu har gurin mota Ummuh ta rakomu tana mana fatan Alkhairi, hannun sukayiwa junansu kara rikeshi Adam yayi "Arab dan Allah ka sauko da zuciyarka kasa yarinyar nan a firgice take da kai.." "naji!" a takaice ya fad'a tare da bud'e motar ganin bana gaba yasashi tsayawa turus cikin bala'in yace "Ke fito ki dawo gaba!" Ina zaune na jingina da jkin kurejar idona a rufe bamma san yana magana ba, domin nayi nisa a tunanin yaruwar data riskeni,

"Ke dan gidanku Ina miki magana kin min shuru nine zan zama direvanki? "Kayi hakuri..." cikin kufula yace "fito ki dawo gaba" jiki a sanyaye na fito nan naga duk basa nan ajiyan zuciya na sauke domin na tsani cin mutumci a bainin naasi, haka na zauna na mayar da fuskana jikin glass Ina kallon waje shigowa motar yayi tare da buga murfin yana jan tsaki nide ban kulashi ba, domin Allah kaɗai yasan abinda ke raina kiris nake jira na sauke nawa kwandon rashin mutumcin domin tunda ya shigo rayuwana hakurina yayi karanci,
***
Tafiya kurame shine tafiyar da mu kayi munyi tafiya sosai kafin ya tsaya a wani kauye fita yai yaje yin sallah ganin be cemin kala ba, nima na fita, ruwa na zuba a buta naje bayan gurin nayi tsarki sannan nayi alwala na rigashi dawowa cikin motar domin yaje siyan abinci koda ya dawo tekawey ya ajiye bemin magana ba nima kuma ban kulashi ba haka muka ci gaba da tafiya komai ya siya seya ajiye ni kuma banyi karanbanin tab'awa ba, ashe ranshi ya b'aci har barci ya fara fisgata ya taka wani wawan birki motar tayi gaba ta dawo baya kainane ya bugu na dafe hannunna a gurin Ina cije baki domin naji zafi sosai ban zata ba , ya jawoni tare da had'a himar dina da wiyana ya shakeni sosai "Ni kika mayar asararre? in kashe kud'ina gurin siya miki abinci amma ki brshi ya lalace ga soko ko?" hawaye ne ya shiga zariya wani nabin wani da kyar nayi magana domin numfashi na ya fara barazanar barin ganagan jikina "Daka siya kace min Hauwa'u gashi? ko kace naci ne da zan d'auka ? an fad'a maka ni mayunwaciya ce , to ban bukata shi kenan! d'auki kayanka, Arab ka shafa min lafiya ka fita sab gata..." tureni yayi na bugu da glass din motar me shegen karfi abin bakin ciki kainane ya fashe amma glass din ko tsagewa beyi ba haka ya figi motar a guje ..

ajiyan zuciya kawai nake iyayi ga hawaye da yaki dena tsayawa kaina wani mugun ciwo yake min azzalumin nan ko ya juyo yaga halin da nake ciki ajiyan zuciya na sauke me karfi domin wani gargada muka shiga shi kuma yaki tafiya a sannu, seda na kara buga kaina daga nan bansan meya faru ba tsaban a zaba se farkawa nayi na ganni kaina jikin wata dattijuwa fara sol, ga kyau ga ,gayu jikinta mul-mul ajiyan zuciya ta sauke shi kuwa yana zaune fiskan ,kan da d'an dama cikin tsamin hausarta tace "jeka kira likitan" yana fita ta dawo da dubanta gareni rufe ido

nayi itama bata takura min ba, ashe suma nayi koda muka iso zari'a ya tab'a ta yaji jikinta zafi rau gashi bata motsi shine y ciccib'e ta a falo yaga iyammu "cikin takaicin halin d'an nata tace koma kayi sallama domin ba d'akin kafura ka shigo ba, ai ko arnan suna konkon.."

"Dan allah iyanmu kiyi hakuri ki duba halin da ƴar nan take ciki.. "dakata! ince bakin halin naka ne ka gwada mata, dukanta kayi ka fasa mata kai bayan rashin tarbiyan da ƴan boko suka nuna mata (matan shi take nufi) kashe musu 'Ya kake son yi ba, kaje ni ba abinda zan muku na zare hannun na zaga iyalanka.... "dan girman Allah ki gafarce ni wallahi ba abinda kike zato bane iyanmu ba abinda na mata" share shi tayi taci gaba da karatun ta, ajiye jiddah yayi kaman ze mata kuka da kyar ya shawo kanta shima da sharaɗin ze tsaya a gidanshi ya zama namiji, ya amsa mata ne kawai amma bejin ze samu karfin gwiwar tsawatar musu domin suna haɗa mishi zafi su gwara kanshi yanda suke so ne, daga karshe seda suka danganta da asibiti tare da likita suka dawo ya cire min karin ruwan shayi ta had'a min kad'an nasha na shiga yun kurin amai iska ta ringa hura min tare da watsamin ruwan sanyi har aman ya koma "sannu fa Allah yana sane dake fatana ki zama haske a rayuwarshi Allah ya dubi lamuranki ya saukaka miki, ubangiji ya ɗaukakaki" wani kuka ne ya kwacemin bata hanani ba seda nayi me isata kafin nayi shuru Ina sauke ajiyan zuciya sallama aka bamu muko koma gida kaman wani me aljanu mun isa gidan ko cikakken min ashirin bamuyi ba ya mike lokacin Ina kwance a doguwan kujera iyanmu tana duba ishmawiy ya mike "Iyanmu zamu kaduna domin a gidan sawda zata zauna"

cikin gatse tace "tsawon shekara nawa?" gaba yayi tare da ɗaga kafaɗa "zuwa lokaci da allah ya takaita zamanta a gidan... "kaci gidanku" murmushi yayi tare da fita kallo na tayi tare da juyar da kai tausayin yarinyar take ji, i'ta kuma haka Allah ya kaddara mata shiga cikin iyalan Ibrahimu Gidan da ake rayuwa cike da bakar kishi, "tashi ki bishi Allah ya tsare, zanso ki mayar da hankalinki kan karatu musammam ma, ta mahamadiya domin zata temaka miki qwarai wajen inganta rayuwar aurenki zanso ki fita zakka wajen ilimin islama a cikinsu domin Allah ya jefoki ne tsakiyar matan da suka jika da boko matan da basu bawa mijinsu mihimmanci kaman yanda suka maida hankulansu kan ayyukansu ba, zance ma gwara Nafisah" nide ban bawa zanceta muhimmamci ba domin na rasa inda ta dosa Allah ya temaka ma nayi wanka asibiti ..

Ga link Dan Allah idan kinsan ba karantawa zakiyi da comments ba karki shiga!

https://chat.whatsapp.com/HsMb0FG2FMMFCBLoDfHoyQ

*Maman Faruq*
12/26/23, 9:00 AM - UMMI JB: *♡SIRRIN ƊAUKAKA♡*

_Wattpad@ayshajb_

®🌁

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION..*

FREE BOOK

Page6
Jingine da motarshi yake yana ganin fitowarta ya shigan tare da rufe murfin  a hankali nake tafiya har na karasa inna shiga yaja motar juyar da kaina nayi gefe har munyi nisa da tafiya kafin ya waigo. "i'tace mahaifiyata iyanmu mu Shida ta haifa, Sawda ce babba tana aure a kaduna malamace yarinyarta ɗaya tal, sai Musa shi kuma yana sudan da iyalanshi sai Abbas shima yana sudan Aminu yana Bauchi nine na biyar se karaman mu Zaliya wanda take ABU Mahaifin mu ya rasu shekara shida  kenan" bance mishi komai ba har muka isa Kaduna Gidanta baban gidane a gefe guda akwai makaranta wanda ake koyar da matan aure har da na ƴan mata da yara megadi ne ya buɗe mana get yana de-deta tsayuwar motar muka fito yana gaba inna biye dashi a baya  Da sallama muka shiga falon ba kowa zama yayi tare da nuna min kujera memakon nayi yanda yace sena zauna a kasa.
  Shuru mukayi na yan mintuna kafin ya katse shurun ta hanyar fad'in, “na kawoki nan ne domin ki zauna na d'an lokaci ki mayar da hankalinki kan karatun da zakiyi domin matana ba jahilai bane , ko wacce da kika ganta da iliminta da sana'arta matsalar ki ne ki nutsu kinyi karatu domin inganta rayuwarki domin mahaifinki Yana da burin kiyi karatu banda shirme... "Hmmm kasan aiki nane shirme ai Daman nace matanka jahilai ne , daga zuwa na sun nuna min kalar tasu ilimin, da kace na mayar da hankali ko karna mayar ince hankalin nawa ne? Kuma a jikina yake, nagode insha allahu zanyi karatu zan nutsu kodan nacika burin Raina" Gyad'a Kai yayi kafin yace. “yana da kyau.." "Daman ba kyau ne?" Na fad'i Haka inna lanƙwasa hannuwana..

"Ki kiyaye harshen ki, kisan abinda zaki ringa furta min karki bata min rai"

Sunkuyar da Kai nayi kasa.

"Kayi hakuri insha allahu zan kiyaye"

"Assalamu alaikum" tace kafin ta karaso cikin shigar kamala a nutse ta zauna kusa dashi.

"Amin wa'alaikis Salam barka  sawda malama Sawda ummin halimatu"

Murmushi tayi kafin ta juyo gare ni "inna yini" nace mata murmushi tayi kafin tace "lafiya lau hauwa ya gajiya da hakuri da k'anina?" Ta karasa maganar tana kallonshi bance Mata komai ba had'e fiska yayi "haba! Dan Allah ai seki sa ta renani" a hankali yayi maganar,

Girgiza Kai tayi kafin tayi waya kichin "Yahgana ki kawo abinci" kashe wayar tayi , tare da mikewa "Zo muje kiyi wanka da sallah kafin ta kammala"

Ɗakin Halima ta kaini tare da nuna min Banɗaki wanka da alwala nayi inna fitowa ta shigo da bakar leda "Yanzun arab ya aiko kiyi amfani dashi. Bance Mata komai ba ta fita Dogayen rigunane guda Shida se Himar da kananun tarkace a Raina nayi tsaki kafin na saka D'aya daga cikin kayan sallahn dake kaina duka nayi kafin na kwanta saman salayan Nan da Nan barci ya

dauke ni cike da gajiya..

Yana ganin shigarsu shima ya mike masallacin dake wajen Gidan ya nufa anan yayi sallah ya dawo  abincin da aka jera ya zuba ya fara ci, Ummin halima ce ta shigo "Hauwan bata fito ba?" Ba tare da ya D'ago ba ya Gyad'a mata Kai.

Dakin ta shiga Nan ta isketa kwance Girgiza kai tayi tare da dawowa "Ya naganki ke d'aya Jiddan fa" "Barci take"

Shuru ne ya biyo baya na d'an lokaci kafin ta tsake shurun ta hanyar fad'in "Muazzan naga Goshin yarinyar Nan da ciwo inna fatan ba matan ka bane suka sila?" Da sauri yace "a'a ba ko d'aya me ruwan su da i'ta da zasu tab'a ta" Qurr ta masa da ido badan ta yarda ba tace shi kenan.

"Wani shawara ka yanke game da rayuwarta?"

"Eh to in naga zan baki kudi kiyi yanda ya dace domin anan zata zauna inna tunanin inna had'ata da matana Gaskiya Bazata ji dad'in zama cikin su ba, abin da ya dace kawai tayi zaman ta Nan tunda Kinga Ga Halima naga Hanisa ma tana Nan (Yar Aminu tana karatu Gurinta). Katse shi tayi "Ban ki maganarka ba, Amma har tsawo wani lokaci Zaka tsaya a Gidanka yaushe zaka zama namiji me fad'a aji, haba! Wannan wacce irin rayuwa ce ace mutum bashi da 'Yanci shida gidanshi baka isa ka zauna na minti biyar ba tare da an tada hayaniya ba inna jin zafin wannan abun Mata uku Amma duk ba me Hankali.." Mikewa yayi cikin Gajiya da jin kalaman ta sosai suke tab'a zuciyarshi murya a dakile yace "Zan tura Miki kudi kiyi duk yanda ya dace ni na tafi"

"Dole ka tafi tunda an tab'a maka Zinari Allah ya kyauta saura Kuma ka share Yar mutane dan nasan halinka sarai... "Daman me zan Mata? bana tunanin zan zauna da yarinyar nan fa, domin bata cikin tsarin matan da nake so Gata bak'a yar K'auye ba ilimi kai bata min ba ko kad'an sallamarta tayi taje tayi rayuwarta..."

"Allah ya nunamin ranar da zaka zo kace in baka Hauwa Allah ya kaimu lokacin da har kasa zaka rok'e ni in baka matar ka ni kuwa a lokacin zan gwada mata bade haka kace ba? Zaka ga yanda Bak'a yar K'auye zata b'ata Lissafi da tunaninka a sauka lafiya"

D'aga kafad'a yayi alamar maganarta bai dameshi ba fita yayi yaje ya bawa motarshi wuta hotel ya kama domin washe gari ze juya,

Tun lokacin data bar d'akin na farka Band'aki nashiga tare wanko fiskata nabi bayanta Amma kafin na karasa na farajin maganar Arab da Hannun na rufe bakina domin wani i'rin kuka me ciwone naji Yana shirin qwace min duk ni d'aya yake jifa da kalaman Nan, me namishi da zafi silalewa nayi na zauna a qaka hawaye na bin fiskata bansan iya lokacin dana d'auka ba naji sallaman mutane biyu da sauri na tashi na share hawaye na falon na shiga cikin fara'a tace "harkin tashi bisimillah zoki ci abinci" Sunkuyar da Kai nayi kasa a hankali naji yaran da suka

shigo d'aya wacce nakega zamuyi sa'anni tace "Ummina wacece wannan Black beauty din?" Matar Kawun ki ce wacce nake Baki labarin suna hanya" zata sake magana na kusa da ita ta make bakina "Haba Hanisa meye haka.." wacce tacewa Hanisa na kalla a qalla zata Kai sha shida , tace "Wallahi Halima kin fiya bin ƙoƙof" hararanta Halima tayi kafin tace min ."ya Sunan ki"

"Jiddah"

"Suna me dad'i zamuyi Qawance?"

Murmushi nayi kawai tare da mayar da hankalina kan abinda nake ,

Wani i'rin kallo Hanisa take bin ta dashi ba tare da kowa ya lura da hakan ba, mikewa tayi ta nufi Dakin su wayarta dake makale da Caji ya cire tare da Kiran mahaifiyarta tana d'auka tace "hello umma Kinganta kuwa yarinyace fa wacce a yanzun take 14, akwai kyau duk da bak'ace Wallahi umma tana da bala'in kyau sekin kalli hancinta da qwayar idonta dayake Nan kaman na mage zaki tabbatar da hakan"

*D'aya B'angaren*

Mikewa Bashama tayi cikin bala'in tashi hankali "Hanisa wallahi tunda na rasa Arab to Wallahi D'aya bayan d'aya dukk'an su sesun rasa shi abin takaici ya rasa wacce ma ze aura se yar cikinsa a I'na ya auro ta ma" "Wallahi umma ban sani ba Amma karki damu a hankali dan binciko Miki" Sallama sukayi tare da kashe wayar,

Rayuwata a kaduna wani i'rin rayuwana da zance Alhamdulillah domin Ummin halima tana girmama lamarina uwace na gaban kwatance Wanda ta tsaya a gidanta makarantar su Halima wacce ta nace da se munyi qwance aka sakani zamu tafi takwas Se karfe D'aya zamu dawo muna yi sallah zamuyi wanka muyi shirin islamiya Wanda yake mallakin Ummi ne tsakanin makarantar da Gidanta babu nisa sosai sannu a hankali lokaci ke tafiya har na shafe tsawon shekara biyu a gidanta na mayar da hankali sosai a kan karatuna ban cika magana sosai da mutane ba cikin Kankanin lokaci Allah ya d'aukaka al'amura na kowa son qwance yake dani Sabida kokari na, Amma basa gabana domin Wallahi Halima kad'ai da Hanisa sun isheni kokarina da qwanzo na yasa malaman makaranta ke bala'in Sona Aure kan na watsar dashi domin Daman ban d'aukeshi da wani mahimmanci ba rayuwana nake cikin qwanciyar hankali yau a matukar gajiye nake hakane yasa driver na sauke mu na shiga Gida da sauri na fad'a d'akinmu kasancewar inna fashin sallah yasa nayi wanka tare da fad'awa saman gado Hanisa da shigowarsu kenan tace "kai Jiddah yau Kuma barci ne" ya mutsa fiska nayi tare da juyawa mata baya domin bana jin yin magana tsaki tayi domin wannan halin nawa na bala'in bata haushi Sabida in na Mata i'rin Haka seta fita sabgata ni kuwa ban damuwa , I'nama nake sanin na b'ata mata rai Halima ne de dake bata da hakuri Nan zata hauni da masifa takan ce. "Gaskiya jiddo banson iskanci da shariya ya inna Miki magana zaki bawa iska ajiyata?"

"Kiyi hakuri" iya abinda nake ce Mata kenan, duk da haka be Mata se tayi kananun surutai i'ta

bata son wannan halin nawa na fiya miskilanci wani lokaci se Ummi ta daka mata tsawa take hakura da mitan,

A hankali nake kirga kwanakina har na shiga kirga mako har na koma wata ayau nake lissafin shekarata Hud'u a Gidan ya kasance inna da sha takwas kenan mun kammala sakandiri lafiya sakamako yayi kyau Dan murna har azumi nayi domin duk nafisu Makin me kyau, a so biyu Arab ya tab'a zuwa tsakanina dashi gaisuwa dan nama manta da matsayinsa gurina. Zaman wata uku mukayi kafin Ummi ta samo Mana wani makaranta ban tab'a tsintar kaina cikin damuwa da bak'in cikiba seda ta shilar shigata jami'a domin seda na gwammace da banyi karatu ba a rayuwata nayi kuka Kuma har gobe inna kuka domin abinda nayi ban tab'a tunani ze shafi ahalina ba, tunda na had'u da Arab nake kuka Kuma har yanzun kuka nake.

Cikin doki da murna muka fara zuwa makaranta a gida kuwa Ummi ta dage sosai gurin koya Mana girke girke yau da huri muka muka fito inna zaune nida Halima Hanisa muke jira Halima ce ta mike tare da fad'in "Kinga bari na duba abu a library inna zuwa" hankalina na kan karatun da nake nace Mata "toh" batare da na d'ago ba, wata Yarinyar dake nesa dasu tana ganin tabar gurin ta karaso muga desk din tayi "Hi Jidda Usama" d'agowa nayi domin sarai nasan muryanta tun shigowata take bibiyata ta nace min yanda kuka San cingon, murmushi tamin Tami nima na mayar Mata roban yogurt  biyu ta ajiye tare da tura d'ayan gabana "bisimillah" Girgiza Mata Kai nayi domin kawa kawai naji zuciyata ta kasa nutsuwa da i'ta marerece min tayi ni kuwa naki karshe mikewa nayi tare da kashe littafaina nace "Aliya nagode azumi nake" juyawa nayi na bar gurin tab'a Bluetooth din dake makale da kunninta tayi "kunde ji Wallahi taki Sha dan Allah zan gwada  in tasan wata bata San wata ba"

Cikin tsananin b'acin rai ta ture Yogurt din tare da barin gurin daman ba tafiya nayi ba duk abinda ta fad'a inna jinta d'aura hannu nayi akai tare da sallati Nan da nan hawaye ya cika idona wake bibiyar rayuwata ne? Banida me bani wannan amsar cikin tashin hankali na fara kokarin tafiya ji nayi an dafa kafad'a na da sauri na juya Hanisa tace "Jiddah lafiya na ganki ke d'aya me kike anan? Halima fa" cikin rawan murya nace "Taje duba abu ke muke jira tun d'azu" Hanisa tace "Amma meke damunki naji muryanki haka?" Girgiza Mata Kai nayi, "bakomai"

Karasowan Halima yasa muka tafi Gida tun daga wannan lokacin na rasa walwalata Hanisa tayi tambayar duniya naki fad'a mata Halima ma tayi mita har ta gaji tabari wasu i'rin mugayen mafarkai nake sosai na dage da addu'a saraka da azumi duka inna yi domin sakada maganin masifa, a hankali na fara wani i'rin rama , Daman nagi na gwanar Kib'a ba, Nan da Nan na zabge .. Ummi de ta zuba min ido bata tambaye ni ba domin ta lura inna da mugum zurfin ciki..

_Banyi Alkawarin Typing kullun ba Amma isha Allahu na dawo zaku ringa jina inna samu lokaci Nagode_

https://chat.whatsapp.com/HsMb0FG2FMMFCBLoDfHoyQ

Ga link Dan Allah idan kinsan ba karantawa zakiyi ba karki shiga, in kinsan bazakiyi comment ba karki shiga!

*Maman Faruq*
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: *♡SIRRIN ƊAUKAKA♡*

_Wattpad@ayshajb_

®🌁

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION..📚📚*

7..
Tunda nayi sallar subayi na koma azkhar dinma da kyar nayi domin wani i'rin mugum kasala nake ji, kwanciya nayi Hanisa da Halima sun fita domin al'adace da zaran mun idar da sallah zamu fita munyi shara mu gyara gidan duk da akwai masuyi Ummi bata sangartamu ba, aiki muke sosai domin nike girki Sabida bala'in kaunar abinci na mayar da hankali sosai gurin karance karance littafan girki ban b'ata lokaci gurin karatun novels, kamar yanda na maida hankalina gurin, Girki Hanisa kuwa gwanace gurin had'a turaruka masu kyau da khamshi Tawa Halimat an barta gurin zanen lalle da kitso,

"Masha Allah yan Mata na sannunku ubangiji ya baku mazajen Auren nagartattu Wanda zasu rike mu ku, rabbi ya maku mazan da zasu d'aukaka daraja da martaban ku, inna Hauwa?" Ta karashe maganar tana tambayar su, murmushi sukayi dukk'an su, cikin jin dad'in addu'ar ummi Hanisa tace "Ameen Ummin mu, Jiddah bata jin dad'i tana kwance d'aki" Halima ta karb'i zancen da fad'in "ummi bansan abinda ke damunta ba, ko magana bata son yi"

"Subhanalillahi bari na dubata"

Hanyar d'akinsu tayi,

"Wallahi duk se naji wani iri in-law, ba lafiya" cewar Hanisa kamar zata fashe da kuka Haka tayi maganar..

Ajiye wukar da take yanka lawashin albasa Halima tayi "bari kawai nima karfin Hali nakeyi Amma na damu da sahiba sosai" cikin mutuwar jiki suke aikin tare da jin ba dad'i rashin kasancewarta tare dasu ..

Damuwar da take ciki be hanata yin Sallama ba domin haka kawai take jin kaunar yarinyar sosai inna kwance zazzab'i nake ji a hankali na amsar Mata sallamar zama tayi a gadon tare da kama hannuna "ummi.." na Kira sunanta tare da fisar da iska , wani zafi ne, yake fita a bakina.
"Sannu Hauwa Allah ya kara miki lafiya shine bazaki sanar min ba? Me yasa kike barin damuwa a ranki ni amatsayin 'Ya na d'aukeki keda Halima baku da banbanci gurina Amma naga yanda na d'aukeki ba haka kika d'auke ni ba."

"Ummi.." kukan da take dannewa tun d'azun ne ya kwace mata a hankali na matso jikinta tare da kwantar da kaina saman kafad'arta wani i'rin kuka nake Wanda banson ma'anarsa ba, nasan inna kewar iyayena sosai inna cikin maraici da kad'aici “waya tab'amin  shaleleNah? (A duk lokacin da take son rarrashi na  wannan sunnan  take kirana dashi), Hanisa ce ko Halima? Fad'amin kinji Shalele.." wani i'rin murmushi nayi tare da sauk'an hawaye runtsa ido tayi domin duk na b'ata Mata jikin Himar d'inta (Wai dan Allah ke yar Borno ce yawanci haka kike ambatar Sunan  Hijjab wanda suma yan Borno Haka suke Kira jama'a na yawan min wannan tambayar,)

"Ummina basu bane bansu bane! 'Yan uwana basu min komai ba, hasalima sun damu da damuwata ummi zuciyata zafi take min, bugawa takeyi banajin dad'in komai bana ganin komai da haske ya zanyi ne Ummi?" Na fad'i Haka inna kara fashewa da sabon kuka, "kiyi hakuri ki ringa addu'a ki dena biyewa shed'an da rud'in zuciya ki ringa nutsuwa kina ibadarki kinji sannan ki yawaita sadaka domin babban maganice kina da ilimi kina da sani Amma meyasa kike barin shed'an la'ananne yake galaba akan ki? Haba Shalele" ajiyan zuciya na shiga saukewa sakamakon shafa kaina da take rik'e d'ayar hannunta nayi sosai "insha Allahu Ummi zan ringa kokari"
  "Yauwa Yar albarka bari na Kira likita ya dubaminke.." da sauri nace.
"A'a nasha magani ummi zanji sauki"
Batason jayayya dole yasa ta kyale ni tea ta had'amin da kyar nasha ta Kuma bani magani Daman bansha ba kawai bana so ta Kira likita ne.

Kamar kwai haka take lallab'ani wunin ranar ta bani kulawa domin ko makaranta bata je ba, ganin haka yasa suma sukace bazasu jeba, seda ta tsawatar musu suka tafi kwana biyar inna kwance Alhamdulillah nayi dama domin inna tayasu da wani aikin, kasancewar lahadi ne yasa da yamma Ummi tace in shirya zamuje sayayya haka muka shirya dukkansu Suna zumud'i Banda ni da nake jin zuciyata babu dad'i, i'ta take Jan motar har muka iso wani babban shago duk muka fito mun faka motar mu gaban wani had'add'en bakar Jeep shiga mukayi a hankali muka fara shagayewa kowa na daukar abinda yake so Banda ni, da duk nake jin wani i'rin sanyi na shiga jikina gaba nayi da kwanton hannuna na fara d'iban kananun kaya brezia pants da riga shimi da shomshort haka kawai na tsinci kaina da d'ibansu duk da ni ba ma'abociyar saka su bane, musamman ma bran, domin nonuwana Tasa ne (irin nonuwan da suke Nan cur d'as suke Zaune a qirji daga kasa akwai fad'i sun baje Amma nipples d'insu a cure yake a tsakiya nonuwa Wanda ko yara goma aka shayar sunanan da k'yansu basa zubewa) murmushi kawai nake zabgawa wanda rabon da inyi har na manta, shigowarshi kenan ta tasa shi gaba tana mishi surutu shi kuwa bema san tana yi ba, kaya yake d'iba mata wayarta da aka kirane yasa ta yin shuru tare da matsawa gefe tana amsa wayar na gama d'iban kayana juyawar da zanyi cikin rashi sa'a na bangaje mutum tsantsine ya d'ib'eni duk kayana sun tsarwatse cikin zafin nama ya finciko hannunta tare da rumgumeta a faffad'an qirjinsa wani i'rin ajiyan zuciya suke sauke tare, Kara matseta yayi sosai qirjinta na gugan nashi zuciyarta wani i'rin bugawa yake Wanda yasa yake jin nonuwanta sosai a jikinshi wani i'rin juyi yayi da hannuwanshi a kuqunta , yarrr tsigan jikinta ya tashi a hankali ta bud'e idanuwanta masu kama dana mage gata da mik'akk'un gashin ido masu tsawo kurawa juna ido sukayi wani i'rin kallo yake mata wani i'rin matsiyacin gudu matashiyar budurwan tayi har tana wani sufa tsaban kishi wata take kallo jikin abin sonta Wanda ko da wasa be tab'a kwatanta mata kallon da yake mata ba, inba gizo idonta ke Mata

ba, kad'an ya rage bakunansu be had'u Dana juna ba.

Jin ihuta ya ankarar dani da sauri na kwanci kaina cikin rashin kuzari nace "kayi hakuri dan Allah ban lura da Kai bane" shuru yayi bece min komai ba kayana na kwashe "dakata zan Miki kashedi Nabil nawa ne ni kad'ai dan ni Akayi shi shegiya me idon kuliya, kin wani manne mishi kina mishi kallon karuwai to Mijina yafi karfin ki.." murmushi kawai nayi domin sarai kishi ke d'awainiya da i'ta Amma kalamanta sunfi zafi tafiyata nayi Nan ta shiga mishi masifa kala yanda kuka San dutse haka ya mayar da i'ta siyayyar da basuyi ba kenan ,

Na samesu tsaye ni suke jira a hankali na Mika kayana aka saka min a leda Ummi ta biya muka nufi mota waigawar da zeyi ya yanga tana kokarin shiga mota kamar wacce akace in juya ai kuwa mukayi ido hud'u wani i'rin had'add'en murmushi ya sakar min Sunkuyar da Kai nayi tare da shigewa motan, Nan Halimatu ta hau mita "haba sahiba duk kin shanyamu wai inna kika tsaya naga ba kayan arziki kika d'iba ba?" Murmushi kawai nayi "ban son isk'anci ya inna Miki magana kin min banza!"

"Toh uwar masarasa hakuri kin cika Mana kunni " cewar Hanisa cikin zolaya tayi maganar harara ta mata sanin bazatayi magana bane yasa nace. "in-law bana so fa babu wandan ya kai sadiyata hakuri bana so fa!" Cikin marerecewa nayi maganar inna kallon Halima tare da bata hakuri da ido juyar da kanta tayi jikin glass tana kallon titi hannunta na rike domin sarai fushi take dani "Ummi ki taya ni bada hakuri dan Allah Hali dubu tayi fushi" _banzaye kawai_ cewar Hanisa cikin zuciyarta. "Yi hakuri to Halimatutu" dole yasa ta murmusa domin cikin zolaya ummi tayi maganar.

Haka muka karaso gida muka baje a falo Yahgana ta kawo Mana abinci tare da Mana sanda zuwa kowa ya bud'e kayanshi Amma ni na kasa domin Wallahi kunyar Ummi nake ji, "muga kayanki Jiddah cewar Hanisa" zubur na mike na shige d'aki batare da na d'auki kayan ba kai hannu tayi zata bud'e kayan Halima tace. "Kinga karki bud'e mata kaya" harara ta watsa mata tare da jawo ledar tana shirin bud'ewa Ummi tayi murmushi. "Barshi Hanisa" badon ranta yaso ba tabar kayan, "Kuje kuyi haraman sallah domin magrib ta gabato."

D'aki sukayo lokacin na fito daga band'aki bayan nayi alwala sallaya na shimfid'a "ki gama wallahi sekin bud'e na gani" murmushi na sakar mata, Halima tace "dake mayyace Wallahi zaki cinye mutum har kashi! Nacin ki yafi na kowa"

"Oho de sena gani"

*Maman Faruq*
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: *♡SIRRIN ƊAUKAKA♡*

_Wattpad@ayshajb_

®🌁

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION..📚📚*

......8

Ganin har yanzun ta kasa Dena cika mishi kunnin da shirmenta ne yasa shi taka motar sheda ta saki wani i'rin kara dafe qirjinta tayi tana sauke numfashi a kai$^2$ faka motar yayi tare da juyowa Gareta "Zaifi kyau in naji Duka" wani i'rin kukan takaici ta saka mishi cikin shagwab'a wanda da zaran tayi take samun zuciyarshi domin shi mutum ne da yake son mace ta ringa zuba mishi shagwab'a qura Mata ido yayi Yana kallon yanda take mishi kuka harda buga kujeran da take Zaune "abinda Zaka cemin kenan haba Qalbi ka rumgume mace wacce ni matar auren ka baka tab'a min i'rin wannan rumgumar ba!" Kuka taci gaba dayi zuciyarta na kara hasko mata yanda ya manna Jiddah a qirjinsa Girgiza Kai kawai yayi tare da jan motar ko kulata beyi ba, kwantowa tayi jikinshi sosai tana mishi wani abubuwa ranahi ne ya kara b'aci. "Ya isa Haka! ki bari mukarasa masaukin mu" shareshi tayi dakyar da temakon Allah suka nufi Gidan da Makarantar suka bashi domin malamin jami'a ne , Suna shiga falo ya fara cire Kayan jikin jawota tare da hurgi da mayafin ta zip din rigarta na ja, seda ya Mata tunbur kafin ya man nata da bangon falon runtsa ido tayi jikinta na rawa domin har yau tsoro take ji Aure shekara biyu ta kasa sabawa da yanayin sa i'ta de a barta da i'ya Roma's tafi sonshi da samu nutsuwa ta B'angaren Amma da zaran aje fagen Auratayya minti kad'an zata fara kokarin janyewa dan ba karamin wahala take sha ba, had'e bakinsu yayi cike da mugumta yake tsotsar labb'anta hannunshi D'aya ya tallafi bayanta d'ayar Kuma yana matse albarkan qirjinta ..

Wani i'rin numfashi take sauke ajere hannuwanta ta d'ora a kuqunshi tana juyashi a hankali yajata suka kwanta saman doguwar kujera kanshi yasa a qirjinta Yana lasan tsakiyar su "Ashhh" abinda ta iya cewa kenan ta lallib'o bakinshi tana tsotsa a hankali hannunta na Boms dinshi tana matsawa lumshe ido yayi, kafin ya bud'e ya janye daga jikinta .

Zama yayi tare da rik'e Bindinsa "oya zuki Yi sucking.." da sauri ta Girgiza mishi kai , dama seda ya fad'a hakan a ranshi da karfi ya jawota "se kin tsotse baze yiwu kullun ki ringa jin dad'i ni bana ji ba"

"Wallahi bazanyi ba.."

"Zakiyi nace.!"

Da karfi ya danna kanta kwancewa tayi tana kakarin amai dogon tsaki yaja kafin ya ware kafarshi d'aukanta yayi ya d'ora samanshi.

"Wayyo Zafi"

Zungura Mata yayi da karfi ta sake fad'in. "Zan mutu Nabil har wiyana nake jinshi dan Allah ka barni na kasa sabawa da kayanka.."

Kara rik'e Kuqunta yayi Yana tura mata sosai "Ashh Zafi"

Matse d'uwas dinta yayi kafin ya bud'e idonshi ..

"Haka naji lokacin da kika zage ta"

Hannunta ta zuba duka a winyan shi tare da fashewa da kuka.

"Nagaji wallahi"

"Nima nagaji da Auren ki tunda Baki gamsar dani"

"Wayyo marana Nabil dan Allah"

Kokarin kwacewa take domin ba karamin cin ubanta yake ba, riketa yayi sosai.

"Mintina biyu kawai nayi yi hakuri Na fitar"

Da karfi ta kwaci kanta tayi hanyar d'akin data gani da gudu bin bayanta yayi da kallo zuciyar shi na mishi zafi har yau besan dad'in Aure ba, daya bijiro mata da bukatarshi bata yarda ya samu gamsuwa da i'ta Kuma a hakan take ihu da kururuwan tana sonshi da kishin sa. Kwanciya yayi jikin kujeran tare da kama Abinsa Yana shafawa hakurin Yana daf.

Tunawa da i'ta yayi tana sayye da dogon himar lokacin da yake shirin d'aukarwa Kayan kwalliya ta taka Himar dinta ya tad'eta cikin rashin sani ta bigeshi tayi baya zata fad'i bayan kwandon dake hannunsu kayan ciki ya watse tallafota tare da rumgumota jikinshi yayi har yanzun Yana jin tudun nonuwanta jikinshi wani i'rin murmushi yayi tare da shafa kanshi Yana tuna lokacin da take kwashe kayan ta cikin sauri a kunyace duk da bata cikin nutsuwar Amma a nutse cikin sanyi take komanta "inna Sonta" de-den fitowarta bayan tayi wanka kunninta yaji Mata wannan kalmar "Nabil?" Bud'e idonshi yayi akan ta "Eh inna sonta kuma zan aureta.."

"Nashiga uku Nabil Dan Allah karka fasa min zuciya Wallahi inna sonka"

"Haka Kuma zaki barni dan Wallahi bazan iya zama dake ba"

"Wayyo Allah Nabil Zaka kashe ni yanzun bakaji kunyata ba, Wallahi baka isa ba"

Tsaki yaja sannan ya tashi domin haukar banza take bin bayanshi ta farayi tana surutai "Kariya kike baki sona Nuwairah tunda na Aure ki cikakken minti biyar ban tab'ayi a kanki ba na gaji Wallahi inna bukatar wacce zata d'auki d'awainiyata"

"Wallahi da Raina bazaka Auri wata mace ba!"

Banko kofa yayi Wanda saura kad'an a fiskarta ihu tasa Nan ta shiga wargaja kayan falon Yana jinta tana haukarta har gama shiryawa ya fito, kallon falon yayi a tsawace yace. "Tashi

mahaukaciya Kuma na rantse da Allah kafin na kirga biyar ki gyara gurin Nan" yanda yayi maganar ne yasa ta mike ta fara gyara gurin tana kananan surutai sanin ba girkin zatayi ba yasashi shiga kichin.
***
Tasowar mu kenan daga islamiya wanda yake kasar Gidanmu dukanmu uku Himar dinmu har kasa ko wacce na rataye da jakar littafan ta.
Haka muka karaso Gida ban lura dashi ba nayi jikin Ummi na kwanta tare da shafa cikina "Ummina yunwa nake ji Kuma girkin ki" shafa kaina tayi "to shalele jeki watsa ruwa tukun" D'aki naje na baje a gado "washh dan Allah na gaji Wallahi" make ni Hanisa tayi a cinya "aikin uwar me kikayi" dariya na mata juyawa nayi na kalli Halimatu tana nan rik'e da wayar Hanisa domin i'ta kad'ai keda waya duk da mun mallakin hankali da nutsuwar mu, Ummi taki bari mu karb'i waya to nida bani tsayawa da samari Halima kan in har muka fita se ta samo saurayi domin i'ta me jama'a ce ga surutu da barkwanci ba ruwanta shiyasa ake sonta ta iya kwashe kwashe "Hali dubu wani Gara kika samo?" Nayi maganar bayan na mike inna kokarin cire Kayan jikina "Hmm bari sahiba wani labari nake karantawa" tsayawa nayi inna kallonta da kyau, in ba gizo idona kemin ba kamar harda matse kafa Halima keyi shammatar ta nayi na kwace wayar inna kallo "inna lillahi Halimatu yanzun meye amfanin haka, isk'anci fa kike karantawa Dan Allah ki kame kanki karki karar da ruwan jikin ki a banza, kiyiwa Mijinki tanadi Wallahi banso.." fisge wayar tayi "dalla barni malama tanadi kan inna yinsa,"

"Wallahi sena fad'awa Ummi" da sauri ta ajiye wayar "Yi hakuri sahiba na bari" ta fad'i Haka tana marerecewa duk da inna karance karance Wallahi nasan me nake karantawa , wanka na shiga koda na fito basa Dakin.

"Sawdat yarinyar ki ta girma.." katseshi tayi da sauri "ba maganar yarinyata muke ba, kace zaka Umura da iyanmu?"

Sosa kanshi yayi "Eh Amma ba yanzun ba.."

"Tashi ka tafi inna da aiki"
Marerecewa yayi "dan Allah anan zan kwana.." ai bata ji karshen maganarshi ba tace "Kariya ne daga Nan zuwa Abuja ba nisa tafi gurin gwala gwalan kan, 'Yata bata da daraja ko ka manta Kai da bak'in ka kace ,baka da muhallinta?"

Zeyi magana ta kashe shi "Nagama magana Araba!"

Fita yayi mikewa tayi tare da kwashe kayan da yakawo min a d'akinta ta ajiye,

Fitowa nayi na samesu Suna wanki bance musu komai ba, na nufi kichin abincin dare na d'ora Yahgana na tayani Ummi ce ta leko tare da fad'in "kisa da yawa" Gyad'a mata Kai nayi, muna hira da Yahgana har na kammala tuwon semo da miyar obono ,

Fita nayi a kichin din nace ta Gyara inda muka b'ata domin ana Kiran sallar magariba "Ban gaya Miki ba Cingon d'inki tace a gaisheki" cewar Halima zip din rigana naja tare da cirewa "wacce

kenan?"

"Aliya Mana" murmushi nayi "Tom nagode ki gaisheta"

Wanka na shiga a gurguje domin kaurin girki nake inna Fitowa na tarar Uwar iya, ta shimfid'a min sallaya Hanisa kallonta nayi "nagode Tawa" A nutse na fara gaida Ubangiji na, inna karanto mishi damuwata bayan na masa kirari da sunayenshi tsarkaka inna kuka cikin sujjadata nake rokonsa ya yaye min damuwata Ya Kuma kai haske da rahama kabarin iyayena addu'ata na karshe Shine Allah ya bani miji nagari nagartacce , seda nayi isha na zauna "Dan Allah ustaziya ke muke jira yunwa muke ji" cewar Halima tana hararan Gefe mikewa nayi na kawo shafa'i kaman zata fasa ihu domin Wallahi na iya dad'ewa a sallah inna sallamewa ta hau mita katse nayi "Kinga karki cikani da hayaniya in baraki iya jirana ba, jeki inna dalili? Kayi sallah Bazar Bazar? Kana assalamu alaikum shikenan kayi shi cikin nutsuwama ji kake kaman Badede ba, barni nayi komai na cikin hankali banson gaggawa"

Hanisa tace. "Maganarki Gaskiya ne in-law"

Falo muka je Ummi ma bata fito ba, abincin na zuba Mana muna cikin ci ta fito cikin Santi Halima tace "Gaskiya sahiba hannunki da zaki ji nake kunni na kaman ze tsinke" ta fad'i Haka tana shan kunun aya, "Akwai bikin da za'ayi kasan anguwarnan Gidan Alhj Sabo Hauwa ko zaki amshi kwangilar girkin?" Tunda ta ambaci sunana nasan da gaske take maganar murmushi nayi cikin jin dad'i nace. "insha allahu Ummi" da sauri Hanisa ta kalleta zuciyarta na Mata d'aci wai gata ummi Bazata bata ba, Amma ta bawa wata bare banza Hmm,

"Wayyo dad'i Sahiba Allah ya Sanya albarka ubangiji ya dafa Miki Allah yasa su baki kudi da yawa ki sai Mana waya" ta karasa maganar tare da kallon Ummi domin da gaske waya take so nima kallon Ummi d'in nayi.

"Halimatu" sunkuyar da kai tayi tare da fad'in "Na'am ummi" Tsam Hanisa ta mike dakatar da i'ta ummi tayi "dawo ki zauna"

"Ummi zangawa zanyi"

"Shi kenan" tafiya tayi, tana shiga d'aki ta shige band'aki fanfo ta kunna akanta tare da fashewa da kukan bak'in ciki "meyasa komai ta fini? Ta fini ilimi ta fini iya girki gashi har Ummi na bata darajan da ni da nake 'yar kaninta bata bani ba meyasa!" Kuka take sosai,

"Halima ki fita idona na rufe"

"Dan Allah Ummi kiyi hakuri" a raunane tayi maganar

Sassauto da murya Ummi tayi "Wallahi inna tsoron lalacewar tarbiyan ku shiyasa bana so ku kulla alaka da waya, inna tsoron Allah inna tsoron Halinki , kinada rawan Kai, Jiddah ta fiki nutsuwa maitarki kike nuna kina son waya Halima in lokacin rik'e waya yayi zaki rik'e idan kinyi

hakuri dan Allah karatu nake so kuyi ba waya nake so ku rik'e ba, ku kame kanku jami'a kuke banda kwashe kwashen kawaye da samari , na turaku karatu ne, ba k'awance da kula maza ba, kuji tsoro Allah ku tsare min kimata amatsayina Na UWA duk abinda ya sameku dani za'ayi kuka bakina za'a gani dan Allah ku mayar da hankali"

"Toh Amma ummi meyasa Aka bar Hanisa da waya?"

"Ban isa bane babu yanda banyi ba, na Hana Aminu yaki ji to me zance tunda nashi ne"

Nasiha ta Mana sosai jiki a sanyaye muka shiga d'aki Hanisa har tayi barci sauya kaya mukayi sannan muka kwanta.

Washe gari da hurin muka kammala aiyukan mu sannan aka sauke mu a makaranta Nan suka nufi nasu ajin kasancewar kowa da b'angarensa  inna shiga aji naji d'alibai Suna hiran an kawo sabon malami Mara mutumci domin fiskanshi daure yake baya dariya shuru nayi inna saurarorn hirarsu domin yanda nake ji Suna fad'a ya musu lectures na kwana biyu bayan bana Nan, "ai Amma Gayen nada kyau fa" cewar wata d'aliba me Suna Fadila Hassan Aliya tace. "Amma matar shi bata da mutumci Wallahi ranan kawai kallonshi nake kunji yanda take zagina" Dariya nayi "au daman kallon malamai da kyauwun su kuka Zo ba karatu ba? Allah ya shirya" Asiya Bashir tace "Wallahi jidda koke seya tafi da imaninki gayen karshene gurin Had'uwa.." banji sauran maganar ba nace. "Allah ya sauwake har yau ba'ayi namijin daze tafi da zuciyar Hauwa Usama Benue ba, babu shi Wallahi" haka suka karaci shirmensu can naji sunyi shuru hankalina nakan littafin dana bud'e ji nayi ance "Ke!" Cikin tsawa ban juyo ba domin na tsani ihu tab'a ni na kusa Dani tayi "wallahi kin shiga uku dan Allah ki tashi" tsaki naja tare da mikewa "Sir sunana Hauwa Usama Benue kana iya cewa  Jiddah ba ke ba, don kana malami bashi zai Hana in gyara maka ba, domin ba Dede bane ko sauran d'aliban zaka iya tambayar su, sunana" (kan uba lallai) kara tamke fiska yayi duk da yaji dad'in sake ganinta a karo na biyu be hanashi gwada mata halinsa ba, nan yace kowa ya bashi aikin daya sashi Nan naga kowa ta d'auko takarda tana something assmnt "Zoki fita min a aji mara kunya kawai"

Dariya D'aliban suka saka haka na fita jikina a sanyaye jikin bishiya naje na zauna tare da saka kaina tsakiyar cinyata kuka na saka sosai naji zafin Abinda yamin haka har ya gama musu lecture aka fito break Nan suka shiga nuna ni Suna min dariya sharesu nayi, bayan anyi azhar muka koma aji, a tak'aice wannan me fiskan saniyar seda yasa na rasa karatun shi na kwana uku domin Wallahi nayi bakin ciki sosai Sabida Yana da mahimmanci da nazo zan shiga aji zece. "Koma Gidan ku su koyar dake yanda ake ma babba magana shashsha kawai" fita nayi naje na zauna a waje ranan ban sake shiga aji ba, a hanyar komawar mu gidane na fashe da kuka juyin duniyar Nan Halima da Hanisa sunyi na fad'a musu damuwata naki, haka muka je, Gida washe gari kuwa cewa nayi Wallahi ban zuwa makarantar ,

Dakyar suka lallab'ani nabisu bakina d'auke da addu'a na doshi ajinmu Sallama nayi har kasa na tsunguna "inna kwana malam" amsawa yayi batare da ya juyo ba duk yan ajin sun zuba Mana ido Suna jira suga ya koreni Na d'auki tsayin minti shida kafin yace "jeki zauna" Alhamdulillah nace cikin zuciyata

"Nagode sosai Sir" tana mikewa yabi bayanta da kallo duk da cikin Himar take Amma seda shed'an ya raya mishi yanda mazaunanta suke motsawa , zama nayi wani i'rin aiki ya bamu acewarsu Yana da wahala Amma ni dake yar nacin karatu ce take naga be dameni ba, minti biyar yace Yana bukatar Something, Fadila takai mishi office d'insa Yana fita suka hau mita da kwashe mishi albarka, Nide shuru nayi inna rubutu haka Fadila ta tattara ta Kai mishi Yana Zaune Aka kwankwasa izini ya bayar tana shigowa be barta tace komai ba ya nuna Mata inda zata ajiye, fita tayi a hankali ya fara bin takardu Yana makin har yazo kan nata juya takardan yayi tare da nanata Sunan "Jiddah" murmushi ya sake Yana bin rubutunta da yayi mugum tafiya dashi cikin jin dad'i ya bata cikakkun Makin, Yana gama ya had'a takardun batare da ya d'auki nata ba, ya baiwa Aliya take ta raba lokacin naje sallah koda na dawo na manta da maganar takardan haka na dawo Gida.

https://chat.whatsapp.com/HsMb0FG2FMMFCBLoDfHoyQ

*Maman Faruq*
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: *♡SIRRIN ƊAUKAKA♡*

_Wattpad@ayshajb_

®🌁

*FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION..📚📚*

Free Book
Page9.
Bayan kwana biyu mun fito kenan muna Zaune bayan mun idar da sallar a zahar inna cikin duba jakata naga babu takardan da sauri na dakata inna tunani can na tuna ai ranan ban karb'a ba, mikewa nayi, "Ina zaki je da sauri haka?" Cewar Halima. "Zan karb'i littafina a office wancan malamin malam Nabil ko wa mantawa nake ma da sunanshi" dariya Hanisa tayi kafin tace "abokin fad'arki de, ranan nake ji ashe duk kukan da kike shi yake saki" batare da na tanka zancenta ba, na nufi office d'insa kwankwasa nayi daga ciki yace "Nuwairah tashi ki tafi" hararanshi tayi tare da Gyara zamanta jikinsa abinci ta kawo masa Amma dan tsaban rashin yarda taki komawa domin ta fara jin labari d'alibai na biyoshi Suna mishi tallar kansu shiyasa taci alwashin zama taga wacce shegiyar ce zata Zo, "Shigo" abinda yace kenan Yana kokarin sauke ta a jikinshi Amma taki sema kara k'ankameshi da tayi "Assalamu alaikum.." kaina na kasa maimakon a amsa sallar se naji tsaki da sauri nad'ago kaina wani i'rin kallo take jifana dashi bansan lokacin da na hurga Mata harara ba, domin na tuna i'ta taci mun mutumci a mall din da mukaje siyayya ran Nan, "Sir Littafina nazo d'auka" kasa kasa yake kallonta har yau shigarta d'aya sanye take da doguwar Himar har kasa , kafarta ne kawai kake iya hangowa cikin takalmi.
yarinyar akwai hankali da Nutsuwa Shi yasan abinda yake ji akanta, fita tayi ba tare da ta

biyewa Nuwairah dake mata zagin tsaman nama ba, domin haka kawai take jin ta tsani Jiddah duk da bata san wacece i'ta ba, zuciyarta ke daɗe ingizata..

"Jubin daka maida nutsuwarka kanta Allah inna raye babu macen data isa ta raɓeka.."

"NUWAIRAH!"  a kausashe ya kira sunanta wani irin malalacin kuka ta sakar mishi duka ta kaima qirjinta zuciyarta na Zafi. "Wallahi Nabil bazaka tozarta martabata ba, ashe da gaske suna biyoka wannan shegiyar daka rumgumace fa? taya me nake da har ka samu damar nan Bazai taɓa Yuwu waba, Wallahi!" da sauri ta mike tabar ofishinsa, hankalinta a bala'in tashe wani irin so take hangowa a qwayar idonsa ..

Ina fita na saka littafina cikin jakata tare da watsar da shirmenta gefe domin haukar banza take babu namijin da zanma haukar so da har zan bari masifar kishi ya rufe min ido naci mutumcin ƴar uwata, ashe a banza dana sani ma na tanka mata, inna zuwa na zauna tare da dafe kaina "Aliya kinga mahaukaciyar matarshi wata bogaja kaman ajebo bazar bazar ba nutsuwa Se kace Agir" in ji Fadilah kasa kasa suka sa dariya,

"Ɗalibai kusan me?" ido kawai suka zuba mata bata damu da amsarsu ba taci gaba da maganarta. "Wannan yarinyar ƴar iskace domin na kamata tana bibiyar mijina.." gwalalo ido sukayi waje nan kallo ya dawo kaina cikin wani irin jin kunya kaman kasa ta tsage na nutse na sunkuyar da kaina, "Bari kuga wani abin mamaki" wayarta ta cire ta shiga nuna musu hoton data ɗaukesu ranan a mall ɗin. wani irin kazamin kallo aliya take bin jiddah dashi, ciƙe da takaici , Kallon zan baki mamaki take mata, Miƙewa nayi da sauri zan bar gurin suka samin dariya "Amma anji kunya kullun kina nanuke da himar ashe ana can gefe ana cin mutumcinsa, turr da rayuwa irin taki"

Fadila tace "wallahi kuwa ashe de tantiriyace to anyi walkiya ta haska.." ban karasa jin maganarta ba na wuce da mugum sauri kuka na shirin kwace min biyoni Halima da hanisa sukayi suna kirana na tsaya amma Ina zuciyata wani irin zafi take min,

da sauri ya biyo bayanta nan yaga giftawar Hauwa inba kariya idonshi ke mishi ba kaman yaga hawaye fisƙanta komawa yayi tare da rufe ofishinsa.

Kafin ya dawo gurin kowa ya kama harkan gabansa Matarshi ma tayi tafiyarta, Gida ya biyota tana zaune ta ɗaura kafa ɗaya kan ɗaya tana jijjiga jiki ko sallama beyi ba ya shigo kaman wanda aka jefoshi "Mekika aikata?" wani kallon reni tabishi dashi tare da jan  tsaki. runtsa ido yayi jijiyar ƙanshi sun fito ruɗu ruɗu, miƙewa tayi tare da nufar hanyar ɗaki, wani irin jawota yayi tare da ɗaga hannu zan mareta a razane tace "N..i..ni? akan wata banza kake shirin taɓa lafiyata NABIL? Hmm ya maka kyau zaka iya sallamata kaje  kaci gaba da rayuwar daka zaɓarwa kanka amma ka sani kai namijine duk abinda kayi za'a maka" tana gama faɗar haka tayi shigewarta ɗaki, zubewa yayi a kasa ranshi na suya, yau da badon Nuwairah ƴar uwarshi bace renon Hajiya Latifa. da ba  abinda zai hanashi datse igiyar auren.

Nabil Abdallah shine cikakken sunansa matashi ne ɗan kimanin shekara talatin da huɗu,

Mahaifinsa Abdallah Shine konmishinen ƴan sanda a Chadi kasancewar su fulanin can ne, zuwa yanzun da girma yazo mishi ya ajiye mukamin yana kasuwancinsa , Abdallah su uku mahaifiyarsu Me suna Saddiqah ta haifa daga shi sai Hajara wanda suke kiranta HAJIH tana aure Achadi i'tace Mahaifiyar Nuwairah sai Autarsu Asma'u wanda ta auri wani manomi Aurenda seda akayi rigima sosai domin Saddiqah taki, tana gani kaman bazai iya riƙe mata autarta ba, gashi ba ɗan kasar bane ɗan Najeriya ne, Yashigo da kayane ya haɗu da i'ta tunda ya ganta yaji duniya sai Asma'u nan itama ta nace se shi badon ransu yaso ba suka bashi Aurenta da sharaɗin in ya tashi komawa kasarshi bada ita ba, sede ya ringa zuwa yana dawowa ya amsa musune kawai badon ranshi yaso ba, Alokacin matar Abdallah Mairo tana da cikin Nabil,

Shekara biyu da Auren Asma'u da Usama amma shuru ba labarin haihu inda suke zaune lafiya cikin rufin asiri domin bashi da arziki amma yana mata hidima dede karfinsa soyayya tarairaya duk wanda yazo gidansu rayuwarsu sha'awa yake basu, ada Abdallah be so Aurenta da Usama ba yana gani kaman baze iya riƙe mishi Autarsu ba, amma ganin yanda yake tattalinta yasa hankalinshi kwanciya wata biyar tsakani Allah ya sauki Mairo lafiya inda akayi shagali yaro yaci Suna Nabil tunda Asma'u taga Nabil taji duniya ba abinda take so kamarshi soyayyar duniya ta ɗora mishi.
Nan ta fara damuwa da rashin haihuwarta ganin lokaci na tafiya, sunje gurin likita ya tabbatar musu lafiya kalau lokacine kawai beyi ba, addu'a sukaci gaba dayi amma shuru seda aka kwashi shekara tara, lokacin Nabil yana da shekara bakwai tana tare dashi bayan shi mairo bata sake haihuwa ba, Hajih kan yaranta uku duk maza tana ta Addu'ar Allah ya bata mace domin Saddiqah tace yar cikin Gidan za'ayi inhar ta samu mace zata Aurawa Nabil, Mairo kan sede tayi dariya kwance tashi a saran me rai, kwatsan se gashi Allah ya bawa hajih ciki nan aka shiga addu'ar allah yasa mace zata haifa cikin ikon Ubangiji kuwa ta haifi mace inda taci suna Nuwairah yarinyar ta taso cikin wani irin gata uwa ba kwaɓa uba ba kwaɓa domin duk abinda ranta yake so shi ake mata, Ganin zasu bata tarbiyanta yasa mairo karɓanta amma a banza domin Nuwairah tari ta sangarce inda basu cika shiri da Nabil ba, domin sam yarinyar bata mishi ba, Asma'u takance mishi "Yarona kayi min Addu'a allah ya bani haihu" sai yayi murmushi yace. "Ammu insha Allahu zaki haihu mata zaki haifa min domin nafi so daga gareki uwa ta gari"
"insha Allahu Nabil zan haifa maka mata, sabida inhar akace Nuwairah ce Humm bazance komai ba amma yanda aka ɗora rayuwar yarinyar, zaiyi wiya ka iya zaman Aure da ita duk da nasan kanada hakuri amma watan wata ran, Nuwairah zata tunzuraka ka aikata abinda ba haka ba"
hawa , a nutse ta Gyara zaman cikin , tana maijin Farin ciki, Sai dai Jiddah kan sai yadda Hali yayi domin, Tayi dogon suma, Kwananta Biyar Ta farka bakinta d'auke da salati, Jumanace ke Zaune da i'ta sauri tace. "Sannu Aunti amariya" Murmushi ta sakar mata "Kwana na nawa kwance?" Jumana tace. "Wini shida kenan"

Tambayar data jefa mata yasa ta kallonta "Abbanku yazo?" Batace mata komai ba "Kinyi shuru"

"Hmmm" kawai Jumana tace mata tare da fita a d'akin Ofishin Nafisa taje suka tawo tare "Barka da arziki"  Sunkuyar da kai tayi

"Meke damunki Yanzun?" Ya tsina fuska tayi "inna jin marana yamin nauyi" Nafisa tace "Ya Danganta da cikin Jikinki ne ki kula sosai domin an fara kawo Hari" ta fad'a tana cire Karin Ruwan da sauri jidda ta kalleta "Maman Jamil Ciki Kuma?" Nafisa tace. "insha Allahu kuwa wata hud'u kenan" wani i'rin hawayen dad'ine Ya sauko fiskanta "Alhamdulillahi Allah kai mai kub'utarwa ne Ya Arrahimu yah maliku ya ƙuddusu Yah hayyu, Yah Kayyumu, Yah Allah kaman yadda ka kub'utar dani Allah ka kub'utar da abinda ke cikina lafiya Allah ka saukaka Al'amura na ubangiji ka karamin Hakuri juriya da Dangana.." wani i'rin tausayinta ne ke sake samun matsunguni cikin zuciyar Nafisa, "Ameen" Nafisa tace sannan ta riketa a hankali take tafiya har suka shiga Bayin wanka da wanke baki tayi sannan ta d'auro Alwala A zaune ta ringa jiro sallolin dake k'anta tanayi tana Hutawa , Bai zoba har ta cika kwana Goma Nafisa ta biya komai ta kula da lafiyarta sosai bata da abinda zata biya matar domin ta sota , tamkar d'iyar cikinta haka ta d'auketa Bata rik'eta kishiya ba, randa ta cika kwana Goma Sha biyu suka dawo Gida, Jumana ce ta Gyara mata shashinta Haka ta cigaba da Mika Al'amuranta ga Allah Bata wasa da Sallah sadaka, da taimakon Gajiyayyu Har ta shafe wata Uku Gidan bai leko inda take ba, Abin na damunta Amma ta barwa ranta ta mayar da komai ba komai ba, tana masa Girki kuma Yana ci , Ganinsa ne de batayi,

Seda cikinta ya shiga wata Bakwai Ran Nan da dare inna Zaune saman kujera domin Cikin kwanakin nan inna fama da yawan fad'uwan gaba da ciwon kai Gefe d'aya da ya sarƙafeni Hannuna rik'e da Hisnul-Muslim inna duba adduo'i kaman wani munafiki Haka ya shigo kallon tsaf na masa duk ya susuce Hasken ma ya dushe D'auke kanta tayi daga kallonsa Bai lura da cikin Jikinki, dayafara turowa ba ya zauna kusa da i'ta tare da d'aura kanshi saman kafad'arta.

"Yallaɓai sai yau aka sako min kai kenan?" ta fad'a tana shafa Kanshi daya Tara Gashi duk da shi ba ma'abocin tarawa bane, mamaki ne ya kamata sosai.. d'agowa yayi cikin Sanyin murya yace "Dan Allah dan Annabi kiyi hakuri"

"Ni? Me kamin da kake bani Hakuri?" Ta fad'a tana sakin murmushi tare da Jan Karan hancinsa. Wani i'rin sanyi jikinsa yayi Allah ne ya bashi Jiddah Amatsayin mata i'rinta ne matan da ake musu lakabi da mar'atu-Swahliha Yana kallonta ta d'auko abinda yake aske Gashi ta joya tare da ajiye kujerar Tsunguno Zama tayi ta aske mishi Tass tare da Gyara mishi fuska kallon kansa yayi a madubi tare da kallonta Kaman yayi kuka Haka yake ji kawaicinta yayi yawa.

Komawa kujera tayi ta zauna tana sauke Numfashi  tare da Rik'e Bayanta domin ya rik'e,  biyota

yayi tare da Zame Himar d'in da tun d'azun take sanye dashi Mutuwar Zaune yayi lokacin da idanunsa ya sauka , bisa cikinta “Hasbunallahu Yanzun kina da ciki shine ko ki sanar mu HAUWA?" Murmushi ta sakar masa “Tunda idanunka sun gane maka ai shike Nan."

Cikin wani i'rin Jin dad'i ya d'aura hannunshi saman cikinta Yana shafawa "Ubangiji ya raba lafiya Allah yasa ki Haifa min 'Yan biyu kaman yadda Halima ta Haifa" shekara d'aya kenan da haihuwar Halimatu ta haifi Aalik da Aaleen. Murmushi tayi Sannan ta kwanta cikin Kujera d'agota yayi "a a taso Yunwa nake ji wallahi..” dakyar ta Mike tana rik'e Baya a Haka cikin Daren ta d'aura Girki bata fito ba sai da ta kammala sannan ta had'a mishi saman tire a hankali take takowa har ta shigo d'akin a saman darduman carpet ta ajiye mishi Saukowa yai tare da Zama, Zuba mishi tayi zata mike yace "Zauna muci.." kawad da kanta tayi domin bata K'aunar Kallon shi bata ce mishi komai ba ta Mike ta Nufi Band'aki wanka tayi da ruwan sanyi tana zubawa jikinta tana sauke numfashi domin zafi take ji sosai tana Fitowa ta kunna Fankan dake fuskantar Gadonta ƙure gudunshi tayi sosai d'aure da zani ta kwanta tana jin yadda cikinta ke Juyawa.

Yana Kammalawa ya kwashe kayan hayewa yayi saman Gadon har Ga Allah Bata so ya tab'a jikinta daurewa kawai tayi harya nutse ga gajiyar da take fama dashi rik'e shi tayi sosai “Wai Allah bayana!" A hankali yake bi da i'ta “Banji yadda nake so Kiyi wani Abu Mana Wallahi ƙam kike Babu ruwa a Jikinki.." lumshe i'do tayi  hawaye na sauka mata har yanzun Yana jikinta Amma magana yake fad'a mata tana jinshi ya gama fad'anshi "Baki da dad'i Wallahi nifa na gaji bazan iya wannan rayuwar ba, ki binciki Jikin ki" sauka yayi a jikinta tare da mirginawa Gefe, kukan zuci take, i'ta lokacin da yake da lalularsa bata tab'a fad'a mishi wani magana ba, sai ma, damuwa data daurawa kanta, Ɗan Adam kenan mai wiyar Sha'ani tana ta kokarin mikewa domin taje ta tsarkake jikinta ta kasa i'ta bata i'ya kwanciya da najasa ba. "Temaka min na mike bayana ya rik'e.." tsaki yaja tare da Juyawa Yana Gyara kwanciyarshi "Magana nake maka Yallaɓai.."

"Dalla malama ki ƙyale ni haba! nagaji bazan i'ya wani temaka miki ba, aikin me kikayi da bayanki yake ciwo in Zaki tashi ma ki tashi" shuru tayi  tare da ƙurawa Bayanshi i'do i'ta bata son fad'a da masifa, Sunan Allah kawai take ambata domin zuciyarta zafi yake mata muddin tace Zatayi magana inna ga saiya kusan kifa mata mari, ranta ya Bala'i b'aci tsaki taja da karfi ta mike Zaune haureta yayi da kafa tare da mikewa Zaune "Ke har kin isa kimin tsaki Yar iska kawai" wani i'rin Kallo take jifanshi dashi mai cik'e da ma'anoni Da sauri ta Mike ta Nufi Band'aki jingina tayi da kofar ta fasa wani i'rin kuka mai tab'a zuciya Ya Zatayi ne? Wannan wacce i'rin jarabawa ce, wani i'rin rayuwa take fusk'anta haka.

"Allah Nagode maka Ubangiji ka karamin Hakuri da juriya!" Ta fad'a Haka tare da cire zanin jikinta a hankali take wanka tana kuka k'asa k'asa ..

Fitowa tayi ta sameshi har yayi barci sallaya ta shimfid'a ta hau nafiffilu Ranan ko barci batayi ba ta kwana saman Sallaya a lokacin da kowa ke barci i'ta Kuma tana kaima Allah kukanta Biyar da minta Goma ya farka tare da barin d'akin tana idar da  sallah ta Gyara d'akinta kichin ta shiga ta fara had'a mishi abun Kari tana Kammala komai ta wanke kwanunka da yaci abinci jiya da Wanda ta b'ata Gyara gurin tayi sannan ta jera mishi abincin a falonta wanka ta shiga tana

Fitowa ta fara jin Hayaniyar Fure da Zaina a falonta wadda rabon data ga d'ayansu  tun lokacin da abinnan ya faru , a gurguje ta shirya tare da saka Himar ta fito ta samesu Kan abincin data dafa mishi sunyi Kaca Kaca da Falon wani i'rin dogon tsaki taja a zuciye tayi Gurin. Allah ya gani tana Hakuri dasu, Halinsu ya i'sheta.

“in ma Mijina Girki kuzo har cikin falona ku cinye sannan ku b'ata min Gurin banson damuwa fa meyasa ku, kullun in baku tada husuma ba bakwa jin dad'i haba wani i'rin ibilis ne ke kanku?.." Fure ce ta mike tare da shaketa da Himar d'in, “Dan Ubanki waye iblis shegiya ke kika sai abincin?.." tureta Jiddah tayi tana haki ranta a b'ace tace. “Bade ubana ba, Wallahi.." fincike Himar d'in jikinta Fure tayi tare da Wurgi dashi "Au ni kike zagi Aiko zaki ci Kan uwarki Yau, daman ban tab'a shiga Jikinki ba" a razane Zaina ta mike ganin cikin jikin Jiddah ya girma “Na shiga uku ni Abu ke dan Ubanki daman cikin nan Bai fita ba, durun Uwa! aiku ki Haifa in gani.." tana fad'in Haka takaima cikin duka lilis suka mata Fure na dukanta Zaina na kaima cikinta Tun tana i'ya Kare Kanta Har ta kasa ta galabaita ga jini daya tsinke mata ganin Haka yasa suka fita da gudu Karo sukaci dashi Baya yayi Yana kallon yadda suka fito a hargitsa da sauri ko wacce tayi d'akinta Yana shigowa yace “innalillahi ke Meya had'aku suka Miki Haka, wai bana ce ki daina shiga sha'aninsu bane? Allah yasa nide karsu tab'a lafiyan abinda ke ciki.."

Cije baki tayi tana kuka abinda zaice mata kenan wato i'tace ma ta jawosu ma, Yana korin tab'a ta saiga Nafisa ta shigo da Gudu domin karaman Yar Zaina sajida a Kan idonta akayi komai shiyasa taje ta sanar mata “Kai...! Karka yarda ka tab'a ta azzalimi solob’iyo Kana cikin Gida kana ji Amma dake kana tsoron Zaina ka kasa komai kalli yadda take fitar da Jini Allah Yana nan Muazzan Allah baya barci" Durkusawa tayi ta Kama hannun Jiddah "Jumanah..!" Ta kwala mata Kira da sauri tazo ta kamata suka fita.

Binsu Yayi da motar shi tsaban ta galabaita ko idanunta Bata iya bud'ewa ‘Dakin taimakon Gaggawa  akayi da i'ta Kasa komai Nafisa tayi domin ta tsorata da lamarin sosai likitoci ne suka rufu a kanta Fitowa tayi tare da zama a kujeran Reception d'in Tafukan hannayenta tasa a fusk'anta tana kuka Yana tsaye Yana kallonta Hankalinshi a tashe wayarta ta d'auka tare da Kiran iyanmu ta sanar mata, kasa Kiran Ummi tayi sai sako data tura mata da Gmail d'inta Halimatu ta kira, ta sanar mata kashe wayarta tayi tana Zaune d'aya daga cikin likitocin ya fito, Mikewa tayi cikin rawan murya tace. “Dr Aliyu lafiya ya take..?" Dr Aliyu yace “Kai Dr Nafisa Gaskiya  ana zalunci Yanzun su waye kuka daki cikinta haka..?" Nafisa tace. "Sanin wannan lamarin sai Allah ni dai ya Lafiyar ta dana cikin?" Dr Aliyu yace "Za'a mata C's domin alamu sun nuna tun jiya take nakuda" tafiya yayi da sauri ya d'ibi kayan aiki Suna Tsaye gurin aka fito da i'ta tare da Nufar wani D'aki kimanin awa d'aya da rabi wata Nurse tazo ta kirata tana shiga d'akinta ta sameta kwance kaman Gawa kafin tayi magana wayarta yayi Kara.

"Kuna wani asibiti?" Cewar ummi da i'sowarta Kenan daga Kaduna Nafisa tace "Muna asibiti na Harkun karaso kenan" kashe wayar Ummi tayi sannan ta fad'awa iyanmu wadda kusan lokaci d'aya suka i'so "Barka da arziki An samu maza biyu mace d'aya sai dai biyu ba lafiya macen ta samu karaya sosai a jikinta namijin dai hannun d'aya ne ya karye sai na ukun Sabida mace ce farko ga yaran can" ya nuna mata inda aka sanyasu a kwalba, kallon gurin tayi taga su ƙananu Jiddah ta kalla tare da kallon shi tana jiran Karin bayani "Kwankwasonta ya Goce dole in d'inkin

ya warke
za'a kifata a mata aiki"

Fita tayi a d'akin.

Saida ta kwashe sati Uku a kwance kafin ta farka da dare, Sai dai Bata i'ya komai tana kwance Ummi na Gurinta da iyanmu ga Nafisa ma dake tsaye kanta , sai washe gari ta ganshi da sassafe ya shigo Ko kallon inda yake batayi ba, “Sannu Allah ya Kara lafiya" sanin ummi da Mahaifiyarshi na gurin ne yasa ta amsa domin bata so su fahimci halin da take ciki dashi , Bata samu Ganin yaran ba domin suna kwalba Dole sai sun cika adadin kwanakin ,

Alhamdulillah Bayan kwana Goma aka d'aurata Kan magani komai na tafiya dai-dai da taimakon Allah Dana Nafisa sai Ummi domin Iyanmu ta koma sai an kwana biyu zata dawo A hankali lafiya yake samuwa Har ta fara mikewa sai dai Bata mikewa duka Zuwa lokacin an Ciro mata yaran wadda tana ganinsu Allah ya d'ora mata masifar K'aunarsu tayi kuka sosai Ganin yadda saura suke ba lafiya, Macen taci Suna Sanah  Mazan  Kuma  Aakif da Aaki Bayan kwana Biyar Macen da da Aaki suka koma Ranan kaman zata mutu Dan kuka domin yaran sunki Kama nono Aakif ne kawai ke Sha seda aka kara Mata ruwa domin zazzab'i ya rufeta Ummi ke rarrashinta da nasihohi Tana samun karfin jiki suka dawo Gida Zaina da Fure ba wadda ya lek'o ta, makota nata shigowa Suna mata Barka, Zaina bakin ciki kaman ta mutu Ganin Jiddah na raye har da D'a , lallai da sauran Aiki gabanta , Ummi ce ke lura da lafiyarta dana Aakif duk da ba wankan jego take ba Amma tana Amfani da ruwan zafi sosai tsakaninta da Arab sai dai kallo domin  ko zai shekara Mata magana Bata kallon shi sai dai in ummi na Gurin ne take sakewa Suyi magana in Kuma Bata Nan sai dai ya d'auki 'Danshi in ya gama kallonshi ya tashi ya tafi Ta samu arziki sosai a haihuwar domin ta ko'ina samu take costumes d'inta sun mata alheri da makota shima yayi rawan Gani sai da ta samu wata Biyar Ummi ta koma Bayan ta mata nasihohi sosai domin tafahimci Yadda suke Zaune ba me shiga harkan wani, a hankali take Renon Yaronta  tare bashi kulawan daya dace Shekaran shi d'aya ya bar nono batare data yaye shi ba, bata fita tunda ta dawo,

A hankali take fuskanta yadda matan ubanshi suka tsane shi shiyasa bata barin shi ya fita sajida na shigo Mata jefi jefi, domin saita faki idon uwarta take zuwa, Ranan daya cika shekara biyu da wata Uku inna kichin inna girki na fara jin kukan shi domin na barshi kwance Yana barci D'aki na shigo Naga baya Nan da sauri na fita inna Kiran sunanshi “Aakif Aakif.." dakatawa nayi Ganin Zaina da bulala Yaron na ganin uwarshi da sauri yazo Yana makalewa bayanta “Yanzun me wannan yaron ya Miki da zaki mishi wannan dukan?" Ta fad'a hawaye na zubo Mata ganin i'rin dukan data mishi sai Ajiyan zuciya yake tsaki Zaina tayi sannan tace "ba duka ba wata rana saina kashe shi" tana fad'in Haka tabar Gurin jikina na rawa na d'auke shi inna kuka nayi d'akina dashi Wayata na d'auka tare da Kiran Abbanshi ba b'ata lokaci yazo,

Ya sameta Zaune ta tasa yaro gaba tana kuka Zama yayi tare da cewa "Meya Faru?" Tura mishi yaron nayi "Tsakani da Allah na gaji Yanzun wannan karamin Yaron ya chanchanchi Haka! Mena tsarewa Zaina meyasa ta tsaneni haka" tana kuka tana fad'a mishi yadda Zaina ta Zane mata yaro Gashi har yanzun yaki daina kuka, d'aukar shi yai ya kaishi d'akin Nafisa tana wanka

ya zauna jiranta , k'aurin Girki yasani mikewa da sauri domin na ma manta da inna girki saukewa nayi, na kashe gas din sannan na biyoshi d'akin. Na samesu tana dubashi Magani ta rubuta mishi “Ki ringa lura da lafiyan d'anki" Gyad'a Mata Kai nayi, sannan na d'auke shi na fita.

inna Zaune shuru shuru bai dawo ba na Miki na dawo falo Bayan na Goya Aakif dake kuka inna jijjigashi kiranshi nayi a waya, Yana d'auka yace “Kinga banson damuwa gani zuwa" kafin tayi magana ya kashe wayar sai Tara ya shigo Mata da maganin zuwa lokaci yaron yayi barci , Karb'a tayi batare da tace mishi komai ba ta nufi d'akinta ajiye magungunan tayi tare da shimfid'e yaron ta kwanta biyota yayi Bata hanashi abinda yake so ba,  Yana Gamawa ya mike Yana Jan tsaki, fita yayi i'tama taje tayi wanka halinshi sai shi,

Washe gari tana Zaune da safe Aakif na cinyarta har yanzun zazzab'i yaki barinsa Tana jin hayaniya na tashin cikin Gidan Amma taki Fitowa tana Zaune suka shigo shida Gimbiyar shi hotuna ya watsa mata “Shegiya karuwan banza" Zaina tace tana jifanta da Mugun kallo fiska k'unshe da murmushi kallon Hoton tayi taga i'tace da Sir Nabil, lokacin da suka fita da Ummi tayi tuntub'e ya tare ta sai d'ayar lokacin da suka fita da Yamma dashi maganarshi ne ya katseta “Nagode da abinda kika min Jiddah da Aurena kike cin amanata nagode kije nagaji Allah ya had'a kowa da rabonsa..." 'Dagowa nayi inna murmushi "Toh sai me inka sake ni? Ance maka zanji haushi ne ko Zan kurma ihu ne! Alhamdulillah Allah Nagode maka daka rabani da wannan Qangin Yah Allah sharrin Zina da ake bina dashi Ubangiji Allah ka yafe min Allah kasa su gane"

"Wake Miki sharri Bayan ga zahiri kece fa kwance jikin wani Kato da Aurena Amma kin cuce ni Allah ya i'sa!"

"Na sake ki saki uku ki fito ki barmin Gidana!"

Murmushi ta sake yi "insha Allahu Yanzun kuwa Mena tsinta a gidana banda bak'in ciki da masifu Allah Yana kallo zaluncin da kamin kaida matanka Allah baya barci seya saka min Wallahi bazan tab'a Yafewa Rayunkan 'Ya'yana biyu da nake jin K'aunarsu ba" Fita yayi a d'akin Takowa Zaina tayi Gabanta "Ya kika ga wasan? Nayi Cari up, abin wani sarkin Kuma gwara ki sake hawayen ki daina matsewa.."

Kallon sama da K'asa na mata “insha Allahu bazaki tab'a ganin Kukana ba, Duniyace Zainab ta i'shi kowa Riga da wando bare mu da muke cikinta Na barki da Allah na barki Kuma da fitowar Rana da fad'uwarsa Hakk'i na bazai tab'a barin ki ba" Kayanta ta had'a na sawa tare Dana Aakif dake Zaune Yana Kallon maman shi na kwashe kaya Tana Gamawa ta kashe duk wani kayan wutan d'akin tare da Goyashi, Fitowa tayi tana jan jaka zata fita ya kwance Goyan tare da karb'an Jakan kayanshi “d'a nawane bashi kika Zo ba, Zaki iya tafiya"

"Wannan ne Kuma baka i'sa ba Wallahi..! Ka bani d'ana" ta fad'a tare da Kai hannu zata karb'i yaron Mari ya kifa mata tare da Bawa Zaina yaron "Tashi ki barmin Gida 'Yar iska kawai.." janta yayi da jakar Kayanta har waje tare da Kullo kofar Falon wani i'rin kuka ta sake tare da buga kofar “Ka bani ‘DANA Ibrahim..!" Kuka take sosai Ganin yaki bud'ewa yasa ta shiga motar ta a guje tabar Gidan ikon Allah ne kawai ya kaita Kaduna Da karfi take danna horn ba shiri me Gadi

ya bud'e mata tun kafin ya gama bud'ewa ta danno hancin motarta da gudu ya matsa ko gama dai-daita tsayuwar motar batayi ba ta fito a guje tayi cikin Gidan, ummi na Zaune taga mutum ya fad'o tana shirin magana taga Jiddah ce “Ke Lafiyar ki kuwa?!" Zubewa tayi a kasa tare da Rik'e Ƙirjinta tana Jan numfashi da sauri Ummi tayi Kanta..

Maman Faruq
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: ♡SIRRIN ƊAUKAKA..!♡*

Farin Jini Writer's Association

Page22.

"Dan Allah kice ya bani Yarona Wallahi bazan iya barin shi cikin wannan Gidan ba, Ummi Yarona.."
Gyatsa mai had'e da Aman jini tayi cikin tashin hankali ummi ta qwalawa Yahgana Kira da sauri ta fito "Maza temaka mu kaita asibiti" Girgiza kai Jiddah tayi cikin fitar Hayyaci tace. "Aakif Ummi dan girman Allah.." zubewa tayi jikin ummi Numfashinta na shirin barin gangan jikinta, da sauri suka fita da i'ta motarta dake bud'e suka sakata A guje ummi ta figi motar Suna i'sa Emergency aka shiga da i'ta, sai lokaci ummi ta fara niman waya, Dole sai gurin nurse ta ara ta kira wayar iyanmu tana d'auka tace "Sawdat ce Iyata, Ga Jiddah tazo cikin mawiyacin Hali ki binciki Nafisat Meyafaru kar Yar mutane ta Mutu domin Aman jini take, Sunan 'Danta kawai take ambata Bansan Me Arab ya mata ba.."

"inna zuwa" kashewar tayi tare da Bawa Nurse sannan tayi Godiya.

Da kyar suka mata alluran barci domin surutai take musu tare da fisgewa tana son fita. "Kubarni ni lafiyata Lau, ku barni na d'auko Yarona!" Abinda take fad'a kenan idanunta na rufewa "wayyo Aakif d'ina bashi da lafiya Zane min yaro tayi Allah ya i'sa min wayyo Akif.." ruf idanunta ya Rufe tana sauke numfashi alamun alluran da suka mata yayi nasaran sata barci.

Likita na Fitowa ummi ta tare ta, ofishinta suka nufa tsaban tashin hankali ummi ta kasa zama duk da tace ta zauna. "Doctor bazan iya zama ba, fad'a min wani hali 'Yata take ciki? Meke faruwa da i'ta?" Rubutu likitan tayi sannan tace. "Ummin Halima zuciyarta ya kunbura sosai Jininta ya sake hawa fiye dana baya, tana b'oye Abu a zuciyarta dalilin dayasa yayi Haka kenan.." Hoton da'aka d'auki zuciyarta Doctor ta tura mata zubewa ummi tayi saman Kujera tana kallon yadda zuciyarta ya Kunbura "Allahuma ajirni fih musibati waa'akhlifni Khairan minhaa innalillahi wa'ilaihir rajioun! Yah Allah" Wani i'rin hawaye ne ya zubo mata "Dalilin tashin hankali yasa karamin cikin jikinta na wata biyu ya b'are.." runtsa ido Ummi tayi tare da fad'in "Hasbunallahu waa ni'imar wakeel"

Takardan da tayi Rubutu ta tura Mata.
"muna bukatar wa'yannan abubuwan Yanzun!" Mikewa ummi tayi ta fita da sauri Kuma ta dawo "Zuwa wani lokaci zata farka?"

"insha Allahu zuwa dare."

Gida Ummi ta koma tare da Yahgana wayarta ta d'auka ta kira Halimatu da Hanisa ta sanar musu Abubuwan da zata bukata ta d'auka tare da kud'i ta koma asibiti.

Washe gari
Sai biyun Rana alluran ya saketa mikewa tayi a zabure da karfe take son sauka daga Gadon Ummi dake sallah ba shiri ta yanke sallar tare da Rik'eta Yadda ta mike ne yasa jinin zubowa sosai Girgiza kai tayi tana cije leb'e jin yadda Maranta ke ƙullewa Halimatu ce ta shigo da kulan abinci Ganin Halin da jidda ke cikine yasa ta ajire Kulan da sauri ta karasa Hanisa dake Bayanta ne ta juya domin Kiran likita.

"Dan Allah ki nutsu Jiddah." Ummi tace tana sake riketa sosai Girgiza mata kai tayi "Taya zan nutsu Yarona na cikin mawiyacin Hali? Ki fad'a min Ummi taya zan samu kwanciyar Hankali yarona na gurin matar da tayi ikirarin saita kashe shi! wayasan me ta masa Yanzun, yaron da magana ma bai iya ba, Wallahi gwara da cikin Ya fita, wannan ai masifa ce Wallahi ki fad'awa Ibrahim ya bani Yarona in ba Haka ba, Kotuce zata rabumu, Ya dawo min da Yarona, Har mari na yayi dan zan d'auki Aakif. ki kalli yadda ya shimfid'amin hannunshi jikina, Wallahi Bazan bar musu d'ana ba ki fad'a mishi Ya bani Yarona kafin Hukuma ta shigo ciki.." magana take tana jijjiga kai tare da cije baki tana son ƙwacewa.

"Naji kiyi shuru Zai baki d'anki Meya had'aku?"

"Saki uku yamin"

Zaman dirshan ummi tayi a K'asa "innalillahi saki d'add'ai har uku?" Hannu Halimatu ta d'ora akai tare da buga salati Hanisa dake baya tace. "Amma Uncle yayi asara!"

Halimatu tace. "Babbama kuwa" daƙuwa ummi ta musu "Zanci Gidanku" shuru sukayi Ganin doctor ta shigo dubata tayi sannan tace "Ki daina motsi me karfi jikin ki, ba ƙwari fa"

Kallon baki San mai nakeji bane Jiddah ta mata sannan ta d'auke k'anta "Zansha ruwa" nace inna sakin numfashi me d'auke da Hawaye ni kad'ai nasan Abinda nake ji, a zuciyata Doctor tace. "Ruwan d'umi zaku bata" Hanisa ta d'iba a cofin fulask ta bani, Karb'a nayi nasha kad'an Ajiye nayi sannan na sauka a hankali na nufi Band'aki.

Sai Yamma Nafisa ta dawo Gidan nan ta Ga Aakif shi d'aya a falo hawaye ya bushe mishi a fiska "a a Aakif mamma fa" kuka yaro yasa daga Zaune Yana Mika mata hannu domin Yunwa ta cishi sosai babu wadda ya bashi abinci d'aukar shi tayi zata nufi d'akin Jiddah taga fitowar Sa'irah Kofar ta gani Kulle cikin mamaki tace "Ke inna Maman Aakif?" Nan yarinyar ta fad'a mata yadda Akayi i'do ta zaro tana kallon Yarinyar kafin tayi magana wayarta yayi Kara, "Iyah" tace sannan ta d'auki Kiran "Assalamu alaikum Nafisa" cikin Girmama Nafisa ta amsa Mata Iyanmu tace. "Meke faruwa Ummi ta kirani wai Hauwa'u ta nufi Kaduna!" Cikin sanyi jiki Nafisa

ta sanar mata komai salati Iyanmu tayi sannan tace. "Yayi kyau zai Gamu dani i'ta Kuma Zainab zata ga karshenta Sakamakon Yanzun tun anan Duniya Allah ke nunawa insha Allahu sai rabbi ya saka mata."

'Dakinta ta nufa da yaron shayi ta had'a mishi me Kauri ta d'aurashi saman cinyata kafin ta bashi ya fara Kokarin Karb'a, tana sanya mishi Kofi a baki da sauri Ya Karb'a Yana Sha yana sauke Ajiyan zuciya, wani i'rin kuka tasa ganin yadda yaron yake karb'an tia din a Yinwace. "Allah saiya saka maka" wani i'rin kuka ta fashe dashi kallon yadda yaron yake rik'e da Kofin tayi "Wannan wani i'rin son zuciyane yaro karamin za'a rabashi da uwarshi!" Aakif na gama sha ya sake kofin tare da qwala ihu Yana Kiran "Mamma.." mikewa tayi dashi tana jijjigashi Jumana ce ta shigo "Momy lafiya naganki da Aakif Aunti Amariya fa kofarta ƙulle?" Kallon yarinyar tayi sannan tace. "Kisa ruwan zafi ki masa wanka" ajiyeshi tayi domin ya fara barci ta nufi Band'aki tayi wanka.

Zaina ce ta fito bataga Yaron ba rik'e Qugu tayi tare da K'unduma ashar. "wani d'an shege da shegiyace ya d'aga yaro anan? Akan mutum yake da za'a d'auka?"

Nafisa ce ta fito daga d'akinta hannuwanta hard'e a baya, ta rik'e igiyan caji. "Nina d'aukeshi ko zaki dakeni ne, kaman yadda kika sa ya daki Yar mutane.." Hannun Zaina ta d'aga da niyar marinta da sauri Nafisat ta rik'e Hannun. "Ki nada tsaurin i'do ga shegen saurin Hannun Yanzun ke ki kalli tsaban idona Kice zaki mareni? Sa'arkice ni Zainaba?.." Zaina tace. "Ked'in Banza ked'in wofi wacece ke da baran dake ki, ba..." Kafa tasa mata ta fad'i K'asa "Kina cikamin ciki Zainaba Yau zanci ubanki harda uwarki zanga uban da ya d'aure miki tsuliya kike zuba mulk'an Gidana dan inna Miki shuru inna K'yale ki.." zuba mata wayar ta shigayi sosai Zaina ke ihu tana Kare K'anta, Mikewa tayi da sauri tana rik'e zaninta Fure dake tsaye tasa dariya. "Yar Banza Wallahi Nafisa baki burgeni ba, dakin fasa jikin shegiya.."

Zaburowa tayi tare da Rik'e wiyar rigan Fure "Ni ni kike fad'awa haka zaki gani zan miki abinda harki bar duniya bazaki manta ba, na barki na Yau!" Tureta tayi ta fad'i kallon Nafisat tayi. "Kin burge tunda har kika iya dukana Amma zakiga ladar dukan domin zan miki Babban Kyauta..." Wani i'rin dariya tasa harda hawaye tana mata kallon Tsana "Kaman yadda kika Zane jikina sena addabi rayuwarki, kaman yadda kika sani kuka, saina saki, zan Kashe ki da ranki, zan miki abinda kina jin kukan Amma zaki kasa Yinsa! Nice fa! Zainabu-Abu HahhhHahhh!!" Ta karasa maganar tana dariya kaman zautacciya.

"Bakince ke shed'aniya ba, insha Allahu babu abinda zan gani Wallahi Kaman yadda kike tak'ama da shed'an, Haka nake tak'ama da Allah Yanzun aka fara!" Kad'a kai Zaina tayi tare da shigewa d'akinta.

Yana dawowa ya shigo d'akinta. Yana kallonta ta saka kwalli a idanunta "Muazzan ni Nafisa ta duka dan nace ta bani Aakif harda zagin iyayena ni ta Zane har tana ikirarin saita Kashe ni akan ka saki Hauwa'u-Jiddah, Taci min mutumci ni Wallahi ka sake ta, daman nace zan Bata ladar abinda tamin ko ka, saketa Kona bar maka Gidanka..." Jikina rawa yace. "Dan Allah Zaina kiyi hakuri wallahi zanyi yadda kike so" takarda ta wurga mishi "Zana mata d'aya Kuma ka karb'o

Aakif ka kawo min!" Dauka yayi da sauri zama tayi tana murmushi Yana Gamawa ta Sashi gaba, Zaune tayi akan Kujeran falo shi Kuma Yana K'asa Fure ya fara Kira, a waya sannan ya Kira Nafisat.

Suna karasowa ya Mika mata takarda "Meye wannan?" Cikin masifa yace "ki Karb'a in kin bud'e Kya gani! Sannan Aakif ba d'anki bane da zaki d'ukesa nasan dake na zab'eta dan haka ki ajiye min d'ana!!" Ya kasara maganas kicin tsawa.

Murmushi Nafisat tayi. "Qwarai ba d'ana bane, naka ne Amma ka sani Allah yana sane Yana ji Yana Kuma Gani, Zakaga sakamako"

Bud'e takardan tayi a razane ta kalleshi tare da kallon Zaina.

"Kyautace! Na baki sannu a hankali zan baki ladar dukana da kikayi Ba'a tab'a ni a tashi Babu kyauta me tsoka, Na, baki wannan".

Mikewa Nafisat tayi tare da sauke yaron kasa jiki. "inkin manta zan tuna Miki Ayi a Kare yafi abari gobe a karasa". a sanyaye ta nufi d'akinta Fure ma jikinta yayi bala'in sanyi "Kinsa ya sake ni ko? insha Allahu zai mike fiye da abinda kika min namiji ne fa? Ance miki namiji D'an Amana ne wallahi ko kad'an ba'a bawa namiji Amana , ba'a d'aukan yarda abawa namiji , Namiji bad'an goyo da zani bane, insha Allahu Zaina Zaki ga sakamako karki manta aci a sha a rage don gobe, Amma Kuma aci yau aci Gobe , shine Ci! Gida kuwa inna Zaune daram domin zuwa kikayi kika same ni" shigewa tayi d'akinta

Kallon Banza ta watsawa Fure "Malama tashi ki bar Nan!"

"Abinda Dama ta jure, hagu. Bazata Jure ba, ko Nima sawa zakiyi ya sake ni?"

Girgiza kai Zaina tayi. "Ai abun fad'a namai Baki ne." Tace tana murmushi

Kallon shi Fure tayi, "Kayi shuru ai baka ga komai ba, bade ka zauna Gindin Zaina ba, se kayi kuka Mara iyaka shashasha kawai.."

d'akinta ta shige mikewa Zaina tayi zata shiga d'akinta yace. "Kinbar yaron Kuma?"

"Kai a banzar tunaninka zan rik'e d'an kishiya ne, Allah sauwake, ai ya Zama na tsakar Gida, Kuma Wallahi naji ka d'auki yaron Nan ka kai, mata saika gamu dani" ta karasa maganar da jan,tsaki sannan ta shige abinda.

Kallon Yaron da ya zauna shuru yayi wadda da tukan alamu ya fara maraicin uwarsa "Aakif" yace Yana mikawa Yaron hannun "Affa.." yaron yace Yana Mika mishi hannu d'aukar shi yayi tare da Rumgumeshi hawayen da baisan na menene ba ya sauko mishi. d'akin sa ya nufa da yaron,

Kwana na Goma aka sallamoni Gida. Koda muka dawo kurma nazame musu bana magana damuwa tamin yawa Yarona nake son gani kusa dani inna kewar d'ana sosai Yau da abin ya isheni Fitowa nayi na tsaya mata bakin Kofa. "Wallahi kewa K'anin ki ya dawo min da d'ana.. Ummi" Murmushi tayi sannan tace "Yi hakuri shalele" kuka na saka mata tare da zama a kasa Hanisa dake Zaune tace. "Iah ji shashasha Yanzun kuka kike Ai wiya Bata kisa, Babu abinda zai samu d'anki Kinga Anwar na Miki dariya Zamu Ialub'o Sir Nabil, yayi Wuf dake Kinga saiya Baki wasu 'Ya'yan ba d'aya ba Biyu ba.."

Hannu bibbiyu na auna mata zagi. "Ba uwar da zanyi dashi ki barni Kinga tashi ki bar Gidan Nan Wallahi kafin na b'ata ranki!" Na fad'a inna niman abinda zan bigeta dashi kallon Hanisa ummi tayi sannan tace. "Tashi! ki tashi Nagode tunda kinzo ki b'ata mata rai ne, a dai-dai wannan lokacin da take cikin damuwa Bai kamata kizo da wannan batun ba" Cikin sanyi jiki Hanisa tace. "Kiyi Hakuri in-law" Cikin zafin maganganunta Jiddah tace. "Bakisan zafin da nake ji, bane Shiyasa kika Fad'i Haka Amma ba komai, ki tafi kawai banson Ganinki" fita Hanisa tayi.

"Kiyi hakuri na kirashi Yana zuwa" da sauri nace. "D'ana nake bukatar gani ba shi ba uwar me zan mishi"

Murmushi ummi tayi domin tana mata uziri sosai tunda abin nan ya faru ta zama mai zafi Rai, bata da hakuri kana fad'a mata zata baka amsa , can tace. "Ummina dan Allah kiyi hakuri inna miki rashin Kunya, ba laifi na bane, na kasa Jurewane. na kasa Yin hakuri, ni nasan rad'ad'in da nake ji na rashin Aakif"

Sati biyu tsakani ummi na Zaune falo.
Sallama yayi tare da shigowa Kujeran dake fuskantar ta ya zauna. "inna yaron?" Ummi tace mishi " 'Da nawane inna da iko dashi na Riga na sallameta tayi rayuwarta Nima nayi tawa rayuwar, bazai Yuwu na barmata d'ana ta b'ata min tarbiyanshi ba Kamilar mace ake barwa Yara ba watsattsiya ba.."

Dai-dai fitowarta. Nuna kanta tayi tana dariya tare da Zama "Me acikin ido banda tarin ruwa, ka sake ni shine zai hanani rayuwa, Ance maka sonka nake dazai dameni! So uku kana jifana da K'azamar kalma nice Karuwa mazinaciya Ko? Yau Kuma kace min watsattsiya! Bazan maka Gorin abinda na maka a baya ba, Amma kaje nabarka da fitowar rana da fad'uwarsa insha Allahu Kalman da kake jifana dashi zai tsaya a kanka.." mikewa tayi tana hawaye tabar Gurin

Kuka ummi ta fashe dashi tana kallonshi "A gabana kake wannan maganar zarginta kake daman Arab yaushe ka zama Haka! Yaushe ka zama Mara adalci da son zuciya Naji Nagode tashi ka tafi...!"

Azuciye ya mike "Akan yar iska kike Korata shi kenan na tafi.."

Fita yayi mikewa Ummi tayi da sauri ta nufin d'akin da Jiddah take tab'a kofar tayi taji a kulle. "Zoki bud'e min Kofa" murya cike da kuka tace "Me zan miki Ummi kina ji ai Kinji abinda ya fad'a, Yace bazai bani Yarona ba, kin kasa yin komai, ya rabani da d'ana ya baiwa Muguwar

matar Sa ba matsala yaje Allah na Nan"

"Ki bud'e min Kofa Hauwa!" K'ememe taki bud'e Mata kofar Haka har ummi ta gaji ta koma falon ta zauna.

Wayarta ta d'auka tare da Kiran Nafisat tana d'auka tasa mata kuka. "Lafiya?" Nafisat tace mata

"Maman Jamil wani nauyi zan d'aura miki Ga amanar Aakif dan girman Allah banida wadda zai masa Kyakkyawan rik'o sai ke, Ki kula min da Yaro na dan Allah" kashe wayar tayi tare da fashewa da sabon kuka. "Allah kana gani Allah in wani laifi na maka wadda kake Hukuntani Ubangiji na tuba, Allah ka yafe min.."

Maman Faruq
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: ♡SIRRIN ƊAUKAKA..!♡*

Farin Jini Writer's Association

Page23.
♡

Haka ta wuni a d'aki tana kuka ko lek'owa waje batayi ba, rayuwar daki tacigaba dayi, Bata jin dad'in komai ko abinci ummi ta kawo mata sai tayi da gaske take cin kad'an , kukan d'anta take yawanji yana cika kunnuwanta Ga zaurawa ta ko'ina zuwa sukeyi , bata san ya'akayi jama'a suka san bazaurace i'ta ba, Yau da abin ya i'sheta ne ta fito d'akin ummi ta shiga tana sallan walaha , zama tayi kusa da i'ta tana sallamewa ta kwanta jikinta tare da sakin kuka, addu'a ummi tayi ta tofa a ruwa d'agota tayi tare da Sanya kofin a bakinta Bisimillah tayi tare Da shanyen ruwan tana sauke ajiyan numfashi. “Ummi.." kasa karasawa tayi sakamakon hawayen dake zariya saman fiskanta share mata fuska ummi tayi “Allah ya sanya Dangana a zuciyarki Ubangiji ya sassauta wannan zafin ran da kike fama dashi kiyi hakuri kiyi hakuri, ki fauwala Allah lamuranki ki cire damuwar Aakif wiya bata kisa..." Hannuwan ummi ta rik'e

“Wallahi bazan i'ya ba, 'Dana na cikin wani hali Yana bukatar kulawata Dan Allah ki rok'eshi ummi ya bani Yarona! 'Dan uwanki ne ,Bakiji yadda kunnuwa suke jiyo kukansa ba, Kullun mafarki nake dashi yana kuka Yana mik'omin hannu ummi.."

“A Gabanki so nawa inna kiransa ba ya d'aukan kirana so nawa inna tura masa saƙo baya bani amsa laifi na kike ganin ko? Zakice nafiya son Kaina da ƙanina ko Hauwa'u?.." zataci gaba da magana Jiddah tace. “Kiyi hakuri ummi" daga Haka ta mike ta fita, d'akinta ta koma.

Bayan sati biyu.

Fitowarta kenan daga wanka taji yaro yayi Sallama Himar ta saka tare da Fitowa “wa kake Nima?" Yaron yace. “wai ana Sallama da Jiddah.."

"Koma kace bata Nan" har zai fita ummi dake Fitowa tace “Je kace tana zuwa"

"Amma ummi.." katseta tayi “Kimanin wata takwas kenan duk wadda yazo sai ki Kore shi me yayi zafi Jiddah?" Sunkuyar da kai tayi K'asa .

“Babu Aure cikin tsarina a Yanzun d'ana kawai nake bukata, ummi duk wadda ya aureni Yanzun gangan jikina ya Aura zuciyata da tunani na yana ga Yarona, ki barni ummi bana bukatar wani Namiji cikin Rayuwata!" Ummi tace. “Laifi wani baya shafan wani shalele Nah, in har na i'sa jeki shirya ki fito.." ‘Daki ta koma tare da saka doguwar rigan atamfa shigowa ummi tayi tare da kallonta sama da K'asa “wani i'rin shigace wannan? Haka zaki fita Baki shafa mai bare Hoda, Yanzun wannan katon Himar d'in zaki saka? Haba Jiddah ban hanaki suturta Jikinki ba, amma ki cire wannan Himar d'in ki saka mayafi yaushen rabon da kiyi kwalliya ya kamata ki sanyawa zuciyar ki nutsuwa"

“kwalliyar me Ummi? A Yanzun ban bukatar wani Namiji yaga kyawuna bare har na rud'ashi, zamana a Haka yafi min wallahi in har kika ce na sake shiga na fasa fitan!" Murmushi ummi tayi “Allah ya sauke wannan shed'anin dake kanki"
"Ameen" tace sannan ta fita.

Batayi Sallama ba ta bud'e gaban motar da yake “Kaine wadda ke niman iso dani ko ? da alama an fara bud'e babinka na Karshe To bara na fad'a maka ban shirya Aure ba, Bak'in aljani gareni abinda yasa Mijina ya sake ni kenan Wallahi kana Aurena Zaka mutu in kashirya ma yaranka su zama marayu to.." da sauri Mutumin yace “a a Wallahi" murmushin jin dad'i tayi sannan tace “Shi kenan zaka i'ya tafiya"

Tana tsaye Gurin ya tada motarshi sai da taga fitarshi sannan ta shigo Gida, Haka ta ringa Koran duk wadda yazo Gurinta da Sunan Baƙin Aljani gareta. Wasa wasa aka shafe shekara da watanni Abin na Bata mamaki ganin yadda take Wahal dasu Amma har yanzun Banzaye wawaiyu basa ganewa Matsorata ne, ta kanyi dariya in ta tuna yadda suke rikicewa da zaran tace Bak'in Aljani gareta. i'do kawai ummi ta zuba mata,  randa abin ya i'sheta ta isketa d'aki lokacin tana duba sakonin ta Email d'inta “Hauwa'u" ummi ta kira sunanta. Kallo d'aya Tama ummi sannan ta d'auke Kanta domin tasan abinda ya kawota “Na'am Ummina" janye laptop d'in tayi daga Gareta. “Hankalin ki zaki bani magana zamuyi" tagumi tayi tare da zuba mata i'do “Maiyasa duk wadda yazo niman Aurenki kike koransa? Ki fad'amin Auren ne baki so ko me?"

Hannunta ta matse har sai da yai Ƙara. “Ummi bawai Auren bane bana so ban shiryawa Auren bane,  sabida har Yau, ban samu wadda zuciyata tayi na'am dashi bane, Nifa ba Budurwa bace ya kamata in samu nutsattse wadda yasan mutumci da Kuma kimar d'iya mace , Namijin da zai iya kula dani nake bukata inna son Namijin da ko yau na mutu zai ringa tunawa  dani Ummina inna son Namiji Kamili mai Addini inna son Namijin da yasan  wacece mace , abin Nufi Namijin da zaiyi Hakuri da Halayyar ta Akwai Mazan da Basu da Hakuri da zaran mace ta b'ata musu zasu hauta da fad'a ta inda suke shiga ba ta Nan suke fita ba, inna son Nagartacce wadda zai na min Uziri wadda da zaran nayi masa kuskure Zai rarrashi zuciyarsa wadda da zaran na ɓata masa in na bashi Hakuri zai karb'i Uzirina Ya Hakura inna Son Namijin da zai tarairaye ni inna

son Namijin da zai shagwaɓa ni inna son namijin da zai mai dani tamkar yarinya inna son Kimtsattse tunda Kinga ni watsattsiya ce ko Ummi? Banida Nutsuwa! Mazinaciya, inna son Salihi wadda zai karb'e ni a ko ya-ya nake, inna son Namijin da zai Mutumta ahalina Ya girmama min Ummina ,Yah Allah Babu wani sarki Bayan Kai, Allah Kai mai Kyauta ne, Ubangiji kamin Kyautar Bazata! Allah kai mai azurtawa ne, Yah Rahimu ka azurtani da Kimtsattsen Miji. Allah kai meji Ne, Ubangiji ka amshi rok'ona Albarkan Wannan rana ta Juma'a..."

Wani i'rin kuka take mai tab'a Zuciya, tana magana. i'ta kanta ummi jikinta yayi masifar sanyi a duniya, Babu kalma mafi Muni da za'a jefeka dashi kaman ace maka mazinaci abun da ciwo shiyasa har yau take jinshi a ranta i'ta a iya sanin da tayiwa Jiddah yarinyar Akwai yafiya Amma da wuya ta manta abinda aka mata duk da tariga da ta yafe mishi tasha jin tana addu'ar Allah yabi Mata Hakk'inta Akan K'azafin da aka mata, abin da ciwo sosai Amma ya za'ayi sai Hakuri.

“Ummi kina ganin kaman ban kyautawa ko? To kiyi hakuri tunda Aure kike so nayi zan tsayar da Mutum nayi Amma nasan bani da nagartan da za'a Soni ko Ummi?" Ta karasa maganar tana tsare Ummi da idanuwanta masu Kama da mage, mayar da kukan dake son kwace mata tayi.

“inji wa? duk mai niman mace ta gari yazo gareki, Wallahi kina da nagartan da za'aso had'a zuri'a dake, matakin nasara shine hakuri, Kawaici d'auke Kai, ka mayar da komai ba komai ba, ka d'auki rashin gaskiya a inda kasan kai mai gaskiya ne, ka rufawa d'an uwanka Asiri! Duk fa kece mai  wannan halin shiyasa kullun nake takaicin maiyasa Ibrahim ya barki? Wani lokacin nakan masa uziri sanin baya cikin hayyacinsa, kiyi hakuri Hauwa'u insha Allahu Ubangiji maji rok'o ne Allah zai baki Mafiyinsa"

Rumgumeta nayi inna kuka Wallahi inna Mata k'auna, na tsakani da Allah “Nagode Ummina Allah yaja da ranki"

Shafa kaina tayi “Amin shalele Nah" Daga Nan ta shiga mata nasihohi har aka Kira azahar sannan tabar d'akin kwanciya nayi kasancewar inna fashin sallah Nan na tunduma tunanin Duniya, Kiran da sahiba ta ƙwala min ne yasa ni mikewa “Maman Aaleen" Murmushi tayi tare da Zama gefenta "Na'am Maman Aakif Kinga tashi muje Kasuwa zaman gurin d'aya ya i'sa haka" Yamutsa fuska nayi "Ke Bari ban son fitan ne kawai" da sauri tace "Haba Sahibata taso muje muga Gari Allah da kaina zan tuka motar!" Ba yanda na i'ya ganin ta nace yasa ni miƙewa na Shirya.

Mun tadda Ummi Zaune da Yan biyu tasowa sukayi tare da gaishe ni shafa kansu nayi inna jin dama nawa ne haka “Ya karatu Yan biyu na" had'a baki sukayi Gurin fad'in “Alhamdulillah Anti-meh" Halimatu tace “Hajiya Ummi ga angwayen ki zamuje Anguwa da sahibata” Ummi tace “Hanisar fa wato Kuna ware min 'Ya a duk lokacin da kuka keb'ance Ku biyu Ko? bana son Haka fa, banson wariya" Hararan Halimatu nayi “Nifa Ummi ba ruwana  i'tace dai da kini bibinta gwara ki fad'a mata" Jan hannuna tayi muka fita tana mai cewa. “Naji Ummi ayi Hakuri za'a Gyara" muna karasawa Gurin motana ta fasa dariya nace. “Yar Banza Dole kiyi dariya"

Bud'e motar tayi tashiga Nima na shiga d'ayan gefen “Allah sarki Sir Nabil Mutumin arziki..."

Buga sitiyarin motar nayi “Ke zanci abun kazanki Wallahi in baki rabani da maganar nan ba, haba ke kiyi Hanisa tayi! Mutumin Nan Yanzun haka ya mance daku Kuna Nan Kuna damin kanku Akan shi..." Da sauri Halima tace. “Wa? Wallahi haihuwar su Aaleen Setin Dirowa na kayan Yara ya sai min ga Kyautar dubu talatin cab ai Sir Nabil ba k'ashin Yarwa bane.."

“Kinga dakata! daman maganarshi ne yasa kika fito dani koya?" tada motar Halima tayi. Anguwar Kawo sukaje Gidan wata k'awar su, sun Sha hirar yaushe Gamo kafin ta rako su “Sai inna Kuma Yamma nayi fa?" Na fad'a inna kallonta “muje mu d'anyi siyayya mana"

“Toh muje" muna isa ta faka motar Fitowa mukayi wayarta ne yayi Kara muna tafiya tana waya inna gaba Bansan ya akayi ba na bige wata mata cikin masifa tace “Dalla can ke makauniyar ina ce?" Kayanta na shiga kwashewa “Yi hakuri..." Ai kasa karasawa nayi wazan Gani.. ihu tayi tare da kaimin Rumguma “Jiddah..!" Nima cikin jin dad'in nace “Fadila kece?" Jan hannuna tayi muka koma Gefe “Nice ya kike ya Bayan rabuwa ya iyalai ? Kuma Dan nasan Yanzun kin Tara sosai.." dariya nayi nace “Alhamdulillah ya naki iyalan?"

“Alhamdulillah Jiddah kai gaskiya naji dad'in Ganinki sosai Anan kike har yanzun?" Girgiza mata kai nayi “a a nade Zo ne..." Horn din da aka mata ne yasa tace. “Oga na jirana bani Number ki zamuyi magana" musayar Number juna mukayi tare da yin Sallama “Keda waye Haka?" murmushi nayi “Wallahi nida Fadila ce Yar ajin mu" Halima tace “ayya" tafiya muka fara yi, nan ta siya abinda zata siya muka fito Gurin Biyan kud'i ne naja birki, inna kallon matar dake Gaban mu kasa hakuri nayi na tab'a ta. “Ke kaman Jummai?" Juyowa matar tayi tana kallona sama da K'asa “Hauwa'u d'iyar Asma'u da Usama, tsohuwar matar d'an Kasuwannan Ibrahim Arab!" Ta karasa tana murmushi “Makira banyi mamaki ba tunda nasan Halinki azzaluma butulu wacce Bata San halacci ba, ina dukiyata da kika tattara , kece sanadiyar Mahaifana ni Kuma insha Allahu nice ajalinki Makira makaryaciya insha Allahu Zaki ga karshen ki.." dariya tayi tare da fita bin bayanta nayi ina zaginta tare da tsine mata “Ke Kuma fa da zaki biyo matata kina zaginta..." Katseshi nayi. “Au Allah Nagode maka matarka ce ma? Ubangiji ka i'ya had'i me Gidan hayar mu ko? Banyi mamaki ba, domin da had'in bakinka ta kwashe dukiyata wanda yayi sanadiyar fad'uwar mahaifina ya samu ciwon shanyewan b'arin jiki, hakan bai maka ba ka tashe mu a Gidanka wadda sanadiyar bakin cikin nan take mahaifina ya Had'iyi zuciya ya Mutum mahaifiyata tabi Bayan shi insha Allahu zaku ga karshen Kun Tsoffin Banza kawai..!” Halimatu ce tazo taja hannunta Mota ta shiga da i'ta,

“A Ina kika San mahaifiyar Aaliyah da har kuke sa'in-sa Jiddah?" Bud'e i'do nayi sosai inna kallonta tare da jin mamakin furucinta. “daman wannan tsohuwar Banzan ce uwar Aaliyah ahh lallai biri yayi Kama da Mutum tunda har Hali yazo d'aya ba shakka wato i'ta ce Uwar Aaliyah..." Na fad'a inna dariya mai had'e da hawayen bak'in ciki, domin ban Macen halin da matar Nan ta jefamu ba. “Meke tsakanin ku?"

“i'tace tsohuwar matar babana, a gonarshi ya tsinceta tana kwana wai i'ta bakuwace ya kaita Gidan maiGari shine maiGari yace tudda Gidanshi da D'aki Kuma Yana da Hali yaje ta zauna Gurinshi Ashe mutumiyar Banza ce mahaifina ya mata komai mahaifiyata ma Haka, domin ganin yadda Jummai ta nuna i'ta mutumiyar Kirkice yasa mahaifiyata da kanta tace ya Aureta,

Bayan ya Aureta Nan ta fara Fitowa da halinta inda a lokacin da wayo na, inna ganin komai Kuma inna ji Haka aka wayi gari ta siyar da Gidan da muke ciki tare da Gonan mahaifina tatattara komai tabar Gidan dalilin Haka yasa muka shiga matsin rayuwa Bayan mun koma Gidan haya, mahaifina ya yanke jiki ya fad'i ganin bamuda komai na hatsi ga 'Yan uwanshi duk sun gujeshi ke Sahiba munga rayuwa a gaban idona mahaifina Ya mutu... Naga tozarta da wulak'anci, wasu mutanen basu da tunani basa tuna Goben su, masu tuna cewa Gaba tafi baya yawa ƙalilan ne. Abinda matar Nan Tama mahaifiyata na musgunawa Allah kad'ai zai saka mana..."

Shuru Halima tayi tana sauraronta kafin ta sauke numfashi. “taɓ lallai wannan Mata ta cika butulu gaskiya taci amana Kuma insha Allahu Allah zai saka muku Yanzun inna dangin mahaifiyarki?" Jiddah tace. “Ban sansu ba!" Halima tace. “Ya kamata ki laluɓosu gaskiya!" Gyad'a kai tayi “insha Allahu zan duba kayan mahaifiyata domin Akwai wani kundin data tab'a bani sai dai ban tab'a bud'ewa ba. ban tab'a bincika ba, domin bana duba abinda ba'a bani izini ba" Jan motar tayi muka fara tafiya “Ya kamata ki bincika sannan ki dibo dangin mahaifin ki ,duk da abinda suka Miki Bai kamata ki watsar dasu ba, naka naka, Ne, duk lalacewarsa" jingina kaina nayi da jikin Kujerar. “inna Musu aike akai akai bana jin zanje garesu Nan kusa domin zuciyata Bata bani hakan ba"

Halimatu tace. “Allah ya kyauta" Haka har muka karaso Gida.

***

Zama tayi kusa dashi tare da d'aura kanta saman kafad'arshi Tunda suka dawo k'asar su ,ta rasa gane Kanshi da Gindin shi, ya mace akan wata daban wacce a yanzun take matar wani bashi da kuzari kaman yadda yake Da, shafa K'asunbar sa tayi, duk da shi ba ma'abocin tarawa bane domin bata K'aunar ganin Gashi ko sili d'aya a fukanshi “ƙalbi shekaru masu yawa har Yau, ka kasa , cire wannan shegiyar yarinyar a ranka Bayan kasan matar wani ce Yanzun Haka sun hayaiyafa , Jin maganar Haihuwa yasashi zabura ya mike Zaune “Nuwairah tashi muje a binkici Lafiyar ki inna bukatar Haihuwa nasa Sunan Amma h na!" Wani i'rin kallo take masa daga bisani ta fashe da kuka tare da shigewa cikin Gidan da gudu tayi shashin iyayen su! “wayyo na mutu na lalace Nabil zaka kashe ni inna sonka kana Son wata macen da take tare da mijinta wayyo Innarmu" (mahaifiyar Nabil kenan) Da sauri ta fito ta kamata “Me Kuma ya had'a ku wai kukan kullun baku rabuwa da rigima ne? Haba sai kace ƙananun Yara girmafa ake kodan baku ganku da Yara bane!" Ta fad'a tana kallon Nabil dake shigowa “Innarmu ki tambaye shi har Yau yarinyar Can yake so shekara kusan takwas ko Tara ne ya kasa cireta a ranshi bare ya Rumgumi K'addara nifa na gaji da Halinsa baya bani Kulawa a matsayina na, matarsa bashi da wani lokaci saina tunaninta" Da sauri ta mike tayi d'akin Mama-Sadin wacce ke kwance tsawon shekaru tun tafiyar Autarta Asma'u har yau tana kwance komai mata ake Amma tana i'ya magana tana motsa hannunta Zaune ne dai bata i'ya mikewa “Mama-Sadin kicewa Angonki ya kulani Yana azabtar da Ruhi na. na gaji fa Aure ba riba ko daga gurin shi nema wa yasani..."

“Lokacine baiyi ba, in yayi zaku haihu tunda kullun in kuje asibiti lafiya lau ake baku sakamako insha Allahu lokaci na zuwa kije zan masa magana" mikewa tayi "Toh Nagode mama!"

“Ance ana nimanka Gurin aiki Amma kaƙi komawa me kake Nufi?" Sosa kanshi yayi tare da Sunkuyar da Kanshi ƙasa “Nabil.."

“Na'am Innarmu"

“Tashi ka fita min Anan" mikewa yayi “Toh kiyi hakuri zan duba Kuma zan tafi Amma inna mafisar ƙaunar Jiddah Babu yadda za'ayi zuciyata ya rabu da i'ta!..."

“Kinji ko Innarmu? Kina ji a Gabanki Yana fad'a Amma kin kasa hanashi fad'a! Yah Nabil so kake ka tarwatsa zuciyata ne! Wallahi ni kad'ai na ,na i'sheka Rayuwa duniya da lahira! inka Auri wata mace kasheta zanyi ko ka manta Jini shuwa ce! Babana Arab ne, ko 'Yar wa ka Aura saina kashe! Kuma na kashe Banza Kasan inna da Gata, Yayyu na zasu Tsaya min ubana zai tsaya min" Sanin halinta na kishin Banza ne yasa mahaifiyarshi barin Gurin.

Jikinshi ta fad'a tare da sakin malalacin Kuka tureta yayi tare da barin Gidan Gabad'aya Yana sane da motar dake binshi har ya karaso wani gurin hutawa Fitowa tayi tana rangaji kaman wata karaman yarinya “Shekara nawa kina bibiyata Aaliyah na fad'a miki bana sonki bana K'aunar ki, Haba! Ki barni mana ki koma k'asarki. ki dena bibiyata Haka.." murmushi tayi tare da Kama hannunshi tana murzawa cikin nata “Sir Nabil inna sonka Ko baka sona zan zauna da kai a Haka, wannan de da kake Hauka akan ta, tana Gidan Mijinta, to menene dan munyi Aure kai nake jira har ilah Yau, sai ka Aure ni Wallahi Kona addabi Rayuwarka!" Mikewa yayi tare da Zame hannunshi d'akin da ya Kama ya nufa da Mugun gudu tabi bayanshi tare da tura kofar Ganin Yana shirin Kullewa tana shiga ta Rufe tare da Zame doguwar rigan jikinta sai da ta cire komai ta tsaya Gabanshi tana juyi “Mena rasa? Gaban ne bani dashi ,ko Bayan? Kai ma kasan na cika Mace har mace!" Ta fad'a tana juyi a Gabanshi. “Kin rasa martaba nagarta nutsuwa da mutumci Kamun kai  inda Jiddatuh ta fiku kenan Kamun Kai, tallar kanki fa kike min Aaliyah?" Matsowa tayi jikinshi tare da Rumgumeshi keyarshi ta tallafo tare da had'e bakinsu tana mishi wani i'rin tsotsa na fitar hayyaci cike da bukatar shi take tafiya da harshenta cikin bakinshi hannuwanta na yawo a sassan jikinshi.

Lokaci d'aya ya d'auke Wuta kwanciya sukayi saman Gadon nan taci gaba da birkita masa lissafi cikin salon bariki da ƙwarewa wani i'rin numfashi suke fitarwa a hankali ta zame bell d'insa tana shafa K'asan maranshi wani i'rin Numfashi yaja da karfi tare da matse Dukiyar fulaninta wadda suke cike fam kaman balon-bolon wani i'rin kukan k'irsa tasa mishi jin yadda yake matse nonuwanta “Dan Allah Sir ka Aure ni inna masifar K'aunarka.. Washhh" tace Jin ya matse ta sosai Kara birkice masa tayi tana so lallai sai ya mata yadda take so ganin tana Nima Sashi shiga rayuwar da ya tsanane yasashi tureta daga jikinsa Yana Jan tsaki. “Ko mata sun Kare banga abinda zanyi da ballagaza i'rinki ba" wani i'rin dariya mai ciwo tayi “Ni ba? Wallahi inna Nan tare da kai" Kayanta ta shiga mayarwa sai da ta gama tsaf sannan ta Matso gabanshi tare da d'ago fiskanshi tana mishi wani i'rin Kallo.

“Sir Nabil inna maka Soyayyar da zan iya kashe rai ta dalilinka Zaka Aureni Dole saina mallake ka, saina d'and'ani wannan Bananan saina cinye shi.." ta fad'a tana kokarin kai hannunta Make mata hannu yayi tare da jan tsaki sunbatar Goshinsa tayi. “Nasan ka kusa dawowa Bakin aikin

ka, inna nan inna jiran ka, Sahibi Nah"

Tana fita ya dafe Kanshi daurewa kawai yayi yakai zuciyar Shi nesa in ba Haka ba, da Yanzun ya aikata b'arna Allah ya kareshi daga sharrin ta akaro na uku baya fatan su Kuma Had'uwa domin Aaliyah shaid'aniya ce ta bugawa a jarida ,dole sai da ya Koma Gida ya nimi Nuwairah wuta-wuta duk da Yanzun an fara girma Amma har Yau i'ta uwar raki ce, Abu kad'an zatace ta gaji Haka dai yata lallab'ata harya samu Biyan bukata , Matseta yayi sosai a jikinsa Yana fad'in . “ Nagode Jiddatuh Nah inna miki Soyayyar Jini da, Jini..." Abin takaici Yana jikinta Amma Sunan wata mace daban yake Kira tureshi tayi tana kuka. “Nagode Yah Nabil Allah zai saka min, kana jikina Amma wata Banza kake kira Wallahi ban yafe ba!" Ta fad'a da karfi tare da sakin kuka. Jawota yayi jikinsa. “Kiyi hakuri Nuwairah Wallahi bansan na fad'a ba.."

Katseshi tayi “Eh man abinda Zaka ce kenan tunda Soyayar Banza ta Rufe maka i'do" rarrashinta ya shiga yi, da ƙyar dai ta daina kukan tare sukayi wanka Yana Fitowa yace ta zauna cikin shirin A satin me zuwa zasu Koma Nigeria Gyad'a mishi kai tayi tana hawaye.

Muna Zaune nida Ummi da Yamma wayarta ne yai Kara Ganin Number mai Kiran sai da Zuciyata ta tsinke , Maman Jamil ce, d'auka ummi tayi “Me kika ce Nafisat?" Mikewa ummi tayi tsaye

A b'angaren Nafisat taci gabana da magana “ummin Halimatu Wallahi Yanzun na dawo na samu Aakif kwance jikinsa ya sab'ule ruwan zafi Zaina ta watsa mishi wai dan tayi Girki yaje ya bud'e Yana ci, shine ta watsa mishi tafashashshen Ruwa" tana kuka ta karasa maganar

“innalillahi wa'ilaihir rajioun Ni Sawdat Allah ka mana mai kyau.." da sauri na d'auki Makulin motar ummi dake saman center table na fita tsaban Na rasa Nutsuwa ta bansa mayafi ba, hatta takalmi Babu a kafata cikin ihun nace. “Maza baba bud'e min kofa!" Zaiyi magana ta sake daka mishi Tsawa tare da shiga motar Wani i'rin jan motar tayi kaman zata tashi sama da sauri ummi ta fito tana fad'in. “Dan Allah karka barta ta tafi nashiga uku..!" Ganin ta fita yasata zama daɓas tana hawaye wannan wani i'rin zalunci ne? driventa ta kira suka bi bayanta.

Tuki take cike da Ganganci tana kiran Sunan d'anta. “yanzun 'Dan shekara Hud'u aka k'ona mai Aakif ya tsare mata? Tsanar bai tsaya iya kaina ba, har abin dana  Haifa sai an kashe na shiga uku Aakif ta k'onawa jiki da ruwan zafi wayyo Wallahi bazan yafe ba..!" Yanata kokarin kauce mata Amma ya kasa ganin yanda Lokaci d'aya motar ya shige masa Gamm suka bige juna ,juyi motar yayi tare da Gangarawa ya bigi wani bishiya “innalillahi" kawai ummi ke fad'a tana hawaye Ganin yadda motar yake hantsilawa Fitowa tayi daga motar tana salati shima Fitowa yayi da sauran mutanen dake motarsa suka nufi nata motar Hankali a matuƙar tashe jama'a suka cika Gurin. Kafin su karasa ummi ta karasa tana kokarin ta bud'e murfin motan Amma ta kasa Dole sai da aka b'alle murfin motan gabad'aya fiskanta ya Rufe da Jini jikin ummi na rawa ta nuna motar tare da fashewa da kuka “Yanzun Jiddah ce Haka!" Jin Ance Jiddah ya Sashi Fitowa daga cikin jama'ar ya kutsa kai cikin motar , i'ta d'ince ba wata ba, da ƙyar ya fito da i'ta kaman daman jiran afitar da i'ta ake Nan take Motar ta Kama da wuta sauri-sauri gudu-gudu ya fara tafiya har ya karaso Gurin motarshi sakata yayi sannan ya kunna motar  bin bayanshi ummi

sukayi , Asibiti suka nufa da i'ta Amma k'ememe ank'i karb'anta wai sai an Kira police “Durun uwar police! nace kunci uwar,ku! daman ba ceton rai kukazo yi ba! Zaman Yan sanda kukazo yi wallahi in baku dubata ba, zan dakatar da asibitin Nan" Ganin yadda ya fita musu a giya yasa Dole suka karb'e ta sai dai Kash...

Maman Faruq
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: ♡SIRRIN ƊAUKAKA..!♡*

Farin Jini Writer's Association

Page 24

Sati biyu kafin ta farka fiskanta da suke tunanin zai Samu matsala yana nan sarai taji sauki sede ta samu karaya a hannunta na hagu, lokacin data farka shi kad'ai ne Gurinta sai Hanisa dake waje ummi Kuma taje Gida, domin tunda ya kawota asibitin yake Sintiri yaki ya mayar da Hankali gurin aikinsa Ummi ta mishi magana akan ya dakata da Zuwan Amma yaƙi A hankali ta bud'e idanunta haske ne taga ya mata Yawa mayarwa tayi da sauri ta rufe tana jan numfashi da karfi jin yadda Hannunta ke Zugi, da sauri yazo Gare ta cikin Tausayawa yace “Jiddatu Nah.." cikin wani i'rin Yanayi ya Kira sunan Wasu i'rin zafafan Hawaye ne ya shiga sauko mata Bata tsanmaci Ganinsa dai-dai wannan lokacin ba, Me ma yakawo shi gareta, me zai mata! Bayan duk ta silarshi Mijinta ya barta, a dalilinshi aka rabata da d'anta Ƙwaya d'aya tilo, yaron da take jin K'aunarshi fiye da komai Na duniya, bud'e idonta tayi fess saman fuskanshi “Me ya dawo dakai cikin Rayuwata? Nabil ka dena bibiyata na rok'e Ka, Dan Allah ka tafi.." ta fad'a tana nuna masa Hanyar Kofa. “Kiyi Hakuri bazan miki yadda kike so ba..!" murya cikr da kuka tace. “babu Alkhairi a tarayyar mu Nabil ka dubi Girman Allah ka tafi, Akan ka, Mijina ya barni, Akan ka, Ya rabani da 'Dana yaron da nake jin K'aunarshi fiye da kowa.." hannunta mai lafiya ya kama. "Allah zai bamu wasu ki nutsu mana Baki ganin Halin da kike ciki ne?" Ƙwace hannunta tayi “I'na ruwanka! Kai ko maza sun Kare bazan zauna inuwarka ba.." wani i'rin Kallo yake bin ta dashi cike da tarin mamaki kenan har yanzun Bata murdinsa shi yake Haukar banza , murmushi ya sakar mata koma ya Zatayi shi dai Yana K'aunarta Ganin taki yin shuru ya Sashi bin jikinta bakinta ya kama Yana sauke Numfashi a hankali,  runtsa idonta tayi da sauri tana dukan ƙirjinshi da ya tokareta wani i'rin bakon Yanayi take ji, bin ta, yake sosai yana Ƙara sakar mata jikinshi ƙasa ƙasa ta saka wani i'rin kukan da ya gigita masa lissafi da Sauri ya barta lokoci d'aya idanunsa ya sauya cikin tsananin bukatar son kasancewa da mace yace. “Kiyi Hakuri.." sannan ya fita motar shi ya shiga tare da kifa Kanshi saman sitiyarin Yana sauke Ajiyan zuciya Shi kad'ai yasan me yake ji game da i'ta, ya daɗe yana sauke numfashi kafin yabar asibitin, Yunƙurin tashi take amma ta kasa, jikita yamata nauyi, Hanisa data shigo ne, ta taimaka mata ta tashi zaune tana sauke ajiyan zuciya kallon ta tayi sosai, "Ya jikin?" cije laɓɓanta tayi sannan tace. "Da sauki wanka nake so" Hanisa tace "Bari ummi tazo zata san dabar da zatayi" Gyaɗa mata kai, kawai tayi.

Shuru suka zauna har ummi ta dawo, i'ta ta taimaka Mata tayi wanka tare da sauke sallolin

dake kanta.

A hankali lafiya ta fara samuwa Sir Nabil na musu hidima sosai domin jinyarta shi ya d'auki Nauyi, har yanzun Bata bashi fuskan da zai fukanceta ba ,da zaran ya bijiro Mata da bukatarshi Kaucewa take , bata jinshi a ranta Har suka dawo Gida Yana bibiyarta, bai i'ya zuwa Haka kawai ba, sai ya ciko mata leda da kayan siyayya Ko kallonshi batayi bare ta Karb'a Abin hannunsa , a Haka aka kwashe wata shida,  Zaune take a d'aki ta jingina da Gado tayi zurfi cikin tunani ummi ce ta shigo har ta zauna Bata San ta shigo ba, i'do ta ƙura mata.

“Hauwa zuwa yanzun ya kamata ki cire Batun Aakif tunda yace shi bazai baki d'anshi ba, kiyi hakuri, ki dawo da walwalarki , Gabaɗaya kin sauya  kin zab'i rayuwar d'aki fiye da komai , baki dogon magana,  kin Kori duk manimanki zaman ki Haka ya i'sa ,ya kamata ki duba Nabil yana da Nagartan da zaki soshi , shi mai K'aunar ki ne, bai kamata ki ringa masa i'rin wannan Wulaƙncin ba, kefa ba yarinya bace , kinsa abinda ya dace , bawai zan tilas miki lallai ki Aure shi bane , a'a shawara nake Baki, ba umurnin ba, bazan miki dole ba , inhar baki murdin zama dashi ki fad'a masa , ya dena b'atawa kanshi lokaci" murmushi tayi tare da Gyara zamanta. "Ummi Nah umurnin ki kawai nake jira nasan bazaki zab'amin abinda zanyi kuka ba, tunda har Nabil ya miki shi kenan..." Ta fad'a ranta na ƙuna. Kallonta ummi tayi sannan tayi murmushi.

“A'a zab'in ranki nake so kibi. ba nawa ba, banso na Cutar da zuciyarki.." katse ummi tayi. “ba Haka bane Ummi" daga Haka suka Rufe maganar shuru kwana biyu bai zo ba, duk da Ranan Karshe da ya zo Bayan tafiyarshi ya Kira Bata d'auka ba, domin bata bukatar Jin muryan shi , A hankali ta d'auki waya kaman zata kira shi sai Kuma ta basar tare da tura mishi “Uhmmm" rashin zuwan nasa ya dameta ko ba komai mai sonka yafi maƙiyin ka.

Yana can aiki ya mishi yawa shiyasa Bai samu damar zuwa ba, Amma tana maƙale cikin zuciyarshi ga fitinar Nuwairah domin tunda ya fad'a mata Aure zai ƙara ta kwance masa d'an kulawan da yake samu daga Gareta da, Yanzun baya samu domin hatta Girki sai dai yaje ya siya in Kuma yana Gida da kanshi yake Girkawa ,  saƙon ya duba yana sakin murmushi Aaliyah ce tayi Sallama tare da shigowa tana jan tsaki kallonta yayi Yana dariya “Keda wa Kuma?" Gabanshi taje ta tsaya tare da fashewa da Kuka “Dan Allah mai yasa kake Wulaƙantani? Kenan har yanzun baka K'aunata!" Hannunta ya kama tare da zaunar da i'ta jikinsa “Aaliyah.." kwantar da kanta tayi saman kafad'arshi tana shafa Fiskansa “i'na K'aunarka tamkar rai na Nabeel" da wani i'rin Yanayi ta kira sunanshi “Hmmm" yace mata Yana jin yadda take bin jikinshi “kace wani Abu Mana dan Allah" wani i'rin kuka tasa mishi tana dukan ƙirjinshi domin zuciyarta zafi yake mata in yana shareta Shine Mutum na farko data fara masa Soyayyar Aure shine Mutum na farko da ya tafi da zuciyarta matseta yayi sosai a jikinsa Yana sauke Numfashi had'e Fuskansu tayi tana kallon ƙwayar idonshi shima kallonta yake “Kiyi hakuri, kullun inna Baki hakuri Aaliyah Bazan i'ya Auren ki ba.." runtsa ido tayi da karfi domin maganar na dukan zuciyarta bakinshi ta lalaub'a cikin wani i'rin Mutuwar jiki ya biye mata nan suka shiga hargitsa junansu riganta ta cire ya shiga matsa Dukiyar fulaninta numfashi take saukewa akai² tana Kara tura mishi sosai ya b'ata lokacin shi a jikinta , domin shima Yana bukatar hakan, tunda Nuwairah ta watsar dashi gefe ,

Tana kwance yana samanta sai bin jikinta yake yana tsotsewa rik'e shi tayi sosai domin jikinta rawa yake “Dan Allah ka temaka min zan i'ya mutuwa" ta fad'a tare da d'aura hannunshi saman maranta mirginawa tayi ta koma samanshi murmushi ya sakar mata “Bazan tab'a aikatawa ba, zanyi komai dake Amma bazan ratsa Jikinki ba" ya fad'a Yana lasan tsakiyar nonuwanta "Ashhh.." tace tana Kara riƙe shi da ƙyar ya zame jikinshi Yana maida numfashi temakon shi d'aya yanada Banɗaki a Ofishin Yana cikin wanka ta shigo zata taɓa Jelarshi ya bige hannunta dariya tayi. “Akwai randa zanci kuma  na saka ihun dad'i" Bai kulata ba, Can ta sake maƙe murya tace. “Nabil ka Bari na tsotseshi ko zanji dad'i man” ta fad'a tare da shanmatar shi ta rik'e da sauri ya zabura Jin yadda take matse saman a hankali, numfashi yaja Yana kokarin tureta ta d'aura Harshenta tana lasan saman matse hannunta yayi sosai tana furzar da Numfashi duk yadda yaso kauce mata Amma sai da ta d'auke hankalinsa kai mace shaid'aniyace , na gaske sosai take tsotsar bananarsa dole sai da ta birkita masa lissafi wani i'rin zuk'owan da tayi ne yasa shi kawowa , Numfashi ya sauke tare da jingina da bango ba ƙariya yaji dad'i, wanka yay ya fita  fitowa i'tama tayi Bayan tayi waka ta sameshi ya gama shiryawa tsaye tayi Gabanshi tare da fad'in. "Kana ta basarwa baka ji dad'i bane? Ko Bai i'sheka bane na sake tsotsewa?" Murmusawa yayi. "Kinga banson fitina ki Shirya Jikinki"  wani i'rin narƙanƙen Kallo take masa tare da lashe lips ɗinta,  da sauri ya d'auke Kanshi

Shiryawa tayi tare da Kama hannunshi suka fita motarshi suka shiga har Gidan da take ya sauketa tare Bata kud'i Karb'a tayi tana juyawa tare da kallon shi “Na menene?"

"Hmmm"
Kallon Banza ta watsa mishi “Ban ciki da iskanci kud'in menene? inna tambayar ka?" Hannunta ya kama “Na baki ladan aikin..." Da sauri ta katse shi.. “Zuciyarka nake So! Ba dukiyarka ba, kasani sarai bana Yunwar Kud'i zuciyarka nake muradi ,Sir Nabil kai nake So har yau na kasa zama karkashin inuwar wani sabida Kai kad'ai ne a Raina, Da yawa Suna min kallon 'Yar mad'igo duk ta silarka da zuciyarka kawai zaka biya ni..." Kofar motar ya kalla tare da kallonta da sauri ta sauka  Bayan ta ajiye masa kud'in tana d'auke hawayen dake zubo mata “Allah ya tsare min Kai, ban tab'a Jin Zan rasaka ba, kullun ji nake na kusan mallakarka , Kamar yadda yanzun ma nake ji na kusan mallakarka Allah ya tsaremin kai da tsarewarsa" murmushi ya sakar mata sannan ya bar Gidan.

Maganar tada masa ne ya hanashi zama kallonta yayi cike da takaicin halinta “ka gama yawon ta zubar d'in ka gama laguda 'ya'yan mutane Nabil Amanata kake ci, da wata Banza kake had'a jiki..." Tsawa ya buga mata “Dakata Nuwairah!.."

“ƙariya ne? nace Ƙariya na maka dubi gaban rigarka Bayan yamutsewa harda Shedar Jan baki, Ka killace ni a Gida , Amma kai kana Nan kana..." Mari ya d'auketa dashi da sauri ya rik'e hannunshi yana kallonta cike da nadama domin bai tab'a Gangancin tab'a jikinta ba, i'do ta ƙura mishi tana kallon shi “Ka mareni Akan K'wajonka? yau ka tab'a jikin matar ka na Aure akan bazaurar da kuke aikata bad'ala , Ban tab'a zina ba, Nabil ban..." Wani i'rin kuka mai ciwo ta saka tana yarfe hannu "Ka mareni ? Ko ? Akan Karuwanka wanda ka kasa Hakuri ka Aurota insha Allahu sai Allah ya saukar maka da fitinar da yafi karfin ka ni ka daka.." Girgiza kai tayi tana hawaye juyawa tayi ta Nufi d'akinta tana kuka jiki a matukar sanyaye ya kalli rigarshi

Tabbas Ga alamar Nan, bin bayanta yayi ya sameta Zaune tana kuka "Nuwairah kiyi hakuri Wallahi ba da gangan Haka ta kasance ba" wani i'rin dariya tasa tana nuna shi "fitinanne Ka kasa hakuri kaje kana lalub'ar 'Yar mutane.." cikin fusata yace "sai me dan na Lalub'a? Da kina bani bazan kalli jikin wata ba, Yau komai na aika Nuwairah kece sila.." ihu tasa tare da dukan Shi a ƙirji "Haka ma zakace ko, ka fasa batun Auren muddin kana son zaman lafiya.." ta fad'a tana rik'e shi tunkud'eta yayi tare da fita. Haka ta zauna taci kukan ta. Kaman zata mutu domin fashewane kad'ai zuciyarta baiyi ba, Yau Nabil d'inta ne yake bibiyar Mace? (Ji Yar Banza waya bashi kofar bin Macen).

Yana i'dar da sallar i'sha ya shigo d'akinta yana Nan yanda ya barta “bakiyi sallah ba?" A harzuk'e tace "Kai nake ma sallar?"
“a a Uwargida saurautan mata Kinga Yunwa fa nake ji" ya fad'a Yana shafa cikinsa wani i'rin kuka tasa mishi “banyi abincin ba, bazan Kuma girka ba,kaje gurin Karuwanka ta baka" Bai ce Mata komai ba ya fita.

Tana Zaune a falo ya fito cikin Shirin fita miƙewa tayi tsaye tana binsa da kallo "i'na zakaje?" Kallon sama da K'asa yayi mata sannan yace “Zanje inda za'a tarairayeni ko kin manta da bakin ki, kika ce na tafi So meye abin tada jijiyar Wiya.."

"ƙalbi.." kallonta yayi tare da fad'in "Nuwaih Nah"

“Baka Sona ko?"

“Bayan Abbana da Innarmu na uku mama-Sadi kece na hud'u inna Ƙaunarki Nuwairah Halinki ne bana so.."

"To ka fasa fitar ji nake zuciyata kaman zai tarwatse zuciyana zafi yake min Dan Allah ka barta Muyi rayuwarmu, mu biyu kaji Yaya Nah?" Girgiza mata kai yayi cikin saukar da murya yace "inna K'aunarta sosai na azabtu Akan Sonta kiyi hakuri..." Zama tayi ragwajan cikin kujera tana kuka.

Kafad'arshi ya d'aga tare da fita , Gidan ummi ya nufa Yana zama a falo ya tura mata sako “Nawan tawo ina jiranki" tana Zaune saman Sallaya sakon shi ya shigo mikewa tayi daman tayi wanka da Himar d'in jikinta ta fito "Assalamu alaikum.." ta fad'a ƙasa ƙasa. d'agowa yayi Yana binta da kallon So, "Amin wa'alaikis Salam Zuciyar Nabil" zama tayi a d'ayar kujeran tana kallon Gefe tace "barka" tace a gajarce mikewa yayi daga inda yake yazo ya zauna kusa da i'ta tare da matsota jikinshi da sauri ta janye domin ji tayi kaman an jona Mata shocking , Hannunta ya kama “Barkan ki da zuwa tauraruwata Barka Muradi Nah Marhababiki Zuciyar Nabil Haske na, Abin Yabo na, tunani na, mafarki Na, Nutsuwata Sanyi Nah.." murmushin da Bata Shirya masa bane ya sub'uce Mata. A Hankali ta zame hannunta tare da fad'in „ka fiya zuba kaman Kanari”...

Maman Faruq
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: ♡SIRRIN ƊAUKAKA..!♡*

Murmushi ya sakar mata tare da matse hannunta lalubar ƙwayar i'donta yake Amma taƙi ta kalleshi, fiskanshi ya kai dai-dai nata yana fesa mata Numfashin sa a Hankali yake bin fiskanta yana sauk'e Ajiyan zuciya “wai maiyasa kake min haka ne? Wallahi banso Nabil ka dena Kunsantowa Gare ni" Kallon ƙwayar i'donta yayi tare da Lumshe nashi cikin wani i'rin Yanayi ya kwantar da kanshi saman kafad'arta be San abinda yake fisganshi ba, da zaran sun kasance su biyu susuce mata yake , in har bai rab'eta ba, ba ya Jin dad'i cike da mutuwar jiki i'tama ta zame shi daga Gareta Allah kad'ai yasan abinda take ji idan ya kusantota ɓoye ƙwallanta tayi “Kiyi hakuri dan Allah Hauwa ki amince min wallahi inna azabtuwa da yawa. ki tausaya min ki kawowa Zuciyata da rayuwata agaji, inna bukatar ki  kusa dani muddin muka ci gaba da , zama Haka wallahi shaiɗan zai shiga tsakaninmu, ni kaina bana sanin lokacin da nake kusanto ki.." ya ƙarasa maganar kaman zai fasa kuka miƙewa tayi domin zaman ya fara i'sarta  “Dan Allah" juyowa tayi ta kalle shi tare da Girgiza masa  kai "Wallahi bana jinka a raina Nabil bana son..." Kasa karasawa tayi, mikewa yayi shima “Shi kenan Nagode Jiddah" juyawa yayi jiki a sanyaye ya fita. Bai san wani i'rin zuciya ne da i'ta ba, jinginuwa yayi da motar sa tare da harɗe hannuwansa duka biyu a ƙirjinsa. Motar Mijin Halimatu ne ya shigo Gidan buɗe motar shi yayi zai shiga sai yaji Muryan Halima tana  cewa. “Sir Nabil Kaine Haka?" Murmushi yayi mata sannan yace "Maman biyu barka ai na ɗauka maigidan ne Ashe kece"

"Wallahi har ka gama da sahibata?" Sosa kanshi yayi sannan yace "Wannan sahibar  sai a hankali Bansan me na mata da Bata ƙaunata ba, Korana tayi"  Dariya Halimatu tayi "Karka damu kabar komai Gurina insha Allahu zan shawo maka Kanta" cike da zumuɗi da jin daɗi yace. "Nagode ƙwarai" daga Haka sukayi Sallama tashigo Cikin Gidan ɗakin Umminta ta nufa ..

Koda ta shiga ɗaki zaman tayi tare da rafka tagumi tana Tunaninsa bawai bata son sa bane , Gudun Kishiya take yi, Bata jin zata iya hakuri kaman baya hawaye ne ya sauko mata Har yau Bata samu Mai mata son da Nabil yake mata ba, "dole kiyi kuka ke kanki kinsan baki kyautawa Zuciyarki maiyasa kike gudun abinda zuciyarki take so? Har yau kina abu kaman wata  'Yar Ƙauye kina wani baya-baya dashi kaman ba wayayyiya ba, Bayan kinfi kowa sanin shine mai miki so na Haƙiƙa nifa shawara nake baki karki Cutar da kanki akan wani dalili mara tushe meye matsalarki da matar sa , kaman yadda take zama ƙarkashin sa , kema haka zaki zauna ,ba akanta zaki zauna ba,  Amincewar ki yake bukata in  kuma bazaki Aure shi ba, ki fito fili ki fad'a masa  ya daina zuwa kawai bawai kita Juya shi kaman waina ba,  haba Yanzun fa angirma akwai banbanci da Baya kina bani haushi Sahiba.."

Cikin yamutsa fuska tace "wa yace miki inna son sa?" Kama haɓa Halimatu tayi tana Mata kallon kanki kika raina , ƙasan filonta ta  ɗaya tare da d'auko Wayan da ya Bata tun baya har Yanzun hotonshi ne fiskan wayar Sunkuyar da kai tayi ƙasa tana mamakin ya'akyi tasan da wayar .

“A hakan ne baki sonsa ? Tun bayan rabuwarki da uncle Arab kike sauya waya da  duk wani

abinda kika San daga hannunsa ya fito kin b'atar dashi sabida ba ƙaunarsa kike ba, abinda kake so ne zaka tattala shi. Yanzun ba gashi ba, shekarawa nawa kina adana wannan wayar?"

Jiddah tace "Kinga nifa kawai banson Auren ne, inna da matsala banso na Cutar dashi dan wannan mannewar da yake min  ba hakuri zeyi ba.."

Cikin dariya Halimatu tace "Au Kice ɗan son ayi ne ? To aii hakan yafi Kyau,  Zaki karɓi yaren Novel yadda ya dace.."  Jidda tace "Kefa 'Yar iska ce, in baki furta ba Baki Jin daɗi ni bama wannan ba , ke bani da lafiya Hmm" kasa ƙarasawa tayi tare da juyar da kanta Gefe Wallahi kunyar ta faɗan damuwarta take ji,

"Rashin miji a kusa ma ai Babban rashin lafiya ne tunda Ba'a maka wuta-wuta kullun..." Hannu biyu Jiddah ta Kai mata duka "Allah ya shirya ki" Halimatu tace "Ashirye nake kumma kullun sai Abban Aaleen ya ƙara bani darusan masu zafi da tsuma zuciya shiyasa nake so kema ki shiga daga ciki"

"Mai ya kawoki Gidanmu a daren Nan?" Zama tayi bakin Gadon "Wallahi haka kawai naji inna son zuwa Naga sahibata"

Kwana Biyar Bai kirata ba, a ranar na shidan ne ran asabar Ummi ta sameta d'aki tana duba saƙon da aka turo mata. "Shalele tashi ki shiga kichin inna da baƙi" mikewa nayi tare da fad'in "Toh ummi na" Kichin na shiga inna cikin Aikin saiga Hanisa ba jimawa saiga Halimatu da iyalanta Nan muka fara aikin mu uku muna Hira,

Haka muka kammala komai ni dai kaina ya d'aure sosai domin muyi Girki kusan kala uku ga Fruit zoɓo kunnun Aya, da de sauran su, a falon baƙi muka jera komai muna shigowa d'aki nace "wai wani manyan bak'i ummin mu, Zatayi ake wannan hidimar kallon Halimatu Hanisa tayi tare da kwashewa da dariya "Allahu A'alamu" Halimatu tace. tsaki nayi domin na gaji sosai mikewa nayi naje nayi wanka, inna Fitowa Naga basa Nan d'akin ummi  nayi kasancewar inna fashin sallah  na kwanta i'tama Can najiyo Muryanta dasu Aaleen a hankali na ringa Jin magana sama-sama muryoyi daban daban , kasancewar d'akin nata na kusa da shashin baƙi.

Barci ne ya d'aukenibbanyi nisa ba naji muryan Hanisa tana cema ummi "Nifa Gida nayi Ummin mu, Allah ya Sanya Alkhairi abani Goron Abdul na kai masa"  Fitowa nayi nace  "in-law da wuri zaki tafi?" Murmushi tayi "Wallahi kuwa" kallona Ummi tayi Bayan fitar Hanisa Halima na kwance kan kujera "Ansa Nan da wata biyu" cikin rashin Fahimta nace "Me? Ummi" Halimatu tace "Auren ki da Sir Nabil man.."

"Hmm Allah ya kai rai" Ummi tace "Ameen" sannan ta bar Mana falon kaman daman jiran tafiyarta Halimatu keyi nan ta Sanya Gud'a "Allah ka kaimu musha biki wai... wayaga sahiba A Hannun maza za'a karɓan abinda  aka jima Ba'a Had'u ba" i'do na zuba mata tare da faɗin. "Shine kuka shammace ni? Bai sanar dani ba, yayi gaba gaɗi ko? Shi kenan"

Halimatu tace "bafa laifinsa bane Wallahi nida Hanisa mukayi wannan shawarar tunda  na lura

in aka bi naki ba Abin arziki za'a tsinana ba" shuru nayi inna kallonta Wallahi duk jikina a mace yake "Sahiba bani da lafiyan da zan sauke mishi Hak..." Zaburowa tayi "Ke me kika ce? Banji ba"

"inna fama da matsalan bushewar Gaba..." Halimatu tace "innalillahi wainna i'laihi rajioun tun yaushe Kenan?" Jiddah tace "Ya jima" hannunta Halimatu ta Kama har d'akin ummi gaban ta ta zaunar da i'ta kallon su Ummi tayi "Me Kuma ya faru?" Cikin tak'aicin Halina Halimatu ta fara magana "Gata ummi ta fad'a miki da bakinta bansan wani i'rin Zurfin ciki bane da i'ta kana da ciwo Amma kayi shuru Abu na cin jikin ka" shuru ummi tayi tana sauraron Halimatu sai da ta Gama sannan tace min "Jiddah meke damunki?" Sunkuyar da kaina nayi K'asa na kasa ce mata komai so Biyu tana magana Ganin naƙi Bata amsa ne yasa Ummi maida kallonta zuwa ga Halima "Tunda taki magana ai saiki sanar mun"

Kallonta Ummi tayi a tsanake Bayan ta Gama Jin abinda ke faruwa "To Allah ya shirye ki Hauwa'u ubangiji ya sauƙaƙa miki wannan halin naki na Zurfin ciki"

"Dan Allah Ummi kiyi hakuri wallahi kunya nake ji Bansan yadda zan fiskance ki da wannan maganar ba" shuru ummi tayi tare da kallon Gefe zuwa can ta fara magana.

"I'dan mu kace ni'ima to muna magana ne akan sha'awa waton libido a Turance kenan.Tana taruwa ne ga matan da suka balaga masu koshin lafiya walau budurwaye ko kuma masu aure.

Sha'awa halittace wacce ta banbanta daga wata mace zuwa wata.
A lokacinda mace take jin sha'awa haka kawai ko sanda take karanta wani labari ko tinanin wani abu dake motsa shawa ko a yayin da ake gabatarda wasanni (fore play) kamin saduwa to idan dai har tana da ni'ima to zata ji duk ta jike dan wasu fararen ruwane masu yauqi zasu rinka fito mata ,A lokacin ta riga ta kamu kenan wannan ne ake kira Natural lubrication ko Vaginal wet (Ayi hakuri turancin ya shigo)  wanda idan har za a sadu da ita a lokacin to a shirye take, A hakika shima mai gidan zai yi matukar gamsuwa da ita Ba zata ji zafi ko ciwo ba, saboda ta jika sosai ta yadda bata bukatar ayi amfani da wani vaseline ko ointment,

To wadannan ruwan masu yauqin
dake fitowa mace a sanda sha'awarta ta motsa to ita ke nuna alamun tana da ni'ima,Wasu matan sun fi wasu yawan sha'awa da samun ni'imar jiki dan yanayin halitta da lafiya,dama abincin da suke ci  ya sha banban.

Wasu matan tun azal suna da ni'ima mai tarin gaske.Amma daga baya takan gushe sai su rasa sanin dalili ,Hakan zai sa su tsunduma suyi ta neman kayan mata suna cusawa kansu abubuwa masu cutarwa duk da sunan ni'imarsu ta dawo,matsaloli da dama kan faru a sanadin haka , Akwai matsaloli da rashin lafiyoyi da dama dake haifarda gushewar  ni'ima ga mata wad'anda suke bukatar bincike a maimakon haka mata da dama sukan yanke hukuncin cewa ai ciwon sanyi ne ke gare su alhali wata matsala ce ta daban,

Akwai matan da basu da ni'ima a koyaushe gabansu a bushe yake ba wata ni'ima ko jin

sha'awa ,wasu matan sai sun shafa vaseline kamin a iya saduwa dasu, Hakan. kan haifar da rashin samun gamsuwa musamman ga maigidan.

Cushe cushen da mata ke yi da sunan matsi yana daya daga cikin abinda ke zuqe ni'imar mace ya haifar mata da bushewar gaba misali amfani da ruwan bagaruwa wacce tana matse fata amma kuma tana zuqe daushin dake ga wuri gaban mace zai matse amma kuma zai kasance a bushe.To miye fa'idar yin haka kenan ?.
Maigida na saduwa dake amma yana jin kamar ana zoza mashi katako.
wasu cushe cushen , na haifar da cuttukan gaba da kuraje da kaikayin gaba , da irin wani warin, Dan an d'auki wani abun na daban an tura a inda bai dace ba.

Akwai magani Natural fruits da
mata zasu iya rinka amfani dasu dan su karawa kansu sha'awa da ni'ima kai harda , koshin lafiya.
Kamarsu , kankana ,ayaba gwanda
abarba, lemu, timatir rake, dabino, kwakwa, dafaffiyar Gyad'a, zuma,nono,zogale rid'i ,cukwi enibi, tuffa, zaitun, tafarnuwa, albasa, rid'i.

Wallahi wadannan duka sun fi duk wani cushe cushe ko kayan sha na mata da kuke gani amfani da kuma saukin saye.

Zaki iya cin ayaba da dabino a yau.
Gobe sai ki canza ki nemi kankana ki sha,a jibi ki nemi dafaffiyar gyada ki ci,gata ki nemi zogale da albasa da quli quli kiyi d'atu ki ci sai ki ringa canzawa lokaci zuwa lokaci.
Wallahi ina baki tabbaci idan kika fake da hak'an to bawai ni'ima ba ko lafiya da fatar jikinki zaki gan tana canzawa.
Amma an rungumi kayan maiqo da kayan zaqi da kayan yaji kawai ake ci dare da rana ana ta faman shan kayan mata da cushe cushe amma a banza dan ba sune abinda jiki keda bukata dasu ba ai dole sha'awa ta ja baya.

Haka kuma zaki iya had'a wad'annan dan karin ni'ima da gamsarda mai gidanki.

Amma akoi bukatar a kiyaye da tsabta mata a daina cusa duk wani magani a cikin gaba wannan baya da wata fa'ida asali illoli ke gare shi.
A ringa tsarki da ruwan d'umi ,

A daina sanya pant da bai bushe ba I'dan an wanke to a ringa shanyawa har sai ya bushe.

Ga wannan had'in da zan Miki insha Allahu za'a dace" da sauri Halimatu tace "Ummina fad'a naji domin gaba" hararanta ummi tayi sannan tace.
"Za a iya d'aukar d'aya ko biyu daga ciki ayi amfani dasu

Qwai da albasa da timatir sai a soya amma kada a bari suyar ta kone Banda sanya maggi da gishiri da yawa zaki iya sakawa amma d'an kad'an ake so.

Namiji zai iya ci hakan zai kara mashi  yawan ruwan maniyi.

Za a iya neman garin dabino da ruwan kwakwa sai a dama a rinka shan cokali biyu manya safe da yamma.

Ki nemi tantabara ki saka tafarnuwa da daddawa kiyi romo kina sha.

A nemi nonon rakumi sai a saka rid'i a dama sai yayi kauri sai a  rinka sha.

Ki tafasa ruwan zogale ki zuba kanumfari da citta sai ki tafasa ki sauke ki ringa kurb'awa kad'an kad'an kamar shayi" K'anta na K'asa Halimatu tace "Kai Masha Allah ummi Kinga da yawan jama'a zasu Amfana dashi tunda gashi a saukak'e Abubuwan zaka Nima ka had'a Allah ya Kara miki ilimi da nisan Kwana uwata abin Adona"

Ummi tace. "Tashi ki tafi Gida Yamma yayi" Halimatu tace "Ummi har kin gaji da gani na? Ni daman inna son kayan Gyaran Aure nasan zaki haukata sahiba da ingantattun kaya , kar a manta dani da Hanisa..." Maficin dake gefenta ta jefeta dashi "Halimatu sannu kinji Allah ya yaye miki" mikewa tayi tana dariya "Ameen Ummina Bari na mu tafi sai Bayan kwana biyu kuma  Amariya  a daure a dena share min Suruki , a ringa Kula shi" Ni Wallahi duk kunya ta kamani Halimatu ko a jikinta ,

d'akina na wuce na d'auki wayata Na Kira layin shi Amma a kashe yake , tsaki nayi tare da yaye labulen windon inna kallon waje , sannu a hankali komai yake tafiya yayin da ummi take tsuma d'iyarta da ingantattun i'tatuwa ga mayukan Gyaran jiki data had'a mata wadda yasa jikinta Kara murjewa Yana laushi da bulb'e tayi haske Masha Allah tana Nan killace a d'aki Bata fita ko'ina.. kullun tana  makale  jikin  window kunnuwanta bud'e yake ko zata Ganshi ko taji dirin motarsa Amma shuru tana kewarsa sosai kullun Yana mak'ale cikin Zuciyarta.

★★★

Lokaci d'aya Nuwairah ta d'aga mishi hankali ganin lallai da gaske Auren zaiyi yasa ta tattara ba tare da sanin shi ba ta nufi Chadi ya dawo Gida bai Ganta ba dole shima ya shirya tafiya ba shiri inda yaje ya tadda ta shirya ma iyayensu Kariya da Gaskiya , fad'a aka mishi sosai Bai ce komai ba kwana biyu da zuwanshi ya kai ma Mama-Sadin maganar Auren shi bata hanashi ba, saima tara yaranta da tayi ta musu Nasiha akan su barshi ya Auro zab'in ransa Mahaifin sa bai so ba, Amma dole yabi umurnin ta, daga Nan Chadi suka tura jama'ar su zuwa Nigeria  sun dawo musu da labari mai dad'i na tarban Arziki da aka musu musammam girke-girken da aka musu abin ya musu dad'i Sosai duk wannan abin da akeyi Nuwairah Bata sani ba, domin tana Gidan Matar Yayanta can ta tare , lokacin da ta dawo taga yana had'a kaya a sabbin akwatunane ta kalle shi tare da kallon Kayan "menene wannan Nabil ?" Tura mata akwatuna biyu yayi Gabanta "Kayan Jiddah nake had'awa ga naki kayan..."

"Nabil bazaka Janye maganar Auren Nan ba? Mena rage ka dashi da har wannan kod'add'iyar Yarinyar take manne da kai duk iskanci da kuka yi Bai i'sa ba..." Kallo mai kyau ya Mata sannan ya d'auke Kanshi fita tayi ta nufi shashin Maman-sadin zubewa tayi Gabanta "Mama na hanashi

Auren yaƙi dan darajan ma'aki ki hanashi Wallahi inna ƙaunar mijina bazan juri Ganin yana rab'an wata macen ba.." Nabil dake bayanta yace "Nuwairah hakuri zakiyi" kuka tasa tare da Kallon Mama-Sadi "Wallahi bazan yarda ba baze ma Wuyu ba, ni Wallahi bazan lamunta ba..." kallon shi Mama-Sadin tayi sannan tace "Zauna kema ki min shuru" kuka ta Kara fashewa dashi "Taya zanyi shuru Bayan Kuna d'aure mishi Gindi yayi abinda Ransa ya masa kun ware ni Daman ba ƙaunata kike ba..." Hannu ya ɗaga da niyar marinta Kakarshi ta daka mishi tsawa Dole ya Kyale tare da Sunkuyar da kanshi Kasa A Hankali ta fara mata Nasiha cikin tattausan lafazi.

"Haramun ne mace ta hana mijinta ƙarin aure, saboda aure umurnin UBANGIJI ne a qur'ani Mai girma, matukar namiji zai iya adalci, yana da lafiya, da kuma wadata.

Domin hana shi ɗin Yana daga cikin saɓawa umurnin ALLAH, a matsayin ki , kuma mace musulmah ta sani ko ta tuna faɗin ALLAH da yace'; kuyi taimakekeniya akan ɗa'a ga umurnin ALLAH da kuma takawa.

Hana masa karin aure kan iya jefa shi cikin wani hali na alfahsha daban daban, wanda hakan za ta iya samun zunubi itama domin da gudummawar ta ciki, bayan zunubi kuma za ta samu nakasu a rayuwa ko na cuta, ko baƙin ciki da damuwa ko rashin daɗin zaman su gabadaya.

Abu mafi kyawu da ake so ga mace in MIJIN ta na son Kara aure shine ta taya shi da addu'a da yi masa nuni ya nemo mace ta gari yar gidan tarbiyya kuma ita ma ta taya shi da addu'a, domin kwanciyar hankalin sa na ta ne kuma aure ana yi ne don samun kwanciyar hankali da morewa jindaɗi duniya da kuma biyayya ga ALLAH.

Kishi gaskiya ce, amma tayi koyi Da matan Manzon ALLAH s.a.w, da matan Sahabbai, da matan salihai bayin ALLAH na Ƙwarai.

Kuma kiyi tunani mai kyau wasu mazan sai dai suyi ta neman mata. ba su tunanin kara aure, ke naki yayi tunani ƙarin auren sa ,mutuncin ki ne da na ya'yan ki, yau ace ga mijin ki MANEMI mata uban ya'yan ki wadda a kullun nake Burin Ganin Yaranku da Addarku Asma'u kafin Ubangiji ya d'auki Numfashina akwai kyau? Ai abu mafi kyawu cikin duniya da lahira ace mijin ki yana da ku matan sa halaliya biyu ko uku ko huɗu, bare kuma mata Masu fad'in da kishiyar gida gwara na waje' wa'ennan matan su kam sun taɓe sunyi hasara muna yiwa dukkan Musulmi ALLAH yayi masa tsari da auren wa'ennan , irin matan su kaman taimakon mijin su suke akan alfahsha yaje yayi tayi, wato su dai a gida da cin gado ya zamo su kaɗai ne, wannan irin matan babu alkhairi zama tare da su.

Mace mai Ƙaunar ka ba za ta taɓa son ganin ka cikin alfahsha ba, mace mai hankali ba za ta taɓa yarda uban ya'yan ta ya zamo mazinaci ba, sai dai ma in ta fahimci yana yi tayi ƙoƙarin dai-daita shi ta hane shi da addu'a ta taimake shi ta masa NASIHA da ya ƙara aure.

Abinda ke faruwa a yanzu dayawa ba soyayya ake don ALLAH ba sai don abin duniya da sha'awa ƙyale ƙyale, shi ya janyo wannan ba ruwan mace da lahirar mijin ta, ita dai kawai koma

menene yaje ya aikata matukar buƙatar ta za ta biya kiyi hakuri Nuwairah ki barshi ya kara Auren tunda yana so" mikewa tayi tsaye "Shi Kenan ba Auren ta za kayi ba? Kaje kayi Kuma Wallahi sai dai ka sake ni bazai Yuwa na zauna da Wata Banza ba" fita tayi.

Kallon shi Mama-Sadin tayi sannan tace "Ƙyaleta kishi da shed'an suke d'awainiya da i'ta ka shirya ka koma ka barta Nan i'tama Hauwa'u Nan zata zauna duk ka had'e su Guri d'aya lokaci yayi da kaima ya kamata ka nutsu Guri d'aya kaman yadda mahaifinka ya dawo , Kaima a jiye musu Aikin su, ka dawo Nan Asma'u in da rabon mu gana zata Zo gareni tashi ka tafi" mikewa yayi cikin Mutuwar jiki ya fita bai koma shashensu ba , ya Nufi b'angaren Mahaifiyar shi, i'tama Nasiha ta masa watsar da Nuwairah yayi a Gefe in tana fad'e Fad'enta , ba ya kullata balle ta zageshi , Ana saura sati bikin ya tawo Nigeria inda ya had'u da sabon damuwa domin Aaliyah taji labarin Aure zaiyi Domin 'Yan lek'en asirinta ne suka kawo Mata rahoto hatta wacce zai Aura sun sanar Mata, inda tayi tsalle ta dire tace ayi Auren ta Gani yana sauka a Mota ga motar ta ya shigo a Guje tana Fitowa ta watsa mishi kallon Banza.

Maman Faruq
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: ♡SIRRIN ƊAUKAKA..!♡*

Farin Jini Writer's Association

_Ku daure kuje ku dangwala min subscribe d'in Channel d'ina , mai Suna FARIN JINI HAUSA TV. Ku nuna min k'auna zaku ringa samun littafan mu audio_
.....26
Kallonta shima yake yana sakin murmushi Aaliyah ta zame mishi ƙarfen ƙafa “Meyasa kake Yaudaran zuciyata Nabil...?" Numfashin ta ya tara “dakata malama karki d'oramin kayan kwalba, ke kike Yaudaran zuciyarki Tun farko na fad'a miki Aaliyah baso d'aya ba, ba so biyu ba...“Abinda zaka CE kenan? Wai me na maka ne Haka daka tsaneni? Haba Sir kaji Tausayi na ka tuna Girman so , Wallahi bazan i'ya barin ka ba.." hannu ya d'aga mata "Kinga banson surutu banson damuwa Aaliyah ki tafi dan Allah" share hawayenta tayi "Shi kenan" motar ta taja tare da barin Gurin a guje Girgiza kai yayi tare da shigewa cikin Gidan ya shirya da Yamma ya Nufo Gidan Ummi A waje ya ci karo da Halimatu zata koma Gida "a a yau a gari Sirikina?" Cikin zolaya ta fadi Haka. “wallahi Hali-dubu Bari kawai nayi ƙoƙarin dawowa da wuri Allah baiyi ba, da fatan na sameku lafiya?" Halimatu tace "Alhamdulillah yaka baro mutanen Chadi?"
“Kowa lafiya ya Amariyata?" Halimatu tace "tana nan kalau, zakaje ka tadda rigima domin a cike take fam" ware i'do yayi tare da fad'in “Ai nayi laifi dole na bada Hakuri" Jakar r da ya zomata dashi ne ya baiwa Halimatu ta kaimata "Daman baki tafi ba?" Tace a dai-dai lokacin da take shirin kwanciya "Yanzun dai zan wuce gashi Sir Nabil ne ya dawo dan Allah sahiba tashi na miki kwalliya" kallon Halimatu tayi sosai sannan tace "tashi ki tafi abinki Wallahi ba kwalliyar da zanyi" Halimatu zata sake magana Jiddah ta nuna mata hanyar waje cikin ɓacin rai ta fita. shashin Ummi ya fara zuwa suka gaisa kafin ya dawo Falon ya zauna Fitowa tayi sanye da ƙaton himar kichin ta nufa ta d'auko mishi kunnun Aya tare da saka cofi sannan ta dawo Gurin "Assalamu alaikum" wani i'rin wawan Ajiyan zuciya ya sauke tare da hamsa sallamar Yana bin

ta da kallo ganin yanda ta sake haske ga fiskanta sai ƙyalli yake ƙamshin jikinta ne ya Sanya mishi Kasala.
Ajiye kayan tayi tare da zuba mishi miƙa mishi tayi Amma yaƙi amsa sai kallonta yake cikin wani irin Yanayi, ce masa tayi "Hmmm Kallon fa? Sai kace Yau ka fara gani na , Mallam.." lumshe i'do yayi tare da jan wani i'rin numfashi tana durkushe a Gabanshi hannu ya kai ya harɓi kofin tare da haɗawa da hannunta ya riƙe Hasbunallahu yace lokacin da yaji lallausar hannunta kaman audiga zamewa tayi domin muddin yaci gaba da Riƙe za'a samu matsala Zama tayi kusa dashi a hankali ta fara mishi magana "Nabil shine kayi gaban kanka batare da ka nemi shawarata ba, ku ka Rufe ni?.." ajiye kofin yayi Bayan ya gama sha. "Gani nayi inna ta bin ki kina kaucemin shiyasa nayi hakan Amma kiyi hakuri , Zuciya tace ta kasa zurewa baki San yanda nake ji game dake bane" shuru tayi tare da ƙura masa idanuwa mikewa tayi a hankali domin ji tayi Bazata i'ya zaman ba, wani abu ne yake fisganta a hankali shima ya miƙe tare da kamota ya had'eta da jikin Bango domin muddin ya barta Haka Tasha dashi juyar da kanta tayi Gefe tana jan tsaki ta lura baya i'ya saita nutsuwarshi muddin ya kusanto gareta "Kaga banson iskanci Meye Haka?" Juyo da fiskanta yayi Yana kallon ƙwayar i'donta "Somin tab'i ne domin wani abun sai Nan da kwana shida.." zata tureshi ya Kama hannunta tare da matsewa , nashi fiskanshi ya d'ora saman nata yana fesa mata Numfashinsa mugum Kasala ne ya sauko mata lokacin d'aya riƙeshi tayi "Dan Allah banso ka dena" Yi yayi kaman baiji abinda tace masa ba , bakinshi ya d'ora saman nata tare da fito da harshen shi yana lasan laɓɓanta wani i'rin numfashi ta sauke tare da runtsa i'do a hankali jikinta ya fara rawa sosai yake zagaye saman bakinta tare da laluɓar jikinta Amma taki barinsa haɗe bakinsu yayi Yana Mata wani i'rin tsotsa mai tafiyar da zuciyar mutum riƙe shi tayi Gam tare da fashewa da kuka jikinta na rawa kara riƙeta shima yayi sosai Yana shafa bayanta tsotsar bakinta yaci gaba dayi tana sauke numfashi kaman wanda ya samu minti Haka yake ji, zamewa tayi tare da zama a ƙasa tana sauke numfashi ga hawayenta da yake zuba fita yayi a Gidan Gabdy domin muddin yace zai sake tsayuwa shed'an zaiyi gabala akan shi, ya aikata abinda ba haka ba, da ƙyar ta lallaɓa ta tashi Band'aki ta shiga tare da yin wanka domin a jiƙe take tana kwance Ummi ta shigo da ƙwariya wanda yake cike da dafaffiyar Madara sai ƙamshin kanunfari yake yi tashi nayi zaune na Karb'a sai da taga na shanye kafin ta fita domin muddin ta ajiye tace nasha bana yarda in Sha sai dai in barshi a firiza in Halimatu ko Hanisa sunzo suke Sha , to dataga dai bani ke shanshin bane , yasa take zama saina shanye zata fita , a hankali Gidan ya fara Cika da jama'a hatta Zaliha Autarsu ummi ma wannan karon tazo domin muna zumunci sosai da i'ta tun Ranan da ya matseni ban sake yarda mun zauna na minti Biyar ba, domin lamarinsa tsoro yake ban Nabil bai i'ya zama shuru ba, sai ya lalub'e Albarkan jikina ,  ga wani ciwon kai , b'ari d'aya dake damuna ban cika barci da dare ba, sabida zazzab'in dake yawan takura min , Ana Gobe d'aurin Aure inna kwance Da safe Halimatu ce ta shigo da kibiya  a hannunta "Tashi sahiba Muyi kitso tun jiya nake binki Amma sai kaucewa kike" Cikin Mutuwar jiki nace "Ki bar wannan kitson domin Wallahi kaina ciwo yake min jikina duk a mace yake.." Dukan wasa ta kaimin "Dalla tashi duk wannan k'ananun ciwon na rashin Sir Nabil ne,nasan da zaran ya baki wannan yaren Novel d'in zaki Tashi Garau..." Mikewa nayi zaune "Amma ke kan Allah ya shiryi bakin ki" Haka na zauna tana min tsiya ta yarfa min kananun kitso ana kammala kitson ta shiga zana min lalle hannuna da lalle Kira ya shigo wayata "Haske Nah" abinda Aunty Zaliha dake zaune kusa dani tace kenan cike da Kunya na juyar da kaina ..

"d'auki kiran man?" Girgiza mata kai nayi batare da nayi magana ba, "Ana so ana kaiwa Kasuwa gwara ma ki aje wanna Kunyar Anan kishiya Gare ki, kije kina wani ƙunbuya-ƙunbuya kina basar dashi Wallahi in Nuwairah ta san ba jansa kike a jikiba , zata riƙe Kayanta i'ta Kad'ai gwara ma ki saki zuciya da jikinki domin wannan Kunyar taki zaisa ki Cutar dashi.." inna jinta ta Gama fad'e Fad'enta tare da zaro magana Fadila dake kwance tana dariya domin tun wancan lokacin muka d'inke da Zumunci cewa tayi "Wallahi Aunti ki fad'a mata dai , don na lura Sarai da take taken ta, mude in za'a wassake daga Cutar Ƙariya ma a tashi domin Gobe za'a Karb'i Abin Nan de wadda aka dad'e ba'a jin shiganshi ba" kai innalillahi Wallahi Basu jin Kunya Haka suka ringa sakin zance bance musu kala ba, Haka suka Gama Zancen su sai da lallena ya bushe na wank'e sannan na kira wayarshi "Amariyata inna aka makale min ke ne tun d'azun nake son zuwa Ganin ki, domin nayi kewar wannan karamin bakin.." murmushi nayi tare da fad'in "Uhmm Allah ya shirya ka" Gyara zaman shi yayi tare da marerece mata "Dan Allah inzo ba abinda zanyi illa ganinki" da sauri nace "a a yi zamanka.."

Kashe wayar yayi yana murmushi , bade gobe zaki zama mallakina ba, ai baki isa ki hanani ganinki sosai ba,

Bin wayar tayi da kallo tana lumshe ido haka kawai inna Zaune lafiya kazo ka fitine ni, Sallar magariba a ka kira Fadila ce ta Shigo kallonta nayi dai-dai lokacin da nake shirin shiga band'aki "Bade tafiya zakiyi ba?" Nace inna kallonta "Nabar Love a Gida tun safe ai dole na koma tunda Kinga mun Kammala Cincin d'in.."
"Dalilai masu yawa da ƙwararan hujjoji Ashe kai fasiƙi ne ban sani..." ɗauke ta yayi da mari cikin ɓacin rai yace "Karki yarda..."
"Dakata Nabil ai ba ƙariya tayi ba" Juyowa yayi yana kallon Nuwairah dake bayanshi ta harɗe hannuwa tana kallonsu "Ƙwarai kuwa kuma kin min dai-dai da kika masa wannan hukuncin Duk

wasu abubuwan da kake aikatawa kallonka kawai nake, munsha fita da Jiddah tana ganin Motar ka, Amma saina ƙaryatata saboda bana so wani matsala ya shiga tsakaninku last fitan da mukayi wanda kace zaka kaimu shopping daga baya kaƙi amma a shop mall ɗin na ganka da Farkanka...”
“Ya isa!”
“Meye abin jin Zafi anan? Gaskiyace kasan da zafi kake aikatawa? Baka san mutumcin mu dana iyayenmu kake zubarwa ba? Why Nabil? Ka ɗauki ƙazamin riga ka sanyawa kanka wai kai ne da ajiye Karuwa a waje..” runtsa ido Jiddah tayi da ƙarfi tare da fashewa da Kuka me sauti ƙarasowa Gurinta Nuwairah tayi tana lallashin ta “Haba Aunty Nuwairah maiyasa tun farko kika rufe Ni? Bai yasa baki fayyace min Halin Mijin da nake Aure ba? Yanzun a haka zamuci gaba da rayuwa da Miji irin sa? Gaskiya bazan iya ba! Wallahi bazan iya cigaba da zama da Nabil cikin wannan ƙazamin rayuwar daya jefa kanshi ba” Kallon Dr dake koro mishi bayanin sallama yayi tare da duban takardan Ganin an biya komai ne yasa shi kallonta “Waye ya kawo ki asibiti? Meya sameki? Wa ya biya kuɗin?”
“Me kuwa zai kawo ni asibiti bayan baƙin ciki da takaicin Ɗa Namiji, akan meyasa kake tuhumata da tambayar waye ya kawo ni asibiti Kana can tare da Karuwanka kana sheƙe ayar ka meyasa Nima bazan fita in shaƙi iska ba....” a zabure ya matso yana shirin Marinta Nuwairah ta riƙe mishi Hannu tana faɗin “Dalla can dubi yanda kake ta wani ɗaga jijiyar wuya, dan kawai ta faɗa maka abinda ba haka bane”
“Da kin ƙyale shi, kayi abinda ranka ya maka amma Zamana da kai ya ƙare bazan iya zama da ƙazami irinka ba”
“Kinga Jiddah ya isa haka tashi muje gida tunda an sallameki”
“Babu inda za'a tafi har sai ta faɗa min uban daya biya kuɗin Asibitin nan!”
“Au haba? To ko zargina kake saboda kana da Karuwa a waje nima kana zargin zanyi abinda kake aikatawa ne?”

_Afuwan bana jin daɗi ne_

Maman Faruq
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: ♡SIRRIN ƊAUKAKA..!♡*

®AYSHA  JB

FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION

*Wannan page ɗin naku ne, AYSHA JB CLUB tare da Wattpad Fan's Much Love Guys🥰😍 kuyi yanda kuke so dashi..*
34Shuru kawai Nuwairah tayi tana kallon yanda suke cacar baki, ba irin haƙurin da bata basu ba amma Ina koma zuciyarshi yai sama Cikin gajiyawa da haniyarsu ta ɗauki wayanta tana faɗin. “Tunda bakwa jin haƙuri bari na kira Gida wataƙil in suka zo zaku ƙyale wannan maganar” ta ƙarasa maganar tare da kai wayan kunninta karɓe wayan yayi tare da jan ƙwafa ya fita waje kallon Jiddah tayi tare da ɗaukan jakarta dake gefe sannan tace. “Oya Malama zaki tashi ne ko nayi tafiyata dan naga ke da mijin naki kun ɗau zafi sosai in Kuma daga nan akwai inda zaki tafi

ne sai ki sanar min" Saukowa Jiddah tayi daga gadon tare da saka takalmin suka fito motan Nuwairah ta shiga suka nufo gida dai-dai ana kiran Sallar magariba ɗaki Jiddah ta nufa tayi alaula tare da sauke sallolin dake kanta, Nuwairah ce ta shigo mata da jakanta tare da magungunan da aka bata a asibiti Abincin dake kitchen ɗin ta ɗumama tare da kawo ma jiddah tana idar da Sallah ta koma bayi tayi wanka riga mara nauyi ta saka sannan ta tsakuri Abincin kana tasha magani lumshe ido tayi tana jin yanda kanta gefe ɗaya ke sarawa shigowa yayi tare da tsayuwa yana ƙare mata kallo, ko ɗagowa batayi balle tace mishi wani abu, "lokaci na ƙarshe kenan da zan sake tambayan abinda ya kaiki asibiti da ɗan iskan daya biya miki kuɗi" buɗe jajayen idanunta tayi tare da watsawa cikin nashi kallon ƙwayar idonshi tayi sosai kafin ta ɗauke kanta, miƙewa tayi tana shirin fita yasa mata ƙafa ta faɗi, zata tashi ya sake danneta "Wacece ke da zan miki magana kisa kai ki wuce ba tare da kin bani amsata ba..?" cikin wani irin ƙarfin hali tasa duka hannunta biyu ta tureshi, wanda sai da ya buga ƙeyarshi da bango, motsin da tayi da ƙarfi ne yasa hannun da akayi mata ƙarin ruwa ya fara fitar da jini, nuna shi tayi da yatsa cikin ɓacin rai tana faɗin "Karka yarda ka ƙara taɓa tsaftataccen jikina da ƙazamin hannunka.." miƙewa Yayi da sauri yana shirin kamota fita tayi da sauri dan ta lura muddin ta tsaya zai iya illatata domin wani ƙazamin kishi take hangowa a idanunsa, a main falo ta dakata tana kallon yanda suka tsaya cirko cirko har Mahaifiyar Nuwairah "Meke faruwa anan? Kai Nabil meka zaburo kake shirin yi? tun ɗazun kun cika mana gida da hayaniya, ke Jiddah Ina kika je tun safe? Meya kai ki asibiti?" Mahaifinsa ne ya jero musu wannan tamabayoyin yana jiran Su bashi amsa Kallon Jiddah Nuwairah tayi sannan ta juyo tana kallon Nabil wanda ya ɗauke wuta yana jiran abinda Jiddah zatace tuni zuciyarshi ya fara lugude ga zufan rashin gaskiya dake karyo masa Buɗe baki Nuwairah tayi zatayi musu bayani ganin haka yasa Jiddah taran numfashinta gurin faɗin "Abba bafa wani abun ɗaga Hankali bane, zazzaɓi ne ya tare ni shine nayi saurin zuwa Asibiti.." Kallon Nabil Inna tayi tare da faɗin "Kai kuma Meye kake binta kaman zaka daketa?" da sauri Jiddah tace "Bafa wani abu bane, daman hannuna dana fama ne yake ta bina in tsaya ya gani shine nake gudu..." fita sukayi ya saura su uku kallon Jiddah Nuwairah take cike da mamaki ganin yanda ta rufa mishi asiri ba tare da ta faɗi ainihin abinda ya faru ba, "Allah ya ƙwace ka dan wallahi da nice aka tambaya bazan taɓa rufa maka asiri ba, kana da daman da zaka gyara kuskuren ka kafin lokaci ya ƙure maka" kallon Jiddah tayi tana cigaba da faɗin "Kinyi Abu ne kyau da kika rufawa mijinki asiri lallai ba ko wacce mace bace zatayi abunda kikayi Allah ya tashemu lafiya dan Allah ki ƙara Haƙuri akan na da"

Ɗaki Jiddah ta koma tana shirin kwanciya ya zauna yana faɗin "Hmmm tunda abun haka ne ina ga zan ƙara Aure.." Ɗan Murmushin takaici da ɓakin ciki tayi tana tunanin anya kuwa wannan Nabil ɗinta ne kuwa? Anya ba sauya mata shi akayi ba domin ta lura Gbɗy baya ma cikin Nutsuwa bare ayi tunanin Hankali tattare dashi "Allah ya bada sa'a" daga haka tayi shuru tana tunanin wacece i'ta da har mijinta ya manne mata yake kuma iƙirarin cewa zai Aure ta? Humm koma wacece bazata barta haka ba, tunda Har Nabil ya fara taɓa lafiyan jikinta da sunan Duka Wallahi sai ta Nimo ko wacece Yarinyar taci uban ta, kai har ma da uwar ta.

Ɗakin Nuwairah yaje kamar yadda ya sanar da Jiddah haka itama ya faɗa mata Aikuwa ko tutuf bata ce masa ba, haka ya gama zaman shi ƙarshe fita yayi a gidan, Girgiza kai kawai Jiddah tayi tare da sauke labulen window bayi ta nufa tayi Alwala tazo ta shimfiɗa sallaya nan ta fara jero nafiffilu tana masa Addu'ar shiriya bata runtsa ba saboda damuwa da baƙin cikin dake ƙunshe a zuciyarta kuka take sosai tana tunanin Nabil nacan gurin wata mace, macen ma Karuwa, Sai bayan Asubahi ya shigo gidan lokacin ta gama ƴan aikace-aikacen data saba,

Nuwairah ce ta fito tana kallon yanda ta kammala komai “Kai Jiddah wannan aiki haka, kinsan fa baki da lafiya ai da kin bari nayi komai” “Barka da Fitowa Aunty Nuwairah, ai ba komai wallahi” Hannunta Nuwairah ta kalla tana faɗin “To ya ƙarfin jikin naki? Ina fatan kin ji sauƙi?” Jiddah tace “Alhamdulillah da sauki sosai” Zama Nuwairah tayi tana faɗin “To Masha Allah jiya Yaya yake min maganar da ban gane kansa ba, na fara tunanin gwara a kaishi asibitin mahaukata a dubashi dan ga dukkan Alamu karen hauka ya cijeshi” Girgiza mata kai Jiddah tayi tana dariyan zancen ta. “Kai! Nuwaih yana cikin hankalin shi nafi ɗaukar maganar da wasa yake..” ajiye spoon ɗin tayi tana faɗin “Wasa fa kika ce? Allah da gaske yake kuma nasan zai kai maganar gaba” Kallonta nayi domin wlh na ɗauka barazana yake “Allah ya kyauta” nace sannan ya shiga ɗaki nayi shirin fita.
Jin motsin tura Get yasa ta gyara zama tana daɗe faɗaɗa fuskanta da yalwataccen murmushin a tunanin ta Nabil ne, Amma jin wani ƙamshi na daban yasa ta shiga kokonto waye haka? Jiddah kuwa tsayawa tayi tana ƙarema Gidan kallo sosai tana kallon ɓarnan da akayi da dukiya musamman ma kyawawan kujerun Alfarman dake falon ga danƙareren tv bango “Waye Anan?” Aaliyah dake fitowa ta faɗi haka tana mamakin ganin mace, Cikin nutsuwa Jiddah ta juyo tana tuna mai muryan ja da baya Aaliyah tayi tana nunata “Meya kawo ki gida na?” harɗe hannuwa Jiddah tayi a ƙirji tana matsowa tare da ƙare mata kallo “Aaliyah!! Ohh daman kece Karuwar tasa? Kece kikayi kane kane a rayuwar mijina? Kice kika ɗauke wa mijina hankali oh Na tuna a can baya kince zaki addabi rayuwata hakane Abun dama? To yau koni ko ke dan wallahi saina Kashe ki yanzun! kuma anan!! Saina lalata duk wani halitta na jikinki..” ja da baya Aaliyah ta shigayi tana faɗin “A'a Jiddah dakata nayi miki bayani wallahi Ina Son Nabil shima kuma yana ƙaunata yanzun haka muna shirin Aure ne dan mu mallaki junanmu...” ɗauke ta tayi da lafiyayyen marin da se da ta fitar da jini ta hancin ta, cakume wuyan riganta Jiddah tayi tana jijjigata cikin ɓacin rai “Mijin nawa kike shirin Aura ko? Zaki Aure shi amma a lahira dan baki da gurbin zama cikin matanshi na duniya” tana gama faɗin haka ta shiga kifa mata mari kukuwa kawai Aaliyah ta shigayi da Numfashi saboda riƙon da Jiddah tayi mata Numfashinta na barazanan ɗaukewa Dunƙule hannun Jiddah tayi da niyar kai mata naushi cikin tashin hankali Aaliyah ta tare cikinta da hannu tana faɗin “Dan Allah karki kashe rai, Ciki gareni na sati shida Please naci albarkacin sa...” ta ƙarasa maganar cikin kuka, cikin tashin hankali Jiddah tace “What! CIKI!!! Innalillahi wainna ilaihi rajiun” Jiddah ta faɗa tana ja da baya tare da fashewa da kuka “Ciki de na Haihuwa? Kina da ciki? No! Ƙariya ne!!” dawowa tayi da gudu takai mata wani mummunan naushi a ciki, ƙara me ƙarfi Aaliyah ta saka tare da zubewa a ƙasa ɗif Numfashinta ya ɗauke na wasu daƙiƙu, ruwa me sanyi Jiddah ta zuba mata a Fuska tare da ɗagota “Karki yarda ki sake raɓan mijina ke ko Sunan mijina kikaji Ina so ki toshe kunnuwanki dan wallahi naji Mijina yana tare dake kashe ki zanyi!!” Kaman mahaukaciya haka Jiddah ta shiga dukanta ba ji ba gani, kafin ta shiga janta har ƙofan gida ta watsar da ita dawowa tayi cikin Gidan tare da Zuba fetur ta cinnawa gidan wuta tana fitowa ta tarar da Nabil yana shirin ɗaga Aaliyah dake ƙwance cikin jini Cikin wani irin mawuyacin halin Aaliyah ta Riƙe hannunshi tana faɗin “Yau nake shirin sanar da kai amma matarka ta ɓata komai Nabil Baby Na ciki gareni shine tazo ta kashe ni da Abinda ke ciki na” A zabure ya sa ke ta tare da nufo Jiddah nan ya shiga zuba mata mari cikin ɓacin rai “Akan me? Me yasa kika zubar min da ciki...”
“Nabilllll” da gudu ya nufi gurin Aaliyah tare da ɗaukanta yasata a Mota suka nufi asibiti.
Gida ta nufo gbɗy bata cikin nutsuwarta “Jiddah Ina kika je?” Ina Jiddah bata ma san da ita ake magana ba, riƙe ta Nuwairah tayi tana faɗin “Jiddah menene haka? Ya naga fuskan ki a

kunbure waya dake ki?” wani irin kuka ta fashe dashi tare da faɗin “Nuwairah Yarinyar da Nabil ya ajiye har ciki gareka wannan Karuwar tasa nake faɗa miki ciki gareta saboda naje na dake ta shine Nabil ya mayar min da fuska haka Akan karuwa Ya min haka!” Cikin tashin hankali Inna ta ƙaraso gurin har zaninta na shirin faɗuwa kasa “Me nake ji haka? Ke! Jiddah me kike faɗa ne?” Girgiza kai Jiddah ta shigayi tana faɗin “Babu komai..” Rufe mata baki Nuwairah tayi itama cikin kuka tana faɗin “Ƙwarai Abinda kunnuwanki suka jiye miki haka ne, Nabil ne ya ajiye Karuwa a waje duk wannan rigingimun da muke duk akan maganar ne..." Rufe mata baki Jiddah tayi tana girgiza mata kai alamar karta faɗa “ƙyale ni Jiddah Halin Nabil ya isheni gwara na fayyace komai” tiriyan-tiriyan ta dinga faɗa musu komai Wani wawan burki Nabil yaja yana kallon Nuwairah dake bayani Juyowa mahaifiyarshi tayi nan ta shiga zuba mishi mari tana faɗin “Wannan ba tarbiyan dana baka bane, wannan ba Renon Asma'u bace, Nabil kaine da ajiye mace a waje har da ciki?” sunkuyar da kanshi yayi ƙasa yana sake jin wani ɓacin rai, duk abinda suke Mahaifinshi na kallonsu jinjina kai yayi yana mamakin Halayyar da Nabil ya ɗauko “Da Girman ka, da ilimin ka, kana da iyali kasan Hukuncin zina kuwa? Anya Nabil baka fara shaye-shaye ba kuwa? To wallahi ka buɗe kunninka kaji da kyau bazan ɗauki wannan ƙazantar a cikin gidana ba, ban taɓa Zina ba, dan haka...” da sauri Jiddah tace “Dan Allah Abba karka masa baki, dan girman Allah kuyi masa addu'a shine kawai abunda yake buƙata” gyaɗa kai Mahaifinshi yayi tare da nuna shi da yatsa ransa a ɓace ya bar gurin haka ma mahaifiyarsa Nuwairah kuwa hannun Jiddah ta kama suka dawo part ɗinsu.

yanke shawaran barin Gidan Jiddah tayi, nan da Nan ta shiga haɗa kayanta tare da buɗe wani ƙaramin jaka ta ɗauko hoton Mahaifiyarta, rumgume hoton tayi tana hawaye sosai cikin kuka take faɗin “Umma Ina cikin Ahalinki yau nice matsayin matar ɗan da kikafi ƙauna yau gashi zan barshi bazan iya cigaba da zama dashi a irin wannan rayuwar ba, bazan iya zama baƙin ciki da damuwa su kashe ni ba, gwara na koma inda na fito gwara na tafi kuma tafiyar da bana jin zan sake dawowa”

Zoben Azurfa da awarwaronsa ta ɗora kan hoton tare da ɗan shot note ta ajiye, ATM ta ɗauka tare da Nufar part ɗin Mama-Sadin ganin tana barci ne yasa ta juyawa da niyar fita ɗan gyaran murya taji mama tayi a hankali ta juyo tana kallon yanda Mama ke motsawa da sauri ta fita a gidan kuɗi masu yawa ta cire kafin ta bar ƙasar direct Gidan Fadilah ta nufa dan bata so kowa yasan tazo Nigeria daga dangin Ummi bata samu Fadilah a gida ba, me musu gadi ne yake sanar da ita tafiyan da tayi tare da mijinta key ɗin cikin gidan ta karɓa daga gurinshi kasancewar ya santa da Fadilah shiyasa bai wani damu ba, Ɗakin Fadilah ta shiga nan ta adana kayanta tare da shiga bayi tayi wanka a gurguje tazo ta biya sallolin dake kanta kasancewan dare yayi sosai bazata iya yin girki bane yasa ta haɗa tea kawai tasha ta kwanta.

Chadi....

Bana ganin Comment

Maman Faruq
12/26/23, 9:03 AM - UMMI JB: ♡SIRRIN ƊAUKAKA..!♡*

® AYSHA JB

FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION

Alhamdulilah jiki ya yi sauƙi sosai ina matuƙar godiya da addu'o'inku🥰🤝

35 Riƙe hannuwanshi tayi da ɗan ƙarfi tana kiran sunan shi, a hankali ya buɗe idanunsa tare da faɗin. "Sannu Aaliyah ya kike jin jikin naki yanzun?" ya ƙarasa maganar tare da shafa fuskan ta. "Da sauƙi Lover ai na ɗauka ka tafi.." Girgiza mata kai yayi sannan ya taimaka ma ta ta zauna, shafa cikinta tayi tana kallon shi da murmushi. "Kana murna kuwa?" zama ya yi kusa da ita tare da kwantar da kan shi bisa kafaɗarta shima ya ɗora hannunshi saman nata tare da sa kin kyakkyawan murmushi yana lumshe ido, sun jima a haka na tsawon lokaci kafin ya janye jikinshi daga gareta tare da nufan ofishin likita tattaunawa sukayi akan yanayin jikin na ta kafin ya dawo ya samu har ta koma barci gyara tsayuwar sa ya yi yana ƙare ma ta kallo tare da ƙurawa cikin jikinta ido, sosai yake jin farinciki mara misaltuwa a ran shi kallon agogon da ke ɗakin ya yi yana tunanin zuwa gida gashi dare ya yi sosai banɗaki ya shiga ya kama ruwa tare da alwala ya dawo ya shimfiɗa sallaya ya fara nafila a saman sallayan ya kwana washe gari aka basu sallama ya dawo da ita gida bayan ya sa an gyara komai na gidan da ƙyar ta ƙyaleshi ya nufo gida.

Nuwairah ce kaɗai zaune a falon domin tun jiya suke niman Jiddah amma babu ita babu labarin ta hankalin su ya yi matuƙar tashi sosai dalilin haka yasa mahaifin Nabil ɗaukan zafi kasancewar ba irin kiran wayan da ba'ayi masa ba amma ya ƙi ɗagawa Mama-sadin ma da taji labari hankalin ta ya tashi sosai inda ta shiga faɗa tana faɗin basu kyauta mata ba me yasa basu faɗa mata tunda wuri tayiwa abun tufkar hanci ba, shiyasa kwanaki take ganin Jiddah cikin yanayin damuwa ashe da walakin goro a miya domin Jiddah yarinyace me sakewa da mutane duk da ita ba mace bace me yawan surutu da son hayaniya amma akwai ta da daɗi hira ga iya tausasa lafuza duk maganar da zai fito daga bakinta me kyau ne da kuma ma'ana. tana da haƙuri da kawaici, sau da dama tana tambayar ta yanayin zaman nasu ba ta taɓa gaya ma ta wani abu da ake mata mara daɗi ba yawancin lokuta ma idan ta tambaye ta sai dai tayi murmushi kawai daga haka zata shashantar da zancen ta wani siga yarinyar ta shiga ran ta sosai tana jin ta kamar yadda take jin sauran jikokinta sai dai ƙaunar da take mata daban ne dalilin da yasa ta ɗaga hankalinta kenan akan ɓatan nata.

"Lafiya kuwa Nuwaih naganki cikin wananan yanayin?" kallon shi tayi tana jin takaici da baƙin cikin kasancewar shi ɗan'uwan ta wanda kuma yake matsayin miji a gareta ɗakin Jiddah ta nuna mishi tare da ɗauke hawayen dake zubo mata kallon ta yayi zuciyar shi na dukan uku uku a tunanin shi wani mugum abune ya samu Jiddan hankali a tashe ya nufi ɗakin cikin hanzari nan yaga gabaɗaya ɗakin a hargitse ga dukkan alamu babu wanda ya kwana cikin ta kallon inda akwatunanta suke yay nan yaga babu wasu daga cikin akwatunan zama yay gefen gadon tare da dafe kanshi da hannuwanshi duka biyu yana jin wani irin tashin hankali tare da tunanin Ina taje? Ina ta kwana? a wani hali ta ke? duk ba shi da me bashi wannan amsar kallon gaban madubin ya yi nan yaga gabaɗaya babu kayan kwalliya da mayukan shafe shafenta miƙewa yay yana zagaye ɗakin zuciyarshi na bashi lallai tana Nigeria yanzun haka, naushin iska ya yi yana jin babu daɗi a ran shi, ta gefen gadonta yaga awarwaro da sarƙa ɗauka yay tare da bude hoton dake gurin da wasiƙar da ta rubuta. "a lokacin da zaku iske wannan saƙon nasan nayi nisa Ina so abar wata maganar dangantaka kayi gaggawan aikomin da takarda ta, domin bazan iya cigaba da zama da mutum mara adalci irin ka ba, a yanzun na haƙura da aure da duk wani abu

daya shafi ɗa namiji nafi sha'awar zama ni kaɗai domin babu komai cikin rayuwar Aure daya wuce baƙin ciki da damuwa. duka halin maza haka yake, duk yadda ka kai ga son gane halin maza bazaka taɓa fahimta ba, domin kullum cikin canzawa suke baka gane gaban su balle bayan su, Ina sake jaddada maka ka sauke min wannan ƙadararren Auren nake damin bazan iya cigaba da zama da kai ba, karka ɓata lokaci gurin niman inda nake" wani irin gumi ne yake tsattsafo masa tun daga tsakiyar kan sa zuwa wiyansa kalman Innalillahi wainna ilaihi rajiun kawai yake maimaitawa kallon hoton yake hawaye na tarige rigen saukowa akan fuskansa, Kenan Jiddah ɗiyar Ammah Asma'u ce? ita ɗin ƴar'uwa tace ta jini tasan da haka tsawon wannan lokacin shine bata bani fuskan da zan fahimci hakan ba? Ya Salam me kenan na aikata ban kyauta mata ba, juyowa yay da niyar zuwa shashin Mama-sadin nan yayi arba da Nuwairah tsaye "Ashe akwai ran da zakayi kuka? tabbas nasan wacece ita shiyasa tun farko na watsar da makaman yaƙina muke zaman lafiya nasan Jiddah ƴar'uwa tace Ƙanwa tace shiyasa nayi haƙuri muke zaman lafiya.." dakatar da ita yay ta hanyar faɗin "Kinsan  da waɗannan abubuwan shine baki faɗa min ita ɗin Jinin mu ɗaya ba? maiyasa kika rufe ni? taya kika gano hakan? ni kaina nayi mamakin yanda lokaci ɗaya kika watsar da wannan kishin naki kuke zaune lafiya taya haka ta kasance?"
 "Hanisa ita ta sanar min da komai ita ta sanar min da Jiddah ƴar'uwar mu ce, amma sai na musanta daga ƙarshe se nasa aka bincika min har can Benue ɗin a nan ne na samu labarin komai shiyasa na watsar da komai amman nace bazan faɗa ba, har sai ita da kanta ta fallasa komai. Nabil baka kyauta ba, bai kamata ka taɓa Jiddah akan wata karuwa mara daraja ba, bai kamata ka ɗagawa matarka ta Sunnah murya akan wata banza mara ƙima ba,  Jiddah tana da haƙuri ni shaida ce.
Jiddah macece me sauƙin kai da kwantar da kai dan a zauna lafiya macece da abin duniya bai rufe ma ta ido ba, duk da tana kasuwanci amma haka tayi haƙuri tabar komai duk saboda tana son zaman Aure amma sai kaƙi fahimtar haka, duk wani ƙoƙarin da muke maka da ƙoƙarin sauke duk wasu haƙƙin ka dake rataye akan mu amma duk bamu ishe ka ba, meye a jikin wancan yarinyar?" shuru yay yana sauraronta daga ƙarshe suka nufi part ɗin iyayensu nan suka suka mishi faɗa sosai tare da nuna ɓacin rai akan abinda ya aikata mata shuru sukayi suna sauraron bayanin da Nuwairah take koro musu game da Jiddah "Innalillahi kika ce Asma'u ta rasu? Lahaula walakuwwata illabillah Allah sarki ashe babu rabon mu sake ganawa da Auta ta! Allah ya gafarta muku Husnah Allah yaji ƙanku da rahama  ashe Hauwa'u jikanya tace shiyasa wani lokaci nake mata kallo kamar Asma'u ashe jininta ce  to ka buɗe kunnuwanka da kyau ka jini maza-maza ka tashi ka nimo min jikanya kai harda ɗanta dan baza'a bar shi can ba, bazai yuwu  mu danginta muna raye ita tana can wata uwa duniya ɗanta na tsakiyar kishiyoyi marasa adalci ba. Karka yarda ka  dawo batare da ka samo su ba" Mama saddika ta ƙarasa maganar tare da fashewa da matsanancin kukan rashin ƴarta, nan suka fara lallashinta tare da kwantar mata da hankali.
Miƙewa ya yi yana duba wayarshi da niyar kiran ummi nan ya tuna ya bar wayan a gidan Aaliyah dole ya fito ya nufo gidan, sai dai ganin wata mota yasa shi shiga cikin mamaki fitowa yay yana kallon motan tare da nufar ƙofan ɗakin ya kai hannu da niyar tura kofan Bedroom ɗin nan yaji maganan daya kusan sumar dashi "Shi fa duk a tunaninsa cikin nan nashi ne bai san ƙariya nake masa ba, wallahi ina baka labari susucewa yay yana faɗa min in kula mishi da Cikin saboda yana tsananin son Haihuwa be san bayan shi Ina tare da kai ba..." da ƙafa ya taka ƙofan a zabure ta ja zanin gadon tana rufe jikinta, wayarshi yaje ya ɗauka tare da tattara duk

wasu abubuwan da yasan nashi ne sannan ya nufi ƙofan fita yana faɗin “ki tattara duk wasu tarkacen ki nan da minti talatin ki bar min gida idan kuma ba haka ba se nayi miki dukan da yafi wanda Jiddah tayi miki shashasha wallahi nayi dana sanin haɗa jikina dake ƙazama! kariya!! kiyi gaggawan barin Gidan nan!”
“Nabil! dan Allah ka tsaya nayi maka bayani Nabil wallahi ina matuƙar ƙaunarka wallahi bazan sake ba, dama ɗaya kawai..” wani mugun tsawan daya daka mata ne yasa ta kasa ƙarasa sauran zancen nata fita yayi yana jin zuciyarshi na zafi, lallai ya aikata kuskure a tunaninshi cikin nashi ne ashe ba haka bane bayan shi tana tarayya da wanin sa, yana dawowa gida ya fara shirin tafiya washe gari kuwa sammako ya buga sai Nigeria ummi tayi mamakin ganinsa da kuma abinda ya kawo shi ranta ba ƙaramin ɓaci yayi ba lokacin daya ce mata ya biyo sawun Jiddah ne “To ai rabo na da Jiddah tun ranan da mukayi magana ta wayan ka bayan nan ban sake jinta ba, daman ina tunanin kiran ka ganin kwana biyu shuru ba labari” miƙewa ya yi da sauri yana faɗin “Innalillahi wainna ilaihi rajiun Allahuma ajirni fi musibati..”
“Amma bari na tuntuɓi Iyanmu in ji ko taje zaria” kiran Iyanmu tayi nan ma babu labari hankalinta ya tashi matuƙa nan ta shiga kiransu Halimatu da Hanisa suma cikin tashin hankali suke sanar ma ta lallai bata zo ba, babu ɓata lokaci suka iso gidan duk hankalinsu a tashi. Ummi tace “To wai nikan meya haɗa ku da har tabar Chadi? anya Nabil ba wani mugun abu ka aikata ba kuwa? domin nasan halin Jiddah nasan irin tarbiyan dana bata faɗa min abinda ya haɗa ku”
Sunkuyar da kai ya yi yana jin girman maganan a ranshi “Bari na kira Fadilah ko Gurinta taje” cewan Halimatu kiran Fadilah tayi  tare da sanar mata halin da ake ciki , nan ita ma take sanar mata cewan sunyi tafiya amma yanzun haka suna kan hanyar komawa gida in ta huta zata zo, daga haka ta ajiye wayan jiki a sanyaye fita yayi a gidan yana tunanin Ina zaije nimanta yanzun.
Kiran Arab Ummi tayi tana tare da sanar dashi halin da ake ciki sannan ta buƙaci ya kawo mata Aakif shuru kawai yayi yana kallon wayar domin bata jira taji abinda zai faɗa ba ta kashe wayar Kallon Nafisa ya yi kasancewar a ɗakinta yake nan ya sanar mata Halin da ake ciki “Masha Allah kaga yanzun babu wata damuwa inaga ka basu yaron kawai Ita kuma duk inda take Allah yasa tana hannu na gari” Jinjina kai kawai ya yi tare da miƙewa ya fita a ɗakin a falo ya samu Aakif ɗin Yana karatu “Aakif dare fa yayi sosai kaje ka kwanta haka mana” ɗagowa yayi tare da faɗin “To Abba” yana cikin tattara takardunshi hoton Jiddah ya faɗo kallon yaron yayi tare da ɗaukan hoton kana yace mishi “Kana son ganin Jiddah?” da wani irin mugum sauri Zaina dake fitowa daga ɗakinta ta ƙaraso gurin “Ji nayi kamar kace zaka kaishi gurin Jiddah Hahahaha! Nace maka Jiddah bazata taɓa zama da wannan yaron ba, nice tayi asiri na rabaku nice nasa aka tunzura zuciyarka har ka koreta sannan nice na hanaka Bata ɗanta duk wasu abubuwan da suke faruwa nice na aikata Hahahaha! Nice silar mutuwar Mazkhura nice nayi karan tsaye a rayuwar Jumana nice! Nice!!” miƙewa yayi ya shiga kifa mata mari ba gaggautawa da sauri Aakif ya riƙe shi yana faɗin “Abba kayi hakuri ka dena dukanta bata cikin hayyacinta mu kaita asibiti..” Nafisa dake fitowa tace “Babu wani asibiti Ishara ce Allah ya nuna mata,  ai dama duk wanda ya ɗebo da zafi bakinsa” dariya kawai Zaina take ba ƙaƙƙautawa duk tayi wani iri nan ta shiga fisge kayan jikinta tare da  watsar dasu, gashin kanta ta shiga fisgewa tana ihu da surutai da wani irin gudu tayi waje wani irin sanyi jikinsu yayi nan take tsoron Allah ya sake ɗarsuwa a zukatan su Fure'atu dake tsaye wani irin kakkarwa jikinta yake hankalin ta tashe, hakama Nafisa da Arab jikinsu yayi matuƙar sanyi fita yayi domin duba yanayin da take ciki sai dai duk yadda ya kai ga hanata fita Ina tafi ƙarfin sa Tafi take tana faɗin “Huhuhuuuu zan je gani nan

zuwa Jiddah zan zo bazaki taɓa ganin daidai ba  tunda kika ɗauke hankalin mijina Ihuhhuuuu ja muje ina tafe" a zabure tayi waje shi da mai gadi tare da me musu wanki suka mara mata baya, gudu take akan titi tana ihu da surutai wani Babban gwangwaro ne yazo a guje tare da take ta, gabaɗaya yanayin babu kyan gani baka iya ganin komai banda ƙwaƙwaluwan kanta tare da kayan cikinta wadda suke waje duk tayi daga daga, motan na wucewa suka nimi gawar suka rasa zaman dirsham yayi yana faɗin "Innalillahi wainna ilaihi rajiun" kalman da yake ta nanatawa kenan gabaɗaya ya tsorata ya firgice ya fita cikin hayyacinsa haka aka rirriƙoshi zuwa gida wani irin mugun zazzaɓi ne ya rufe shi gabaɗaya jama'ar dake anguwar jikinsu ya mutu tabbas mutuwa babban wa'azice Nan kowa ya dinga faɗan halayyar ta da irin abubuwan da take aikatawa duk yadda Nafisa taso dubashi a gida kasawa tayi domin ita kanta tana buƙatar me dubata haka duka ɗunguma asibiti har Fure'atu Jumana ce kawai aka bari a gida tare da sauran yaran wadda suka rikita gida da koke koke.
** ** **
Buɗe ido nayi ina kallon Fadilah data zuba min marin a cinyata "Kai Amma Jiddah ke ba ƙaraman ƴar iska bace daman nan kika zo kika maƙale gabaɗaya kin ɗagawa mutane hankali kinga yanda ummi dasu Hanisa suka ɗaga hankali kuwa? yanzun fa daga can nake nace bari nazo na ɗanyi gyare-gyare se na koma kawai ina shigowa me gadi yace nayi baƙuwa wallahi take zuciyata ya bani kece Haba komai yayi zafi fa maganinsa Allah komai na duniya fa sai da haƙuri domin itace jagaba kuma jagoran dake tafiyar da komai, wallahi yadda naga Nabil ya bani tausayi sosai koma menene yayi miki tunda ɗan'uwan ki ne ya kamata ki ƙara Haƙuri akan na baya wallahi baki kyauta min ba domin lokacin da Ummi ta take magana hawaye take.." da sauri na tashi zaune ina faɗin "Ummin tawa ce ke hawaye wayyo Allah sarki Sorry ummi..." "Allah ya shirye ki wallahi nayi tunanin zakice mu tafi ne yanda kika wani zaburo kika tashi zaune" yatsina fuska nayi tare da nufan Toilet da niyar wanka kiran Ummi Fadilah tayi tare da sanar mata Jiddah na gidanta jin haka yasa Nabil nufo gidan cikin gaggawa fitowa nayi ɗaure da zani yayinda nake goge gashi na da towel kasancewar na wanke shi ganin mutum kawai nayi a gabana take nasa ihu ina shirin zubewa saboda tsananin tsoron daya kamani da sauri ya taryo ta cikin jikinsa yana shafa fuskanta domin da gaske de sumewa tayi ruwa ya shafa mata a fuska tare da zubama kyakkyawan fuskanta ido yana kallon yadda take buɗe idanunta a Hankali tureshi nayi ina niman zani na wani irin Kyakkyawan Murmushi yayi tare da danneta yana faɗin "Im so sorry Jiddah nasan na aikata abubuwa da yawa Amma dan Allah kiyi Haƙuri komai ya wuce wallahi nayi nadama kaina bisa wuyana ina mai bada haƙuri kodan albarkacin Ammah da Ummi ayi haƙuri a yafe mini Please Sweetheart" ya faɗa cikin kashe murya tare da zuba mata narkakkun idanunsa shuru kawai nayi domin bana jin zan sauko lokaci ɗaya a bazata naji bakinshi cikin nawa da wani irin masifan na fara ƙoƙarin tureshi ina faɗin "Kawai kace min kazo kaji daɗi dani ne, kazo na Buɗe maka ƙafa bayan irin cin mutuncin da kamin akan wata karuwa.." haɗe bakinsu yayi tare da girgiza mata kai.
Wani irin lafiyayyen kissing ɗinta yake tare da shafo na shanunta laƙwas tayi tana jinshi domin gabaɗaya yayi nasaran kashe mata gaɓoɓin jikinta kifa kanshi yayi yana wasa ƙirjinta sosai tare da faɗa mata wasu irin kalamai masu wiyar ɗauka kuka ta saka tare da ƙanƙameshi tana faɗin "Me yasa ka kasa fahimtar irin soyayyar da nake maka Sir Nabil! mai yasa! Wallahi ina ƙaunar ka sosai, Yayana ina sonka soyayya mara iyaka amma ka kasa fahimtata duk wani kawaici da kunyata na ajiyesu gefe na fito fili na fayyace maka Sirrin zuciyata kaine muradina tun lokacin dana fara arba da kai, sai dai nayi ƙoƙarin nesanta kaina da kai ne saboda sanin matsayi da

kuma son kare mutunci da martaban Aure na..” shafa fuskanta yayi yana faɗin “Na sani nasan kina sona nasan kuma kinyi haƙuri da halin ƙuncin rayuwa kinyi haƙuri akan komai lallai ke macece da kowa zaiso ki zamo mallakinsa Ina miki nikin ba nikin ƙaunar da kike min. Ina so kiyi Haƙuri kizo mu ƙarasa rayuwarmu kina da farinciki da jinin daɗi domin Ahalinki suna can suna tsumayin zuwanki Kowa nason sake ganinki kowa na murna dajin cewa ke ɗin ɗiyar Asma'ulhusnah ce ke ɗin fa Autar Ummanta ce shalelen Ummi Ƙanwar Nuwairah da Nabil matar Nabil farinciki a gidana..” (tsakani da Allah wanga soyayyar ta tsumani..)
rufe mishi baki tayi da nata daga haka suka lula duniyar ma'aurata can ƙololuwan sararin samaniya Cike shauƙin So da Kauna suke faranta ran junansu.
Bayan komai ya lafa ne ya kalleta tare da jan karan hancinta yana faɗin “Ki shirya sai mu wuce gidan ummi tare ko?” Ajiyan zuciya ta sauke tare da gyaɗa mishi kai, tare sukayi wanka sannan ya tayata shiryawa wanda gabaɗaya cikin shiririta aka gama shirin fita yayi yana jiranta a waje, shigowa Fadilah tayi tana kallon Jiddah ta fashe da dariya “Taɓ lallai har an kammala soyewan Allah yasa de ba'a ƙone ba..” da ɗankwalin  hannunta ta jefi Fadilah tana dariya “Kinga bana son sa ido fa” Fadilah tace “Babu wanin nan munafuka ana so ana kaiwa kasuwa, sai a cigaba da haƙuri kisan lamarin rijalu sai ana haɗawa da batun haƙurin nan” rumgumeta Jiddah tayi tana faɗin “Na gode sosai Bestie sai kin shigo kenan” daga haka sukayi sallama gidan Ummi ya kawota sannan ya nufi hotel ɗin daya sauka domin yaƙi zama cikin gidan nan ummi ta shiga faɗa kaman zata ari baki domin ranta yayi matuƙar ɓaci, “Kiyi haƙuri Ummin mu tunda tana cikin ƙoshin lafiya ai Alhamdulilah koma dai menene ya wuce kema Jiddah baki kyauta ba domin kin ɗaga mana hankali sosai” cewan Hanisa “I'm so sorry nasan ban kyauta ba amma in sha Allahu hakan bazai sake faruwa ba ayi haƙuri Ummi na Please kiyi mun ɗan Murmushi mana haba uwata kin san de bani da tamkar ki a yanzun dan Allah kiyi Haƙuri kinji haba ummi Shalelen ki ce fa..” rumgumeta Ummi tayi tana jin hawaye na cika mata ido “I'm so happy too you Shalele naji daɗi ƙwarai kasancewar kina cikin danginki sai dai ina jin babu daɗi ganin kinyi nesa dani nasan ba lallai kuma su sake bari ki zo...”
“A'a ummi karki ce haka ina nan tare dake zaki dinga gani na akai akai Ummi bazan taɓa mantawa da uwa kamarki ba, Ummi kinyi min komai wadda uwa take yiwa ƴarta shiyasa a kullum nake miki addu'a da fatan dacewa anan duniya da kuma lahira a duk lokacin da kike Son ganin Shalelen ki zata zo miki batare da kawo wani uzuri ba..” cikin burgewa Halimatu da Hanisa suke kallonsu daga ƙarshe suka saka dariya har Ummi ɗin, haka suka ci gaba da hira har dare kafin mazajensu suka zo ɗaukan su. Gida ya saura daga Ummi se yaran Halimatu tare Anwar Dan nan suke karatu suna taya Ummi hira kasancewar gidan babu kowa shiyasa suka dawo dan ɗebe mata kewa.
Hira sosai mukayi da ummi inda ta dinga min nasiha tare da bani addu'o'in, sai da akayi kwana shida ana gobe bakwai tukun muka ji labarin mutuwar Zainab wanda seda na gigice domin yadda Nafisa take faɗawa Ummi lamarin ya ɗaga hankalin mu, a ranan Ummi ta nufi Abuja gida ya saura daga ni se yara sai kuma Nabil daya tare min duk ya hanani saƙat kwana goma Ummi tayi kafin ta dawo nan ta same ni kwance ina fama da zazzaɓi “Ummi sannu da zuwa ya ƙarin haƙuri kuma? Ubangiji ya gafarta mata Allah ya mata rahama”
“Allahumma Amin Jiddah sannu ya jikin naki? Nabil yake sanar dani rashin lafiyan ki meyasa bakuje asibiti ba?” lumshe ido kawai nayi ina jin yanda cikina ke juyawa “Kinga bari na kira Nabil ɗin yazo muje asibiti..” dakatar da ita nayi ta hanyar faɗin “A'a Ummi ki bari har ki huta mana” dakatar da ita Ummi tayi tare da kiran Nabil nan suka nufi asibiti gwaje gwaje da Aune aune

suka shiga mata ƙarshe de gado aka basu dan yanayin jikin nata sai a hankali sai washe gari, sakamako ya fito da wani irin murna Nabil ya rumgumeta yana faɗin “Alhamdulillah Allah na gode maka ashe ina da rabo nima Thank you for the last night Thank you Fadilah Dan nasan a gidan ki muka samu Baby...” Ai fita sukayi gabaɗaya har Ummi domin Nabil kan ya zama mara Kunya sosai sukayi farinciki ganin tana da ciki gashi yana ɗan bata wahala sai da ta kwana uku aka sallamesu bayan kwana biyu suka fara shirin tafiya saboda mutanen Chadi sun matsa sosai akan su koma badon taso ba haka ta fara shirya kayanta sauran kwana ɗaya tafiyarsu Arab ya zo tare da Aakif da wani irin murna ta rumgume ɗanta harda hawayen farinciki cikin tsananin jin daɗi shima yace “Umma na! Shine kika barni bakya zuwa gurina da Abba na!” shuru kawai tayi tana shafa kan yaron tare da kissing fuskanshi “Kayi haƙuri Aakif amma yanzun in sha Allahu komai ya wuce ina tare da kai zamu kasance tare har abada”
“To umma meyasa ba zaki zo mu zauna tare da Abba na ba?” miƙewa Nabil yayi dan basu damar ganawa da juna  sosai, da kallo ta raka shi se take ga kamar maganar Aakif ɗin ne ya ɓata mishi rai Nan ta shiga mishi faɗa tare da faɗa mishi babu wani sauran zama tsaninta da baban shi hasalima tare zasu koma Chadi yaje yaga family ɗinta sannan zai zauna gurinta “Wallahi bani zuwa ko'ina batare da Abba na ba...” buge mishi baki tayi tare da faɗin “wani irin tarbiya ce wannan? Ina ilimin da ake yabon ka dashi? Ni mahaifiyarka ina faɗa kana faɗa Abokiyar wasan ka ce ni? to ka buɗe kunnuwanka da kyau gobe tare zamu tafi” shigowa Ummi tayi tana faɗin “Ya ya meya faru nake jin tashin muryan ki?” cike da jin haushin abinda Aakif yayi mata ta sanar da Ummi kallon Aakif Ummi tayi kafin tayi wani magana ya rigata “Ni wallahi babu inda zanje batare da Abba na ba..” Ummi tace “A kul! karka sake kuskuren ɓata mata rai kasan damuwa da ƙuncin data shiga duk saboda kai? Kasan irin wahalan data sha kafin ta saba rayuwa batare da kai ba? Haba Aakif ban sanka da wannan halin ba..” “Ummi ai bata sona inda tana sona to meyasa tayi wani Aure? taje tana jin daɗi ni kuma ta barni har wani baby aka ce zata haifa ni gaskiya bazan je ko'ina ba tayi tafiyarta kawai tunda tana da wani Mijin” Kuka Jiddah tasa tana kallon yadda yake magana yana cika yana batsewa tare da tamke fuska kaman bashi yayi maganar ba “Ummi kina ji ko? wai dan Allah meyasa rayuwa take juya min baya? tsawon shekaru ban saka shi idanuna ba, duk kewarsa da nayi da irin kalaman da zai tare ni kenan wallahi nima yayi zaman shi bani zuwa dashi ko'ina bare yaje yana rena min miji..” Ummi tace “Kaci gidanku ka duka kaba mahaifiyarka haƙuri ina ruwanka da Auren ta! laifi ne dan ta rabu da mahaifinka kai baka san ƙaddara bane? Kayi gaggawan bata haƙuri kafun na saɓa maka shashashan banza, shi uban naka yasan da haka ya sake ta”
Kuka ya saka yana jin Haushin abinda Jiddah tayi domin shi duk a tunaninsa batayi wani Aure ba. “Kiyi hakuri amma gaskiya babu inda zanje bazan iya zama inda babu mahaifina bare ayi mini Kallon agola...” “Innalillahi ummi kina jin abinda yake faɗa ko? irin abunda nayi gudu kenan tun farko gashi an ɓata min yaro babu tarbiyan arziki nasan da tun farko yana tare dani da hakan bata kasance ba Dan Allah Aakif karka ƙara min damuwa kayi hakuri Nabil ɗan'uwa nane ina Son mijina shima Abban ka ne tunda Yayana ne...” “Ni ba Abba na bane kuma na faɗa bani zuwa ko'ina kawai kiyi Haƙuri in da rabo wata rana zanzo amma banda yanzun Kina son mijinki Nima Ina son Abba na” duk yanda taso ya fahimce ta yaƙi saurarontа tayi lallashi ita da Ummi amma ina ya kafe akan babu inda zaije karshe haka zuciya ya ɗibeta seda ta kikkifa mishi mari Amma ko a jikinsa ranan tayi kuka sosai a dalilin haka ta ɗaga tafiyan tana tunanin ko zai sauko ya saurareta da safe ne suka gaisa da Arab inda take mishi ta'aziya kallonta yayi tare da murmushi yana amsawa zuciyarshi a sake domin yanzun baya jin wani rigima ko tashin hankali

“Amma gaskiya Yallɓai banji daɗin tarbiyan da aka yiwa yaron nan ba,  ya za'ayi ina magana yana magana sam banji daɗi ba”
“Kiyi haƙuri insha Allahu zai zo tunda yanzun yaƙi ki ƙyaleshi zan lallaɓa shi” cikin tsananin fushi Jiddah tace “Bana son a sangarta min yaro bana son goyon sangarci a bashi tarbiyan data dace bayan haka ina maka fatan alkhairi Allah kuma ya sada mu da Alkhairinsa bana jin zamu sake haɗuwa ban sani ba ko Bikin Jumana idan me gidana ya yarda to, dan Allah ina sake jaddada maka a kula a san irin tarbiyan da za'a dinga bawa yara” daga haka sukayi sallama har ta juya tana tafiya sai kuma ta juyo tana kallonshi tare da ɗan sake fuska “Na gode Jiddah ina miki fatan samun farinciki me ɗorewa a rayuwarki Allah ya sani ina Ƙaunar ki babu yadda na iya ne” Ɗauke kanta tayi sakamakon ganin Nabil dake tsaye nesa dasu yana jiranta ba tare da tace mishi komai ba ta nufi gurin mijinta.
Kwana biyu tsakani suka tafi ita da Nabil Aakif kan ya kafe babu inda zashi.
***    ** ***
Sun isa lafiya inda kowa ya shiga nuna mata soyayya tare da kulawa na musamman lokacin da suka samu labarin Juna biyun da take ɗauke dashi sunyi murna sosai haka ma Nuwairah tayi matuƙar murna tare da Addu'a Allah ya bata in tana da rabon Haihuwa Mama-sadin ma tayi murna sosai sai dai taji babu daɗi na rashin zuwan Aakif a hoto kawai ta ganshi amma duk da haka bata cire rai da zuwan nashi ba, tattali soyayya ƴan'uwa da soyayyar miji tare da Ƴar'uwa ta Abokiyar zama su suka sake kwantar min da hankali yanzun bani da wata damuwa wadda ya wuce Allah ya sauke ni lafiya kullum muna magana da Ummina ta video call su Halimatu ma haka, Hanisa yaranta Biyar yayinda halimatu take da huɗu, wata tara da kwanaki Allah ya sauke ni lafiya inda na samu Asma'ulhusnah rayuwata a Chadi cikin dagina abun farinciki ne, muna zaman mu lafiya babu me jin kanmu ban samu zuwa bikin Jumana ba amma na yiwa Nafisa aike daga ɓangaren dangin Mahaifina ma muna waya sosai kuma ina tura musu da duk abubuwan bukata ban manta da mutanen da suka tallafi rayuwata ba kamar matar me anguwa da mijinta ina musu alkhairi daidai gwargwado a baki Nuwairah nake jin labarin Aaliyah ta haihu ɗa Namiji  sai dai tana cikin wani yanayi daga ita har iyayen nata sakamakon karayan arzikin da suka samu to daman dukiyan nawa ne, a wani zuwan da nayi Nigeria ne na aika mata da kuɗi tare da sutura da kayan Abinci domin ni ba mace bace me riƙo kuma ban nufi kowa da sharri ba , domin kullum ina cikin kariyar ubangiji ina addu'a sadaka domin ita maganin duk wata fitina ce, Husnah nada shekara biyu na haifi Abdallah takwaran Abba. Nuwairah kan Allah bai bata ba, domin wani hanin ga Allah baiwa ne..
END
Ƙarshe.
ALHAMDULILAH!
Anan na kawo ƙarshen wannan labarin ina roƙon Allah daya yafe mana kurakuren mu.  Allah kuma ya bada ikon amfani da darasin dake cikin littafin, dani daku Allah ya bamu ladan dake cikinsa Na gode ƙwarai, Na gode sosai da jimurin jira, ina ƙaunarku dan Allah🥰❤️ kamar yadda kuke sona nima ina Sonku irin sosai ɗin nan idan nace sosai ina nufin Sosai!!! Jama'ar Wattpad Ina gaishe da kowa Son so domin ALLAH😍🤝 sai mun haɗu a sabo..

Taku ce har kullum ƴar mutan BENUE A'isha JB

*Maman Faruq*